©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

01

2002

Kamar ko da yaushe a ranakun da Nanna ce takan zo daukar su daga makaranta, yau ma yana leko kai yaga motar ta ya koma cikin makaranta. Mintina kusan sha biyar ya bayar a tsakani kafin ya fito, yasan babu wanda zaice ya neme shi sai Khalid, shima Nanna zatayi nasara akan shi bayan wasu yan mintina dole ya hakura su tafi. Titi ya nufa ya tari mashin da zai kaishi Hotoro daga nan makarantar su ta Greenfield da take cikin Sharada. Bai wahalar samu ba kuwa, shi yaune ranar shi ta karshe ma na zuwa makarantar tunda ya kammala jarabawar aji uku ne, duk da yaji suna cewa zasuyi musu wata jarabawar bayan sati daya da zasuyi amfani da ita wajen canza musu aji ba sai a jira fitowar JSCE din ba.

Kusan hakan shine tsari na makarantun kudi, bai wani damu ba tunda ba'a nan zai cigaba ba. Sun riga da sun gama magana da Daddy akan Science and technical zai tafi ya cigaba acan kuma har ya amince. Bakin titi ya sauka ya sallami mai mashin din ya taka zuwa kwanar da zata hada shi da gidan nasu. Ko kadan baya son komawa, ba zaiki yayita zagaye layi har bayan Magriba ba, idan dai-dai lokacin shigowar Daddy yayi sai ya dawo su shiga tare. Amman bashi da wani zabi, ba abokai yake da su ba balle yace zai wuce wajen su.

Kwankwasa gidan yayi, dattijon maigadin su ya bude mishi

"Nawfal, an dawo kenan"

Baba Isa kamar yanda suke kiran maigadin ya furta da fara'a a fuskar shi da tasa Nawfal yin dan gajeran murmushi yana amsawa da

"Na dawo Baba Isa, sannu da kokari"

Sannan ya wuce cikin gidan, bangaren su da yake wajen gidan, wanda dakuna ukune na bacci a ciki, kowanne da bandakin shi, falo sai kitchen matsakaici ya nufa. Mukulli ya zaro a aljihun wandon uniform din shi ya saka a jikin kofar yana budewa. Daddy yace bangaren nasu ne su hudu lokacin da suka dawo wannan gidan watanni hudu da suka wuce, a gaban shi a gaban

kowa yayi maganar, amman shi kadai yake kwana a bangaren, ko da Daddy ya sani bai taba magana ba. Shima kuma ba damuwa yayi ba, ya rigada ya saba rayuwar kadaici ba tun yanzun ba.

Sanin ba kowa bai hana shi shiga cikin gidan da sallama ba. A falo ya ajiye jakar da take rataye a kafadar shi yana takawa zuwa dakin daya zaba a matsayin na shi ya wuce bandaki, ranar da akeyi ba ta wasa bace ba, shisa ya watso ruwa harda alwalar sallar la'asar ya dauro sannan ya fito. Riga da wando ya saka, yana son kamshin a rayuwar shi, tun zai iya tunawa ko turare ya gani dakin Daddy zai tambaye shi ya dauka. Shisa Daddy baya rabo da siyo mishi turaruka, kala-kala, wasu ko bude su baiyi ba ma, yanzun kala biyu ya fesa a jikin shi sannan ya baro dakin baccin yana fitowa falo inda yaci karo da Khalid da yake rike da kofi a hannun shi sai filet a dayan hannun da Nawfal yaga kamar cincin ne a ciki.

"Jalof Nanna tayi..."

Cewar Khalid din yana mikawa Nawfal kofin daya karba yana dubawa, shayine da akewa laqabi da ice-tea a turance, dan kankaru ne a ciki. Khalid ne kadai yasan baya hada hanya da duk wani abu me zafi, ko abinci ne saiya ajiye shi ya huce sannan yake ci. Zai iya cin abincin da ka fito da shi daga fridge amman ba zai iya cin wanda ka zubo daga tukunya ba sam. Amman kowa a gidan yasan baya cin yaji, idan yace baya cin yaji sai mutane su dauka abincin da yayi yaji da yawa ne baya so. A nashi yanayin ba haka bane ba, ko attaruhu daya kasa ka gabaki daya miyar ka zai mishi illa, cokali daya zaiji kamar ya zuba garwashin wuta a cikin bakin shi, awa daya ba za'ayi a tsakani ba kuraje zasu cika mishi baki, zai iya sati yana fama a haka.

Tun yana karami kowa yasan hakan, allergy ne yake da shi na duk wani abu daya danganci yaji. Duk da ya zamana dama ce da Nanna ta kara samu wajen gallaza mishi, da yake duka gidan kowa yana son abinci masu yaji har Daddy, a gaban Daddyn sai ta nuna abincin Nawfal daban take dafa mishi. Bai kuma taba karyatata ba, idan farin abinci ta dafa da miya zai diba ya saka mai da Maggi yaci, ranakun da yake da makaranta ma inya dawo baya bi takan abinci, da yaci sau daya shikenan zaici gaba da hidimar shi, kusan jikin shi ya riga da ya saba da yunwar.

"Ban san ko sugar din yayi maka ba, ka sha kaji"

Khalid ya sake fadi yana mika mishi farantin cincin din

"Nanna ta san ka dibo mata cincin?"

Nawfal ya tambaya, dan daga kafadu Khalid yayi

"Abinda Nanna bata sani ba yana da yawa..."

Dan murmushi kawai Nawfal yayi, Khalid ya saba saka kanshi cikin hatsari saboda shi. Jibga ta Nanna babu wanda ya kai Khalid din shanta, kuma fiye da rabin lokuttan akan shine. Kurbar

shayin yayi, sanyin shi yana saukar mishi da wani yanayi mai dadi, yana son kayan sanyi. Suna saka shi nutsuwar da ba zai iya misaltawa ba. Kai ya jinjina ma Khalid

"Komai yayi dai-dai... Nagode"

Sannan ya karbi filet din cincin din ya karasa yana samun kujera ya zauna ya ajiye shi akan hannun kujerar. Khalid dinma waje ya samu ya zauna

"Zanje gidan Daada idan nayi sallar la'asar. Kila in kwana acan. Ka fadawa Daddy idan ya dawo"

Kai Khalid yake girgiza mishi

"Kabari idan ya dawo yau sai mu fada mishi gobe kai baka da makaranta, ni ina da. Idan na dawo sai a kaimu nima ina so inje, na dade banje ba..."

Kallon shi Nawfal yakeyi harya gama maganar

"Ko Daddy ya barka Nanna ba zata bari ba, ka sani. Zan tafi yau, idan ka tambayi Daddy saika biyoni daga baya"

Baki Khalid ya bude zaiyi magana Nawfal din yayi saurin katse shi

"Zan tafi yau, ba zan kwana a gidan nan ba"

Shiru Khalid din yayi, duk wani abu da zai fada yasan ta bayan kunnen Nawfal din zai wuce. Shisa ya zauna har ya gama shanye shayin, cincin din kwara budu yaci yana kallon shi. Yar karamar jakar shi Nawfal ya dauka. Tare suka fita masallaci sallar la'asar.

***

Da sallama ya shiga gidan Daada, kallo daya zaka yiwa fuskar shi idan kagan shi awanni kalilan da suka wuce zaka ga sauyin da tayi. Idan zaka tona zuciyar shi mutane uku zaka samu a cikinta, Daada na daya daga cikin mutanen

"Nawfal..."

Daada ta fadi itama da alamun jin dadi a muryarta bayan ta amsa sallamar tashi, anan bakin kofa ya zare takalman shi yana shiga cikin dakin, zaune take a kasa kan kafet, akwai kujeru a cikin dakin, zama a kan su bai dameta ba, sai tayi kwanaki bata hau kai ba, tafi jin dadin saman kafet din, idan ma wani ne yazo yayi mata magana takan ce

"Ina zan iya zaman kujera, kafafuwana duk su tara jini, ga jikin tsufa"

In Julde ne dariya yakan yi

"Daada idan kikace jikin tsufan nan sai wani ya dauka kin bawa shekaru tamanin baya"

Ita ma takan dara

"Ko dai banba tamanin baya ba ni din ba ta yau bace ba"

Yau din bata ma zauna falon ba sai yanzun nan, da yake tana zuwa Islamiyya anan cikin unguwar tasu ta Gadon kaya. Da karfe goma na safe zuwa sha biyu. Da ta dawo tana da miya, farar shinkafa ta dafa ta shige daki, bayan azahar bacci ta sha har uku da rabi.

"Ai kuwa gara da kazo, sai ka dauko mun Madina daga makaranta, yanzun nake shirin tashi naga hudu da rabin ta kusa"

Kallon Daada yayi

"Daga shigowata Daada? Kika san kalar gajiyar da na kwaso?"

Cewar Nawfal

"Raggwanci dai ba gajiya ba. Jakar nan zaka ajiye kaje ka dauko ta..."

Jakar ya sauke daga kafadar shi yana ajiye saman kujera, akan Madina ne kawai Daada ba zata saurari komai ba, yasan ba zata bar shi ya zauna idan ba zuwa yayi ya daukota ba. Makarantar da take din ba wani nisane da gidan Daada ba, da ka fita titi tsallakawa zakayi, hade take da islamiyya shisa ma take kaiwa har hudu da rabi, kamar yaji Daada na cewa ta kusan komawa tashi karfe shidda. Bai maida hankali kan zancen ba. Ka'ida irin ta makarantar su Madina sai da aka tsaya ana mishi yan tambayoyi, da Madina bata hango shi tace

"Hamma..."

Ba yasan zasu bata mishi lokaci, da gudunta kuwa ta karaso tana fadawa jikin shi hadi da zagaya hannuwanta a bayan kafafuwan shi. Dakyar ya bambarota yana rike hannunta suka fito daga cikin makarantar

"Yaushe kazo? A gidan mu zaka kwana?"

A shekarun ta har mamakin yanda take magana babu gargada yakeyi. Dan tsamin baki da yara sa'anninta sukeyi babu shi a Bakin Madina, babu kalmar da bata iya furtawa, sai dai wasu kalaman idan tayi saboda fulatanci da Daada takeyi mata kuma kusan dashi bakin nata ya bude zakaji fitar haruffan nata daban. Gashi tana cikin yaran da suke da surutu, sai dai fiye da rabin

nata surutun akan tambaya ne, kome ta gani tana so ta gane. Idan gidan yazo bakin shi ba zai huta da tambaya ba sai tayi bacci.

"Hamma meye wannan? Hamma me yasa kasa wannan kayan yau?"

Tambayoyi kala-kala, yanda tambaya bata karewa a bakin Madina har mamaki yake bashi

"Idan zan kwana me zaki bani?"

Dan jim tayi sannan ta amsa shi

"Tuwo..."

Dariyar da ya kwana biyu baiyi ba ta kwace mishi

"Duk abubuwa masu dadi ki rasa me zaki bani sai tuwo"

Ya karasa maganar yana daukarta ya sabe a kafadar shi saboda titin da suka karasa

"Tuwo da dadi, Daada tana yi mana"

Tace da dukkan gaskiyar ta, ranta yana son tuwo fiye da komai a abinci, sai kuma nama, dan ko abinci zaka zuba ma Madina hannunta akan naman ciki zai fara sauka, sai ta cinye sannan ta fara cin abincin

"Saboda kina zaune da yar tsohuwa shisa tuwo yafi dadi"

Da rashin fahimta take kallon shi yanzun

"Ni da Daada nake zaune ba yar tsohuwa ba"

Dariya ya sakeyi

"Wacece yar tsohuwa Hamma?"

Numfashi ya sauke, dan har sukaje gida duk amsar da zai bata sai ta nemi tambaya a ciki. Yakan ji zuciyar shi da take tare da wani dutse danne da ita ko yaushe ya daga duk idan yazo gidan Daada. Wasu ranakun yana zuwa ko ba zai kwana ba, kamar yana da wani batiri na hakuri da komai da Daada ce kadai take da hanyar caza mishi batirin, shisa yake jin zuwa gidan nata ya zame mishi dole, tana saka komai yayi saukin dauka. Akwai mutum daya bayan Daddy da Khalid da suke kaunar shi, da suka damu da shi, hakan ba abu bane karami a wajen shi.

"Hamma kunnen ka manya"

Sosai yake dariya

"Madina dan Allah ki kyale kunnuwana su huta haka, ke kullum sai kince kunnuwana manya? Kamar naki ne"

Kai take girgizawa tana kama kunnen nashi ta lankwasa, hannunta ya ture

"Sakko wallahi tunda munzo gida"

Sosai ta makale a jikin shi, sallama yayi yana shiga cikin gidan

"Ai kuwa sai kin sakko tunda kunnena babba ne"

Daada da take jinsu tayi murmushi

"Yarinya dai gaskiya ta fada, bata taba ganin kunnuwa irin naka bane shisa"

Fara'ar da bata bar fuskar shi bace ta sake fadada

"Daada kunnen Hamma ya kara girma"

Samu yayi yana saukota

"Kema kunnen ki babba"

Kan yar karamar hijabin da take jikinta ta saka hannunta tana taba nata kunnuwan

"Daada wai kunne na babba?"

Tayi maganar tana shiga cikin dakin ta zauna akan cinyar Daada da ta kamata ta gyara mata zama tana cire mata jakar makarantar ta ajiye a gefe, sannan ta kamo kafarta daya tana fara kwance igiyar takalmin don ta cire mata

"Ko dai zaiyi girma ba zai kai na Hamman ki ba, na shi kunnuwan daban suka zo"

Nawfal da ya samu kujera ya zauna yace

"Daada..."

Dariya tayi tana karasa cirewa Madina takalman

"In dauko riga ki sake mun?"

Kai Daada ta daga, da sauri kuwa ta mike daga jikinta tana rugawa da gudu

"Karki janyo mun kayan nan Madina, ki dauko wadda hannun ki ya fara kaiwa"

Ai da wahala ma idan Madina ta saurare ta, kai kawai ta girgiza. Doguwar rigace ta dauko kalar bula mai haske Daada ta saka mata. Kallon ta Nawfal yakeyi, rigarta na tuna mishi yanda yake son kalar bula, musamman mai haske kamar sararin samaniya, yana kuma son farin abu. In har Daddy zai sai musu kaya ya tambaya wacce kala zaice

"Sky blue ko fari"

Duk da wani lokacin Daddy zai siyo mishi wata kalar daban. A cewar shi

"Fiye da rabin kayan ka fari ne da blue Nawfal, gara ka sirka da wata kalar"

Yasan wata kalar a cikin kayan shi na dan wani lokacine, zai saka wata kalar saboda Daddy a yanzun, a gaba babu abinda wata kalar zatayi a cikin jerin kayan sawar da zai mallaka. Wajen shi Madina ta karaso

"Hamma zan sha ruwa"

Ta fadi

"Da ban zo ba waye yake baki ruwan? Da nazo ba zaki barni in huta ba..."

Shagwabe mishi fuska tayi yana kallon kanta da yake dauke da kitso kwara biyu, wajen keyar gabaki daya babu gashi. Kamar an sude mangwaro

"Kunne na manya, amman jibi gashin ki kamar anci giginya ba wuka"

Turo baki tayi

"Daada tace gashi na zai fito kamar nata.. Ko Daada? Nima dogo har bayana"

Madina ta karasa maganar tana juyawa ta kalli Daada, kai Daada ta jinjina

"In shaa Allahu gashin nan zai fito har gadon baya, so nake ma yafi nawa idan ya tashi"

Hankalinta ta mayar kan Nawfal tana mishi kallon kaji ko? Daman na fada maka, kafin ta sake cewa

"Zan sha ruwa, kaji... Daada ta hanani bude fridge dinta, ka zo ka bani"

Mikewa Nawfal yayi ta kuwa kama hannun shi, dole tare suka nufi kitchen din da yake hade da katon falon Daada din. Bin su tayi da kallo, wani abu na matsewa a cikin kirjinta. Tunda Nawfal ya shigo ta kula idanuwan shi sun fada yayi zuru-zuru kamar wanda baya ci yana koshi. Ta fi kowa sanin halin Saratu ba tun yanzun ba.

"Yaran nan amanata ne Julde, ina tsoron halin matar ka, ba tafiya da shi nake son hanaka ba, ka isa ka rike dan Bukar, da bana raye dole a cikin ku wani ne zai rike shi, amman ina nan, zan so ya zauna a hannuna"

Kalamanta akan Nawfal shekarun baya suka dawo mata, ko yanzun in da zai dawo gidanta gabaki daya zata so hakan. Julde ya daure ta ne da kalaman shi, kalaman da har yanzun suke saka harshen ta yin nauyi wajen ce mishi Nawfal din ya dawo wajen ta, gashi bata da wata bayananniyar hujja tunda duk yanda zata tambayi Nawfal ya zaman su da Saratu yake zaice

"Daada lafiya kalau fa, ki daina damuwa dan Allah, muna zaune lafiya"

Amman tasan karya yakeyi, alamun shi basu nuna haka ba, shatin duka a farko-farkon dawowar ta garin Kano da Nawfal din yakan ce mata dukan na makaranta ne, laifi sukayi amman tasan karya ne. Ta taba tambayar Khalid

"Makarantar ku haka suke dukan yaran mutane Khalid? Na ga jikin Nawfal ko ina shatin bulala ne"

Yanayin fuskar Khalid din tun kafin ya furta

"Duka kuma Daada? Ana duka a makarantar mu, amman ba da yawa ba, kuma Daddy na zuwa yayi magana idan mun fada, ba sosai ake dukan yan gidan mu ba"

Ta san Nawfal karya yayi mata, a yan shekarun shi a lokacin yasan ya adana damuwa a kirjin shi harya boye mata itama. A gidan ya kwana a ranar, da zazzabi ruf a jikin shi, zazzabin da sai da ta bashi magani, kuma tasan dukan ne. A lokutta da dama Nawfal ke karya mata alkawarin da ta daukarwa kanta na daina kuka akan su shida Madina, daga randa tasa kafa ta tsallake komai tayi nufin barin komai din a matsayin shudadden tarihi, sai dai ko tarihi yakan dawo maka lokaci zuwa lokaci, saboda akwai mutanen da labarin shi ba zai taba barin bakin su ba balle su barka ka manta.

Ita a nata bangaren ma bata bukatar wadannan mutanen, ko ya Madina zata gitta ita din babbar tunasarwa ce, ga Nawfal shima

"Wani abu a zuciyata yana fada mun shi kadai ne kwan da nake da rabo a duniya Daada, ga amanar dana, gatan da na hasaso ma rayuwar shi mai yawa ne, ga amanar shi nan kafin in samu dawowa, dalilin da zaisa ni barin shi mai karfine..."

Nawfal amanarta ne, amanar da Bukar ya damka a hannunta, amanar da Julde ya karbe mata take ganin ya kasa tayata rikewa

"Sai dai in har yanzun kina duba bayana, kina duba abubuwan da na bari, idan kin kasa mantawa ki daina kallona da halayen dana bari Daada waye zai daina? Ke kadai ce dalilina na shigowa garin nan, sai kuma Nawfal yanzun, idan kika hanani rikon yaron nan zanji kamar saboda kina dubana da abinda nake sa Allah ya shafe mun shi a littafina... Halayena ba zasu taba kulawar shi ba Daada, na rantse miki tarbiyar shi ba zata samu tangarda ba, kina kallon kaunar da take tsakanin mu, ko ita ki duba"

Wannan kaunar kuwa ta ganta tun a ranar farko da Nawfal ya fara dora idanuwan shi akan Julde yana da shekaru uku a duniya, sati biyu bayan tafiyar Bukar, sati biyun da daga ita har Nawfal din sukayi su a matukar jigace saboda kukan Daddyn shi da yake yi mata. Amman yana ganin Julde ya ruga ya makale shi yana kiran

"Daddy..."

Ta ga Julde da yaran shi, ta ga kalar kaunar da yake yi musu, amman yaro daya taga ya kalla da kallon da yake yiwa Nawfal, yaron da yayi sanadin komai. Har yanzun idan Nawfal da Julde na waje daya zaka ga yana kallon Nawfal din kamar shine tilon abu a duniya da yake cike mishi gurbin duk wani abu daya taba rasawa, kamar Nawfal ne hasken da ya yaye duk wani duhu daya taba samun rayuwar shi. Kome zata gani, ko me zatayi tunani bata da zuciyar da zata yiwa Julde maganar Nawfal ya dawo wajen ta, ko da ya yarda bata da tabbas akan Nawfal din zai amince, yanda Julde yake kallon shi, haka take ganin Nawfal din na kallon shi shima, kamar duka duniyar shi ta tsaya ne duk inda Julden yake.

Dawowar da su Nawfal sukayi falon da surutun Madina na katse mata tunanin da takeyi, bata san ya akayi daga rike hannun Nawfal Madina ta koma kan wuyan shi ba. Dariya takeyi cike da wani irin farin ciki da zuwan Nawfal kadai yakan bayyana shi a fuskarta.

"Da shiriritar nan da kukeyi da zuwa kayi kayo mun cefane ka siyo mun kifi"

Kafin ya amsa Madina ta riga shi da

"Zan bika Hamma, dan Allah zan bika"

Saukota yayi a hankali

"Je ki dauko hijabin ki da takalmi..."

Da gudunta ta tafi, Daada ya kalla

"Ina kudin?"

Itama mikewa tayi tana bin bayan Madina zuwa dakin baccin su. Ita ta dauko mata takalmi da yake mai madauri ne sai da ta saka mata, ta bata hijabin a hannun ta, bata jirata ba ta fita da gudu, haka Julde yake kwaso mata su, duk yawancin takalmanta irin sune. Kudi ta dauko ta fito ta same su a tsaye suna jiranta, bashi tayi ta kuma fada mishi na yanda take so. Yana rike da hannun Madina suka fita, Daada na tsaye tana kallon su. Zuciyarta da adanannen tunanin da takeyi akan su, jikokinta biyu da suka fi har 'yayanta matsayi a zuciyar ta.

Amanar ta
Kaddarar ta
Sai dai taya zata san abinda kaddara ta tanadar musu yasha bamban da tunanin ta?
A lokacin da ta hade Madina da Nawfal a waje daya
A lokacin da ta hango su karkashin inuwa daya suna tayata rike amanar junan su
Kaddara ta rubuta musu yin hannun riga da juna
Inuwar guda daya ce kamar yanda Daada ta hango
Amman hannun rigar da zasuyi da juna dole mutum daya inuwar zata bi
Dole dayan su zaiyi gararamba a ranar da babu tabbacin samun inuwar fakewa.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

02

Kamshin turaren shi ya fara cika mata hanci ta zo juya kwanciya, dan tana daya daga cikin mutanen da in har zasuyi juyi komin baccin da suke sai sun farka. Wani lokacin ma sai ta tashi zaune, kamar yanzun dinma haka ta faru da Saratu. Idanuwanta ta sauke akan Julde cikin shaddar shi ruwan toka da tayi matukar amsar farar fatar shi, agogon da yake manne jikin bango ta kalla tana ganin karfe sha daya harda wani abu na dare

"Ina zaka cikin daren nan?"

Ta bukata tana jin wani abu da ya tokare mata makoshi. Sai da tayi tunanin ba zai amsa ba, dan har hula sai da ya saka sama kan shi batare da ya juyo ba yace

"Yaushe inda zanje ko karfe nawa ya fara damun ki?"

Gyara zamanta tayi, dan batayi magana akai ba baya nufin abin baya damunta. Halayen shi kaf ta san su, zata rubuta littafi akan halayen nashi da ko shi ya karanta sai ya sha mamaki. Yau dinma bata san me yasa take son mishi magana kan fitar da zaiyi ba, tafi alakanta hakan da gajiyar da take jin tayi da halayen shi a satukan

"Karfe sha daya na dare, idan ba maza masu aikin kwana ba, kowanne namiji mai mutunci yana tare da matar shi..."

Numfashi ya sauke yana dan tabe bakin shi, surutun ta ko a jikin shi, ita dinma bawai ta dame shi bane ba balle kuma abinda ya fito daga bakinta

"Me kake tunanin Daada zatayi idan taji babu wani abu daya canza daga halayen ka? Sai ma abinda yayi gaba?"

Wannan karin juyawa yayi ya kalleta da murmushi dauke akan labban shi

"Babu abinda zatayi tunani saboda ba zaki fada mata ba, saboda zaman ki a cikin gidana yafi miki komai muhimmanci, kuma fadama Daada abune da zaiyi barazana da zaman"

Abinda yake tsaye a makoshinta take kokarin hadiyewa amman yaki wucewa, tana kallon shi ya dauki mukullin motar ya fice daga dakin hadi da ja mata kofar. Runtsa idanuwan ta takeyi tana bude su da sauri-sauri cikin son mayar da hawayen da suka cika su taf. Ta gama kuka akan Julde, ta gama zubar da hawayenta akan kishin shi, ba zai zamo karshenta ba. Bata san ko tun farko bata nuna mishi wadatacciyar soyayya bane shisa yanzun yake ganin duk wani abu da zatayi domin kudin shine, dan arzikin da yake da shi.

Ko kanta ba zata yaudara ba, tana son rayuwar hutu, tana jin dadin kudin da yake da shi, sauyin da rayuwarta ta samu a tare da shine babban cigaban da zata mutu tana alfahari da shi. Shisa bata son taga kwandala ta fita daga aljihun shi da sunan yiwa wani alkhairi bayan ita da yaran su. Har wani duhu take ji ya lullube mata idanuwa saboda bakin ciki. Amman hakan baya nufin bata son shi, tana son shi, tana jin soyayyar shi a ranaku mabanbanta, yau na daya daga cikin wadannan ranakun. Ko da ba zasu kasance da juna cikin raya daren ba taso duk juyin da zatayi taji shi a kusa da ita.

Kamshin shine gauraye da dakin, kamshin da zai cika dakin wata ko dakin otel a tare da wata da ba ita ba. Dumin shi da take son ji fiye da komai a daren shine wata zata kwana tana mora. Ta ya zata ce abin baya mata ciwo? Ance lokaci na sa ka saba da abubuwa da yawa, amman kullum Julde saiya karyata mata hakan, saiya nuna mata ba zata taba sabawa da halin bin matan shi ba. Duk yanda take kishin shi, duk yanda bata son wani ya rabar mata shi bai hanata tsugunnawa kan gwiwoyin ta ta roke shi daya kara aure ba

"Idan uku zaka kara dan Allah ka karo, da wannan biye-biyen da kakeyi ka karo uku ka ajiye mu

zama mu hudu, zamu isheka, mun isheka Julde, dan Allah..."

Murmushin da baka raba fuskar shi da shi yayi mata, ko ranshi a bace yake kuwa zaiyi murmushi

"Ajiye mata hudu ba zai hanani hangen wasu ba Saratu, ke dinma ya na kare dake? Aure, yarana kawai da nake kallo suke hanani dana sanin zaman aure dake, ko dan irin wannan surutan da kike yawan yi mun. Zan sake maimaita miki in ba zaki iya zama dani ba furtawa kawai zakiyi...kiyi harkarki inyi tawa, zaki iya nemar mun shiriya idan kina da wannan lokacin, in baki dashi kibar ni da halina..."

Ba dan tana da wani ilimin addini ba, sallah da tsarki ma yanda zatayi su a tsarin addini a gidan Radio ta koya. Anan taji kalar kuskuren da take tafkawa a rayuwarta, amman zata iya cewa jahilci na daya daga cikin babbar cutar da take damun Julde. Watakila da yayi makaranta, ta boko ko ta addini zai rage wasu abubuwan. Yanzun ma lokaci bai kure mishi ba idan har yayi niyya, tunda ita ma takan saurari kasa-kasai da ta siyo na wa'azi kala-kala kuma tana karuwa. Shisa halayen shi suka hadu suna mata ciwo biyu yanzun, kishin shi da kuma matsayin abinda yakeyi ga makomar goben yaran su.

Komawa tayi ta kwanta, bata koyi kokarin share kwallar da take zubo mata ba. Sosai kirjinta yake zafi, musamman da zuciyarta ta shiga hasaso mata hotunan inda Julde yake da abinda yakeyi. Idanuwanta taji sun bushe rayau, ko alamun bacci babu. Tana jin hawayenta tun suna zuba har suka daina, banda ajiyar zuciya babu abinda takeyi, ko juya kwanciya batayi ba, ta dai ja jikinta sosai ta dunkule waje daya ko zata samu saukin zafin da kirjinta yakeyi. Ba duba agogo takeyi ba balle ta san ko karfe nawa, kawai dai taga daren yayi mata wani irin tsayi ne. Kiran sallar asuba kawai take saurare taji an turo kofar.

Tana jin kai kawon shi, tasan kayan jikin shi yake ragewa. Bata dai motsa ba, kwan dakin daya kunna kafin ya fita yaje ya kashe ya dawo yana hawa gadon. Jin da tayi ya rikota yana juyawa da ita ta fuskance shi ya sa ta fara kiciniyar kwacewa, sai dai karfin su sam ba iri daya bace ba, ko sirantaka irin ta yawancin fulani Julde ba shida ita, ba zaka kira shi namiji mai jiki ba, amman dogone na misali, ko ina a jikin shi bai nuna rama ba.

"Kina son gwada karfi dani Saratu, in kin ganni a irin yanayin nan ki daina mun gardama kar inji miki ciwo wata rana"

Wasu hawayen ne masu zafi taji sun cika mata ido, da daudar zinar daya kwaso yake neman hada jiki da ita, ko wankan tsarki baiyi ba, lokacin da taji yanda zata tsarkake jikinta tayi kokarin ganin shima ya sani, kwanaki ta jera kullum sai ta karanta mishi yanda zai tsarkake najasar da yake yawo da ita, bai nuna mata alamar ya dauka ba, amman yaji ta, kuma tana fatan ya dauka din.

"Dan Allah ka kyaleni..."

Ta furta a raunane, ta san halin shi, abinda yayi niyya ba zai fasa ba, kuka takeyi sosai, kukan ta bai karu ba sai da bayan ya gama abinda yayi niyya ya juya mata baya cikin wani irin yanayi da ya fito da tsantsar kunar rai ya furta

"Babu kamar Mero, har yanzun banji irin Mero ba"

Kamar ita tayi sanadi ko ta zama dalilin da ya rasa Mero kuma ya kasa samun madadinta ba har yanzun. Kukanta kara mishi kunar rai yakeyi. Mata uku ita cikon ta hudu a dare daya amman ko kusa da natsuwar da yake samu da Mero basu kusanta ba balle su cike mishi ramin da ta bari. Akan yaran shi yasan menene soyayya, akan Nawfal yasan asalin kauna da dukkan zuciyar shi. Mace, ita din a wajen shi kamar riga ce da zai saka wadda yake so don biyan bukatar shi ya cire ya sauya a lokacin da yayi niyya. Me yasa Mero ta kasa barin ran shi? Zuciyar shi babu wajen kaunar wata mace banda Daada, amman yana jin wani rami a cikin kirjin shi inda baisan Mero ta zauna ba sai da tabar shi.

"Baka taba sona ba Julde, da akwai soyayyata a ranka ko yaya ne ba zaka zubar mun da mutunci har haka ba, ba zaka mayar dani abin nunawa a dangi ba..."

Maganar Mero ta dawo mishi tana saka shi runtsa idanuwan shi yana hango fuskarta, idanuwanta, jan bakin da baka raba labbanta da shi. Ita da kanta ta fada mishi baya son ta, me yasa zata manne mishi har haka? Mata nawa ya sani kafin ita? Mata nawa ya sani bayan ita, me yasa ta fita daban? Me take da shi da ya kasa samu tare da sauran? Kullum, tun bayan ita kullum saiya nemi gamsuwar da yake samu da ita a tare da mata daban-daban amman ya kasa samu. Baya bibiyar mata da yawa haka kafin Mero, ta sake bude mishi sabon shafin da babu kalaman da zasu iya fasaltawa.

Bai bude idanuwan shi ba har bacci ya dauke shi cike da mafarkin Mero, ya kuma bude su da wayewar gari cike da tunaninta. Da yake Juma'a ce shi yake kai yaran makaranta in ba wani babban uzuri ba, a gaggauce yayi wanka ya shirya sannan yayi sallar asubar da ba kullum ya damu daya sameta a cikin jam'i ba. Duk tare suka karya yana hira da yaran kamar bashi da wata matsala in har yana ganin su a kusa da shi. Salim ne dan shi na farko, Fadila da itace ta biyu kuma tana makarantar kwana ta Science and Technical da take nan garin Kano, Khalid sai Lukman.

Suna gamawa ya saka su a gaba suna fita tare, daya sauke sune ma Khalid yace mishi

"Daddy idan na dawo zanje gidan Daada acan zamuyi Weekend tare da Bajjo..."

Khalid din ya karasa yana kallon Julde da yake girgiza kai

"Har kwana biyu zaku je kuyi, ka dai je idan na dawo daga kasuwa da dare in biyo in dauke ku... Shima Nawfal din zan hadu da shi daya tafi bai fada mun ba"

Gardama ba halin Khalid bace ba, duk a cikin yaran shi kadaine ba zai ja magana sau biyu da babba ba. Hakan yasa shi jinjina kai kawai yayi ma Julden sallama yana bin bayan yan uwan shi ya shige cikin makaranta. Julde kuma yaja motar shi yana nufar kasuwa, zuciyar shi tayi mishi nauyi fiye da kowanne lokaci.

*

Yanda yake cin abincin Daada take kallo, ya tattara hankalin shi kamar bai taba yin wani abu mai muhimmanci kamar wannan ba. Tausayin shine cike da zuciyar ta, daren jiya da ta zubo mishi taliya da miyar kifin da tayi ta zallar tumatiri da albasa taga ya kalleta

"Tumatir ne kawai da albasa Bajjo"

Ta fadi tana kiran shi da sunan da ta makala mishi kasancewar shi da daya tilo a wajen mahaifin shi. Tana dadewa bata kira shi da Nawfal ba. Tana gani ya saka cokali ya fara dibar miyar da kifin yana kaiwa bakin shi, saida ya sauke numfashi tukunna ya fara cin abincin. Yau ma haka, kwano ta samu daban tana zuba mishi miyar da tayi saboda shi kawai.

"Daada abincin nan yayi mun dadi"

Cewar Nawfal yana jin kamar ya samu waje ya adana dandanon abincin ya dinga daukowa yana tunawa a ranakun da zaici mai da yaji ko ya sha shayi saboda Nanna ba zatayi abincin da zai iya ci ba. Ya dade idan ya kalleta yana so ya tambayeta laifin shi, yana so yaji me ya taba yi mata mai zafi da ta dauki karan tsana ta dora mishi ba.

"Yarana da gidan uban sune ma abinda na dafa shi suke ci, ba zaka sakani girki biyu saboda baka cin yaji ba wallahi, ba zan iya wannan jidalin ba"

Ta kan yawaita fada mishi, ko a makaranta Nawfal Bukar yake amfani da shi ba Isiyaku ba. Ya san bashi bane baban shi ko bata tuna mishi ba, amman shi din yake ma kaunar da ya kamata yayi wa baban shi da bai san komai game dashi ba bayan suna. Sai dai abu na farko daya fara koya bayan magana shine yin shiru, akan abubuwa da yawa, musamman abubuwan da suka fi karfin fahimtar shi, da kuma wanda suke damun shi. Shiru yafi komai saukin yi, furta wasu abubuwan baya kawo gyaran su, ya taba furtawa Julde cewa Nanna tace gidan ba gidan uban shi bane ba.

Fadan da sukayi a gaban idanuwan shi harya mutu ba zai manta ba, yana da tabon dukan da Saratu tayi mishi a bayan shi har gobe. Shiru yafi komai sauki a wajen shi, yanzun ya kara fahimtar duk abinda ake so yaji za'a iya fada mishi ba saiya tambaya ba, abinda yake son ji kuwa koya tambaya idan ba'a son fada mishi ba zaiji ba.

"Kar dai ka fado daga kujerar nan wajen santi"

Daada ta fadi tana mishi dariya

"Ba dai zai hanani yabon girkin nan ba dan yayi mun dadi... Idan zan tafi kika dibar mun miyar nan zata dade bata lalace ba?"

Kallon shi Daada tayi

"Zata iya kwana biyu dai tunda ba sake dafawa zakayi ba, ko akwai fridge a dakin ku?"

Kai ya daga mata saboda ya cika bakin shi da shinkafa

"To bari sai ka karo kayan miya da kifin in maka da yawa, idan kaje saika saka cikin fridge ka dinga diba"

Murmushi yayi, matsayin Daada daban yake a wajen shi, ko ganinta yayi sai yaji wani sauki a cikin ran shi. Da duk wani abu da zatayi kuma da yanda take faranta mishi. Mikewa tayi tana shiga daki ta fito da hijabi a hannunta

"Gara inje barkar nan sai ma in biya in taho da Madina..."

Cewar Daada tana saka hijabin ta

"Kibari zanje in dauko ta"

Kai ta girgiza mishi

"Ba nisa da inda zanje... Sai na dawo"

Kai Nawfal ya daga

"Allah ya tsare. A dawo lafiya"

Daada ta amsa tana ficewa daga dakin. Abincin shi ya gama ci ya dauke kwanonin ya kai kitchen, ya dawo ya zauna yaji sallamar Khalid daya amsa, uniform din da yake jikin Khalid din na tabbatar mishi daga makaranta kai tsaye nan din ya nufo

"Da baka jirani mun taho tare ba gashi na zo ai"

Dariya Nawfal yayi

"Ka kyauta. Daman bance ba zaka zo ba ai, kawai jiyan na so tahowa..."

Takalma Khalid ya cire yana sake yin sallama ya shiga cikin falon, jakar shi ya fara saukewa dan a cikin ya zubo duk wani abu da yake tunanin zai bukata, yaji me Julde yace, amman yasan wahalar dai yazo gidan Daada. Idan ta saka baki dole yabar su su kwana biyu. Fada ne Nanna zatayi idan ya koma, to ko bai zo ba Nannar shi ba zata rasa dalilin yin fada ba, shisa bai koma ta gidan ba yayi tahowar shi, zaice mata Daddy ne yabar shi.

"Ina Daada?"

Ya tambaya

"Wai zatayi barka sai ta taho da Madina daga makaranta kuma..."

Kai Khalid ya jinjina yana mikewa

"Ni yunwa nake ji"

Kitchen ya wuce ya zuba abinci iya wanda yake tunanin zai iya cinyewa yana hadowa da wani filet din daban ya dawo falon, kan kafet ya zauna ya ajiye filattan a gaban shi yana janyi jakar shi ya bude. Mangwaro ne manya guda biyu ya dauko

"Mangwaron ne a jaka Hamma?"

Nawfal ya fadi yana dorawa da

"Ko dan meye ba za'a samu a jakar ka ba"

Dariya kawai Khalid yayi, inda sabo ya saba jin suna mishi wannan surutun. Kawai yafi yarda da ya saka duk wani abu da yake tunanin zai iya bukata a cikin jakar shi ta makaranta. Har paracetamol zaka samu cikin jakar, inka tambaya zaice maka

"Idan naji kaina yana ciwo fa? Tunda ba sanar dani zaiyi kafin ya fara ba"

Akwai ranar da suke dawowa daga islamiyya takalman Salim suka tsinke. Khalid ya zage aljihun gaban jakar islamiyyar shi ya zaro takalma silifas yana mikawa Salim din yayi gaba abin shi. Su duka binshi sukayi da kallo na wasu dakika kafin su kwashe da dariya. Wata rana dan tsokana ko sabulu ne ya kare musu a bandaki zakaji suna

"A duba jakar Khalid ba za'a rasa ba"

Shiru yake ya kyale su kamar yanda yayi ma Nawfal din yanzun. Abincin shi ya gama ci ya tashi da filattan yana zuwa ya wanke mangwaron, a fridge ya saka saboda Nawfal ya siyo daman, ya kuma san ba zai sha ba sai yayi sanyi ko yaya ne, idan ma yayankawa akayi zai dauki na shi ya saka a fridge. Yanda Nawfal baya mura har mamaki abin yake ba Khalid, idan ya sha sanyin da

Nawfal yake sha na rana daya a sati saiya kwanta gadon asibiti. Da ya fito ma bai zauna ba, dakin da suka saba sauka ya nufa, wanka yayi ya fito ya dawo falon daga shi sai gajeran wando

"Geez Hamma..."

Nawfal ya fadi yana kare idanuwan shi, kallon kan shi Khalid yayi, yanda Nawfal din yayi wani zai iya zaton babu kaya Khalid ya fito, karamin tsaki yaja

"Kasan shekara bata fi daya ba a tsakanin mu ko? Ba zaka daina ce mun Hamman nan kana dora mun girma ba"

Batare da Nawfal ya sauke hannun shi daga kare idanuwan shi da yayi ba yace

"Ka dai girmeni, zan daina in ka daina ce mun Bajjo"

Wucewa kawai Khalid yayi abin shi. Mikewa shima Nawfal din yayi, sai da ya kara watsa ruwa, lokacin daya fito har Khalid ya gama shirin shi ya fita. Shima shiryawa yayi cikin farin yadi harda hula bula ya saka kamar takamin shi daya dauko. Kafin ma ya fito yaji dawowar su Daada saboda rakadin Madina da take kwala mishi kira, sanda ya fito Khalid na fadin

"Lallai Madina, kamar baki ganni ba ko?"

Ko kallon shi batayi ba ta ruga da gudu tana fadawa jikin Nawfal hadi da zagaya hannuwanta jikin kafafun shi

"Hamma na dauka ka tafi kabarni"

Kanta ya shafa

"Nace miki ina nan har ki dawo makaranta ai... Masallaci dai zamu tafi ni da Hamma yanzun mu dawo, me zan siyo miki?"

Daga kai tayi tana kallon fuskar shi

"Biskit"

Khalid da yake zaune yace

"Ni ina da biskit din ai, ba zan baki ba tunda baki kulani ba"

Juyawa tayi ta kalli Khalid

"Hamma na zai siyo mun ai dai, ko Hamma?"

Kai Nawfal ya jinjina yana dariya

"Ki je ki cire uniform, Daada tayi abinci mai dadi"

Murmushinta ne ya fadada

"Tuwo ta dafa?"

Wannan karin har Khalid dariya yayi da Madina bata ga dalilin su nayin dariya ba. Nawfal yace anyi abinci mai dadi, shisa tayi tunanin tuwo ne

"Shinkafa"

Lokaci daya fara'ar fuskarta ta dishe tana raba jikinta da Nawfal din

"Shinkafa kuma"

Ta furta ranta a bace tana sake saka su dariya. Daki ta wuce harda jan kafafuwa a dole ranta ya baci da aka dafa shinkafa ba tuwo ba.

"Daada zama dake yarinyar nan kaf ta kwashe halin tsofaffi, ace ga shinkafa amman tuwo ne a ranta"

Khalid yace yana dariya

"Ku da bakuyi halin tsofaffin ba ai sai kuyita fama da shinkafar ku, amman ni tuwo zan mana anjima"

Mikewa Khalid yayi

"Tafdin, aci tuwo lafiya..."

Dan shi baya so, tuwo da danwake na cikin abincin da yunwar da zata saka shi cinsu ba karama bace ba. Sallama suka yiwa Daada suna fita masallaci.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

03

2003

"Adee..."

Ya kira ta da sunan da Khalid ya saka mata tun lokacin baya iya kiran sunan ta, maimakon Fadila din sai ya gajarce shi zuwa Adee da kowa yake kiranta da shi yanzun

"Ke bakya jin rana?"

Kai ta girgiza mishi, duk rashin magana irin ta Nawfal bai kai Adee ba. Dan ta ita duniya bata tashi ba, komai da sanyi-sanyi takeyin shi. Kusan ita ta kwaso jikin fulanin. Yanzun haka idan kaganta ita da Nawfal din babu wanda zaice itace babba, kanta da wahala idan ya kai kafadar shi, bata da tsayi kuma bata da jiki. Sai hasken fatar da kusan gadon shi sukayi. A gajiye take jinta, ta rasa inda Daddy ya tsaya da yau baizo daukar su ba. Ta riga da ta saba da anyi hutu ta fito a bakin gate take samun motar shi yana jiran ta.

"Yau Daddy ya dade..."

Tayi maganar cike da kosawa. Nawfal bai amsa ta ba, baisan me zaice mata ba. Inda yana da zabi zai zauna a makaranta abin shi. Duk satin duniya sai Daddy yazo ya gansu. Wasu satikan da Khalid yake zuwa. Sai dai a wani bangaren idan ya tuna zai ga Daada sai yaji komawa gida ba abu bane mai muni kamar yanda zuciyar shi take fadi. Sati ukune kawai hutun nasu, idan ya rike numfashin shi kafin ya sauke zaiga kwanakin sun wuce kamar ba'ayi su ba. Zai kokarin gujema Nanna a satikan.

"Daddy muna ta jiran ka"

Muryar Adee ta katse mishi tunanin da yake, yana daga kai ya kalli Daddy da yake mishi murmushin da yake mayar mishi. Sai yaji kamar anfi sati rabon da yaga Daddyn saboda yanda yayi kewar shi

"Ba kun gujeni kun zabi boarding ba yaran nan?"

Dariya sukayi gabaki dayan su. In da zasu biye Julde sam ba zasu hada hanya da makarantar kwana ba. Ya fiso ya dawo gida ya gansu kafin ya kwanta, idan ya tashi da safe ma ya gansu kafin ya fita. Saboda su baya tafiya ta wuce kwana biyu, kewar yaran shi zata fara tambayar shi. Sai dai a lokaci daya kuma bashida zuciyar hana su abinda yaga muraran suna so. Da zai iya da ba zasu zo makarantar kwana ba, musamman Nawfal da baya kaunar yaga yayi mishi nisa.

Su Adee yaran shine, jinin shine, daga jikin shi suka fita. Ba zai karya ba suna da matsayin da za'a kai ruwa rana kafin wani ya taka shi a zuciyar shi.

Amman Nawfal, matsayin Nawfal abune da ba zai iya furtawa ba, babu kalaman da zai iya amfani da su ya misalta yanda yake jin Nawfal gab da zuciyar shi.

"Amana ta ne Julde, yaron nan amanata ne"

Abinda Daada ta dinga jaddada mishi, abinda yake so ya kalli ba ita ba har kowa yanzun yace

"Nawfal amanata ne, ni ya kamata Bukar ya ba amana..."

Saboda Nawfal ya fito daga jikin bukar ne kawai, amman dukkan wata kauna da uba zai yiwa dan shi itace yake yiwa Nawfal. Kuma yana godewa Allah idan yaga irin murmushin nan a fuskar Nawfal. Idan yaga yanda Nawfal yake nuna mishi ko duniya zata hade waje daya tare da mutanen cikinta in dai zata sake budewa to zai riko hannun shi a matsayin Uba.

Soyayyar da take tsakanin su mai girma ce
Sai dai rubutacciyar kaddarar da take tsakanin su tana son danne girman soyayyar

"Bajjo jiba idanuwan ka, kana ma cin abinci?"

Dariya Nawfal yayi me sauti

"Baka ga yanda Adee ta koma ba"

Kallon su Adee tayi

"Rabon da in koma wani abu anfi shekara uku, ina nan yanda nake... Da gaske idanuwan ka sun rame"

Akwatin shi daya tashi daga kai yake kokarin dauka kafin Julde ya karasa ya karba, baiyi musu ba ya sakar mishi. Ko siyayya ya fita dasu shi yake rike ledojin, duk yanda zasuyi su karba zai ce

"Yaushe hannuwan ku zasu iya daukar wannan kayan. Da nauyi sosai"

Da akwatin Adee ya hada ya saka su bayan motar

"Yanayin abincin ka ya sa bana son ka da makarantar kwana Nawfal, nasan wahala zaka sha"

Gaban mota Nawfal ya bude ya shiga. Adee ta hau baya. Daddy ya zagaya ya zauna mazaunin direba ya rufe murfin. Har ya tayar da motar ya juya yana mitar yanda Nawfal din baya cin

abinci duk ya rame. Murmushi kawai Nawfal yayi

"Ina ci fa Daddy, dan baka gani na kullum ne shisa..."

Kai Julde yake girgizawa, ko satin daya fita da yazo ganin su bai ga yayi zuru-zuru haka ba. Shiru kawai Nawfal yayi, dan baisan me zaice ba. Julde baisan cewa yafi koshi a makaranta fiye da gida ba. Tunda yana da zabin na yaci abinda aka dafa ko akasin haka. Idan shinkafa da miya ne, ya amshi fara yana da kifin gwangwani zai juye a ciki yaci abin shi, wata rana zaici snacks. A gida bashi da wannan zabin, akwai kifin gwangwani da Daddy kan ce saboda shi yake siyowa. Kamar kuraye haka su Khalid suke akan nama, shine kawai bayacin nama Kwata-kwata.

Ba allergy bane ba, kawai bayajin zai iya cin nama tun yana da karancin shekarun shi. Da yagan shi a cikin miya ma hankalin shi tashi yake, daga kaza har sauran nau'in nama. Baisan a shekarun yarintar da ba zai iya tunawa ba ko yaci, iya wanda zai tuna kawo yanzun baya hada hanya da duk wani abu nama. Amman kifin nan bai isa ya taba ba. Idan danyene aka kawo dan ayi miya. Nanna zata sarrafa shi yanda zai zama haramiyar shi. Shisa bai taba saka rai a duk wani abu da saiya fito ta hannunta sannan ya iso wajen shi ba.

Idan Adee tazo hutu yana jin dadi, yana cin abinci da miya, da kanta take shiga kitchen tayi mishi miya ta kuma juye a rubber ta kai mishi dakin shi.

"Me yasa kike haka Nanna?"

Shine tambayar Adee duk idan Nanna tayi kokarin hanata. Wasu ranakun harda duka amman ko bandaki Nanna ta shiga sai tasan yanda tayi ta kaima Nawfal din wani abu da zaiji dadin shi. Kifin gwangwani kuwa ita da Khalid suna diba su kai mishi ya ajiye a dakin shi, Khalid da dai-dai zai dauka. Adee zata iya daukar kwalin gabaki daya, wata rana nata na makaranta randa ta dawo hutu take zuwa ta kai mishi. Kamar bata ci kwata-kwata tana tarawa ne don shi. Kananun abubuwa irin wannan yasa yake jinta har ran shi.

"Ka daina jira sai Nanna ta baka abu, idan kagani kana so ka dauka ka tafi abinka"

Ta kan fada mishi wasu lokuttan idan ta kai mishi wani abin. Sai dai yayi dariya, baya son tashin hankali sam, duk wani abu da zaiyi ya gujema fadan Nanna zaiyi, wani lokacin zai rantse ganin shi kawai harzuka matar yakeyi. In ba Daddy yana nan ba baya shiga bangaren ta. Ko yunwa zata kusan halaka shi daya leko ta window yaga tana falo saiya koma, in Khalid yana nan zai mishi magana ya zubo mishi abinci. Idan baya nan kuma zaici duk abinda yake da shi a bangaren shi.

Yanzun ma da suka karasa akwatin shi yaja zuwa zai nufi na shi bangaren

"Kamar jira kake Nawfal? Ba zaka shiga kaga Nannar taka ba?"

Murmushi yayi

"Daddy nagaji, zan watsa ruwa tukunna..."

Kai kawai Julde ya daga ya rufe bayan motar yana daukar akawatin Adee da tayi saurin kamawa tana fadin

"Bajjo zaka ba, akwai wasu kayan shi a ciki, idan ya kwashe naje in dauka"

Ta karasa maganar tana kallon Nawfal da fuskar shi take dauke da alamar tambaya. Kai ta dan daga mishi, cikin sanyin jiki ya karaso yana jan akwatin nata ya hada da nashi ya nufi bangaren shi. Ita da Daddy suka wuce cikin gidan tana bashi labarin da bashi da kan gado dan kar ya tambayeta wanne kayan Nawfal ne a akwatin ta.

*

"Takardun meye wannan?"

Saratu ta tambaya tana rarraba takardun a tsakanin hannuwanta, a karo na babu adadi tana jin takaicin rashin ilimi, daya daga cikin rashin gatan da maraici yayi mata. Duk da boko ce karshen abinda aka damu dashi a inda ta tashi, amman ko bakomai an sa taje makarantar allo, babu wanda ya damu da yanda rayuwarta zata kasance.

"Takardun filayen Bajjo ne za'a siyar da wasu a sai mishi gida"

Wani abu taji ya taso da ba zata ce ga daga inda yake ba, amman dacin shi har akan harshen ta. Filaye Julde yace, hakan na nufin ba daya ba ba biyu ba tunda yana kiran wasu daga ciki za'a siyar a sai mishi gida.

"Yana da dukiyar shi Saratu, Nawfal na da dukiyar da tunanin ki ba zai taba hangowa ba. Ba taimaka mishi nake ba dan ina biya mishi kudinn makaranta, ganin dama ta ne kawai..."

Kalaman Julde suka dawo mata wani lokaci can baya da tayi tsegumi akan yanda zaman Nawfal din yake karin nauyi akan shi. Ba zata daina wahalar da kwakwalwar ta wajen tunanin inda Bukar ya samu arziki har haka ba. Bukar fa, Bukar dai daya bar kauyen su da sunan zuwa neman ilimi. Tsoron kar tunanin ta yayi karadin da wani zaiji shisa take tausar shi, amman akwai ayar tambaya mai girma akan wannan kudin da Bukar yabar wa Nawfal kamar yanda akwai babbar tambayar da kowa yaki yarda ya furta akan asalin haihuwar Nawfal.

"Dukiyar Nawfal bata karewa ne? Har nawa yake da..."

Sauran maganganun suka koma mata saboda yanayin juyawar da Julde yayi yana kallon ta

"Meye matsalar ki da dukiyar shi? Sanin yawan ta amfanin me zaiyi miki?"

Kauda kai tayi gefe, abinda take ji yana kara ninkuwa, wannan dukiyar da yake kira Nawfal na da ita da su Salim take hangota, duk wani jin dadi da yake gidan duniya rayuwar yaranta take hangowa a ciki.

"Su Khalid ma ya kamata ace suna da gidajen su yanzun tunda kana da halin"

Karamin tsaki Julde ya ja kafin ya taka ya fisge takardun da suke hannunta yana mayarwa cikin jakar shi. Bai san me yasa daya dawo hannunta kan jakar shi yake fara sauka ba, sai kuma ta dame shi da tambaye-tambayen da bayaso kan duk wata takarda da zata gani kamar ya aiketa.

"Duk takardar da zaki gani in ba zaki iya karantawa kiji ko ta mecece ba karki sake damuna da tambaya"

Maganganun shi sunyi mata zafi ba dan kadan ba, duk da ba yau bane rana ta farko da yake amfani da duk damar da zai samu na goranta mata rashin ilimi kamar laifin nata ne. Karatun hausar da ya koya daga bayane da dan kalaman turanci daya tsinta akan titi suke kara bashi damar zaginta haka.

"Ka sama mun makaranta ko ta yaki da jahilci ce..."

Ta furta cikin wata irin sanyin murya. Sosai Julde ya kalleta wannan karin kafin ya kwashe da dariya yana girgiza kai kawai. Har ranshi dariya ta bashi. Duk tsayin shekarun nan batayi tunanin shiga makaranta ba sai yanzun? Saboda tana son saka ma shige da ficen shi idanuwa fiye da yanda takeyi yanzun. Takardun shi ya mayar tsaf ya gyara ya karasa yana samarwa jakar waje ya ajiye. Fita yayi daga dakin baccin nasu zuwa falo yana jin motsin Adee a kitchen, hakan yasa shi tunkarar kitchen din ya kuwa ganta tana wanke-wanke.

"Sannu da aiki..."

Da murmushi a fuskarta ta juyo

"Daddy Am... Ba wani aiki bane ba fa"

Kai ya jinjina, komai ma in dai ya danganci hidimar cikin gida amsa daya Adee zata baka, dan wajenta ba aiki bane ba, har mamakin kokarinta yakeyi a kankantar da take da shi, gashi sanyin halinta baisa tana da sanyin jiki ba

"Ni ma zan leka Daada ne"

Wannan karin fuskarta cike da roko tace

"Dan Allah zanje... Saura kadan in karasa..."

Dan jim Julde yayi sannan ya amsa

"Bari to in duba su Khalid, nasan zasuje suma sai su shirya duk mu fita gabaki daya"

Murmushi tayi har hakoranta suka bayyana kafin ta juya kamar tana son kara sauri wajen ganin ta gama da wuri. Ficewa yayi daga bangaren nasu gabaki daya yana nufar nasu Khalid. Hannun kofar ya kama ya murza yana shiga da sallamar da Nawfal ne ya koya mishi yinta a ko ina zai shiga

"Daddy baka yi mun sallama ba ka shigo"

Ya kan fadi har saida ya saba da yin sallamar da a baya bata dame shi ba, kai tsaye yakan tura kofa ya shiga waje. Yanzun kam a kasuwa ko shagon wasu zai shiga da yake a bude sai yayi sallama, yana ganin yanda hakan ke siya mishi kima a idanuwan mutane da yawa. Ba kowa a falon sai Salim da ya kara shigewa cikin kujera kamar yana son hadewa da ita, tv nata aiki amman babu sauti hakanne ma yasa Julde jin sallamar shi da Salim ya amsa can kasan makoshi. Idan wani da baisan yaron ba yagani zai dauki hakan a matsayin rashin girmamawa. Kuma a wajen Salim ba haka bane ba, yawancin maganar shi duk daga kasan makoshi take fita da yanayin kamar an mishi dole dauke a fuskar shi.

"Daddy..."

Nawfal daya fito daga dakin baccin shi jin sallamar Daddy ya kira yana dorawa da

"Ina kwana"

Murmushi Julde yayi

"Lafiya kalau, kun tashi lafiya ko?"

Kai Nawfal ya jinjina

"Ina Khalid? Ku shirya muje gidan Daada, amman ba kwana zakuyi ba"

Dakuna fuska Nawfal yayi

"Da ma ina so inje fa Daddy, munyi maganar zuwan da Adee"

Kai Julde yake girgizawa

"Kwana daya to, dan Allah, gobe idan ka dawo kasuwa saika biyo ka dauke mu"

Numfashi Julde ya sauke yana dai-dai da lokacin da Salim ya fitar da wani sauti dake nuna alamar hirar su ta takura shi yana kara shigewa cikin kujera. Murmushi kawai Julde yayi

"Ku shirya to"

Sai da Nawfal ya jinjina mishi kai tukunna ya juya yana fita hadi da ja musu kofar. Nawfal kallon Salim yayi, baisan lokacin daya yanke hukunci dawowa bangaren da kwana da yini ba. Shima tunda yazo hutun nan yagan shi, kafin kaji hirar Salim zaka dade, zai iya tashi da safe baice wa kowa komai ba, ko hanya ta hadaku wucewa zakaga yayi kokarin ganin ya kauce karma iskar da kuka kwaso ta hadu da ta juna, magana ma idan yanayi kamar bakin shi cike yake da harshe saboda yanda take fitowa.

Nawfal zai iya cewa duk da Salim na cikin mutane shi kadai yake rayuwar shi, ko kasa shi cikin harkar ka da wahalar gaske ya shiga. Duk wani abu da zaisa ayi rikici Nawfal na guje mishi, shisa tunda ya dawo yaga Salim a bangaren da yake kira nashi ya daina zaman falo sam, akwai tv a dakin shi idan kallo yake son yi, shima zai saka sautin dai-dai kunnen shine kafin Salim yazo ya kwankwasa mishi yana fadin

"Ka rage volume din TV dinka Bajjo yana shigar mun kwakwalwa"

Duk wani surutu ma shigar ma Salim kwakwalwa yake kamar kunnen shi yafi na kowa ji

"Anya Hamma Salim ba vampire bane ba?"

Khalid ya taba tambaya bayan ya baro dakin shi a bangaren Nanna ya same su a falon da tazarar shi take wajen taku goma harma da wani dan sirqakon lungu a tsakani yana watsa musu wani irin kallo

"Me yasa ba zakuyi magana irin ta mutane ba? Ta ya mutum zaiyi bacci kun cika gida da ihu?"

Hada idanuwa kawai sukayi shi da Khalid suka mike suna barin bangaren gabaki daya. A cikin su babu wanda zaice ga rana daya da Salim ya taba lafiyar jikin su, amman akwai marin da yayi wa Adee kan tana wanke-wanke tana kida da cokula a cewar shi. Amman dukkan su suna shakkar Salim din. Nawfal ya juya zai koma inda ya shigo Khalid ya bankado kofar yana fadin

"Wai kasan wa nagani ku..."

Maganar ta koma mishi saboda idanuwan shi da suka sauka cikin na Salim da ya dage girar shi duka biyun, ko dan girar Salim kusan kullum a sama take, kamar baya sauke ta, hannuwa Khalid ya daga cikin ban hakuri yana motsa labban shi batare da yayi maganar da sauti ba yace

"Yi hakuri"

Yana takawa a hankali ya karasa inda Nawfal yake ya tura kafadar shi suna nufar dakin baccin Nawfal din da kamar jira yake Khalid ya tura kofar dariya ta kubuce mishi

"Ban san vampire na zaune a dakin ba ai"

Khalid ya fadi da alamar dariya a muryar shi, har mamakin ji irin na Salim sukeyi

"Daddy yace mu shirya zamu je gidan Daada"

Nawfal ya fadi har lokacin da alamar dariya a muryar shi

"Ni ai nayi wanka..."

Kai Nawfal ya jinjina

"Nima nayi wanka, ban dai ci komai bane ba... Zan karya a gidan Daada kawai"

Da gabaki dayan su suke karyawa a bangaren Nanna din, yanzun tunda kowa ya fara girma sai suke zaben lokacin yin karin idan ba ranakun makaranta da Julde ba zai bar su fita basu saka wani abu a cikin su ba ko yaya ne kuwa. Nawfal yana da kayan Tea din shi, akwatin da Adee ta bashi nata harda katon gwangwanin madara da bata fasa ba sai na Milo karami, da kifin wajen gwangwani ashirin. To kuma ma ya ga Salim ya sake kwaso wasu kayan tea din ya ajiye a kitchen din bangaren nasu, da kofuna da yawa ma da kananun kayan amfani, ya ga har gas din kitchen din an hada.

"To mu jira Daddy ya fito sai mu wuce..."

Cewar Khalid yana dorawa da

"Nasan da Adee zamu je, Lukman dai ba zai bar Nannar shi yaje wani waje ba"

Murmushi Nawfal yayi

"Auta kam babu inda za shi"

Suna nan zaune suna hira, ta window din dakin Nawfal da yake ta waje yake suka hango Daddy, kusan a tare suka mike suna fita

"'Hamma sai mun dawo"

Khalid ya fadi, hannu Salim din ya daga yana musu alamar su fita. Dariya sukayi a tare suna

ficewa, daman dan neman tsokana yasa Khalid yima Salim din magana. Har wajen motar Daddy suka karasa kusan a tare da Adee da take sanye da riga da wandon da zaka iya gani saboda hijabinta iya gwiwa ya tsaya, ta rataya jaka a gefe sai robar take away a hannunta.

"Dare yayi sanda na gama jiya..."

Ta furta tana mikama Nawfal robar da ya karba yana jinta da sanyi alamar a fridge ta kwana, dubawa yayi ta kasan robar yana ganin farfesun kifi ne ko miyar kifi, ba zai iya ganewa ba, ya dai san taliya aka dafa jiya da dare da miyar kifin da yasan ba zai iya ci ba dan yaga Khalid da ita, sanda ya shiga bangaren ma dan su gaisa da Daddy ne.

"Meye kika bashi ni baki bani ba"

Cewar Khalid da ko inda yake Adee bata kalla ba. Yanzun da suka kara hankali Nawfal yasan Adee dare take bi idan Nanna tayi bacci ta dafa mishi abu irin haka. Hannun shi na dama da baya rike da robar da ta bashi ya dora akan kirjin shi inda yafi tunani zuciyar shi take dan nan yaji ya dauki dumi sannan ya daga hannun yana nuna Adee da tayi murmushi, yasan ta fahimta, bashi da kalamai in dai akan kulawarta ne, amman tana da waje mai girma a zuciyar shi, Allah yake roko daya bashi aron rayuwa mai tsayi a tare da Adee dan ya kwatanta biyan ta duka kirkin da takeyi mishi.

Su baya suka shiga shi da Khalid ita tana shiga  gidan gaba. Har lokacin da murmushi a fuskar ta

Bata san duka labarin Nawfal ba
Amman tana hasaso rayuwar ta babu Daddy da Nanna
Tana hango dararen kadaicin da take tunanin yana fama da shi
Ita din ko kusa da matsayi na uwa ba zata hango ba balle ta taka
Amman in dai tana numfashi zata sama ma Nawfal duk wani sauki da yake a karkashin ikon ta
In dai har yaya mace na zama mahaifiyar da mutane ke fada zata zamewa Nawfal.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

04

Idan yaji ana cewa lokaci na gudu ada sai yayi ta mamaki, saboda shi sam baya ganin gudun lokaci. Musamman idan yana gida, yini daya sai ya zame mishi kamar yini biyu. Amman wannan karin zai saka baki idan ana maganar gudu na lokaci, saboda da gaske kamar idanuwan shi ya rufe a aji hudu ya bude su ya ganshi yana zana jarabawar gama sakandire ta aji shidda da ake kira da WAEC. Randa suka zana ta karshe sai yake jin abin kamar a mafarki, har Julde yaje ya dauko su bai dana jin shi kamar a mafarki yake yawo ba.

Sai dai ya koma kirga kwanakin da suka rage mishi a cikin gidan. Adee ta samu gurbin karatu a jami'ar Wudil, nisa ta sake yi musu.

"Ga BUK, me yasa sai Wudil? Quantity Survey din ne basu da shi a BUK?"

Ya tambayeta, bai taba zuwa Wudil ba, amman yasan kauye ce, kuma yaji wani a ajin su yana magana cewa babu mata da yawa a makarantar, duk wani abu da zata takura baya son shi sam. Murmushi kawai tayi

"Ka ce mun BUK zaka je kaima Bajjo, in har can din zaka sai in hakura da Wudil..."

Shirun da yayi murmushin Adee kawai hakan ya fadada

"Idan kana gida zan dinga kokarin dawowa weekend In shaa Allah"

Bai dai sake cewa komai ba, burin shi mai girma ne, bai kai da furtawa ba. Amman nisan da zaiyi wa gida da sunan karatu ba zai tsaya makarantun da suka sani ba. Ya fi kowa jin rashin Adee a cikin gidan, dan ma yanzun Julde kudin kashewa yake basu kusan kullum, ba zaici yana da matsalar abinci ba. Mai dadine kamar wanda Adee zata tsaya ta dafa mishi sai dai yaje gidan Daada yake samu. Islamiyya da ya koma yanzun bashi da lokaci mai yawa na zuwa gidan. Yanzun ma daya taso masallaci ya wuce yayi zaman shi yana nazarin darussan da akayi na ranar har sai da yayi sallar Magriba da Isha'i tukunna ya dawo gidan.

"Ina kaje tun dazun?"

Khalid da yake kwance cikin kujera ya tambaya

"In da ka aikeni"

Ya amsa yana wucewa, dakin su ya nufa ya ajiye jakar makarantar shi, ruwa ya watsa ya sake kaya sannan ya sake fitowa yana nufa kitchen, fridge ya bude yana ganin robobin ice cream din shi har biyu inda ya bar su tun daren jiya. Guda daya ya fiddo yana mayar da fridge din ya rufe ya karasa ya dauki cokulla har biyu ya dauraye su, yana daukar wani plate shima ya dauraye ya taka zuwa falon, teburin da ke tsakiyar dakin yaja zuwa kusa da kujerar da zai zauna ya ajiye plate din ya dora cokullan a sama yana ajiye robar ice cream din shi a gefe.

Sake komawa daki yayi ya dauko kifin gwangwani guda biyu tukunna ya samu waje ya zauna. Gabaki daya Khalid hankalin shi ya mayar kan Nawfal da yake bude kifin harya juye shi cikin plate, gani yayi ya bude robar ice cream din ya saka cokali a ciki, tashi zaune Khalid yayi

"Jikin ka na shan wahala a hannun ka Bajjo, kifi da ice cream?"

In dai akan zabin abinci ne ya saba da surutun Khalid din, bude baki Khalid yayi zai sake magana shigowar Salim ta saka shi ya mayar ya rufe

"Na dauka ba'a hada kifi da madara"

Salim yayi maganar cikin sigar da bata bukatar amsa kamar yanda ya saba, kana iya amsa shi yayi maka kallon "Da kaina nake magana, me yasa kake amsawa?". Kowa a gidan ya koyi zama da Salim, duk da haka kafadu Nawfal ya daga

"Har yanzun ban ci da yawan da zai mun illa bane ina jin"

Dan ba zaice ga ranar da yake hada shayi kuma da madara yaci da kifi ba. Kai Salim ya girgiza yana wucewa abin shi

"Da gaske abin nan dadi yake maka?"

Hararar Khalid yayi yana cigaba da cin kifin shi hankali kwance. Yana gama cinye kifin ya mike ya dauke plate din ya kai kitchen, yana dawowa ya hangi Khalid da robar ice cream din shi ya dibo a cokali yana shirin kaiwa baki, da gudu ya karasa amman har Khalid ya kai cokalin cikin bakin shi

"Ewww...Hamma...kace mun shine cokalin farko..."

Wuyan shi Khalid ya rike da alamu ke nuna dakyar ice cream din ya wuce ta cikin shi, fuskar shi a hade take gabaki dayanta, harya ciro cokalin kokarin tattara sauran dandanon ice cream din daya rage a bakin shi yakeyi amman ya kasa, hannu kawai ya iya dagawa Nawfal da ya dakuna fuska yana jujjuya robar hannun shi kamar zata sanar mishi idan Khalid din ya sha abinda yake cikinta fiye da sau daya. Kurkuro bakin shi Khalid yayi amman bai daina jin dandanon ba

"Nawfal meye a robar nan?"

Asalin sunan shi da Khalid ya sa Nawfal din amsawa da

"Ice cream"

Yana dorawa da

"Sau daya ka sha?"

Babu abinda ya tsana irin kurbi in kurba da abu a cikin kofi, ko kuma yana shan ice cream, ko yana cin wani abu kazo ka dauki cokalin ka ci da shi ka mayar a ciki, saiya ga kamar da sauran yawu a jiki ka mayar mishi. Idan Khalid na son ya bar mishi abu haka yake masa wannan rashin kirkin

"Wanne irin ice cream ne wannan?"

Numfashi Nawfal ya sauke

"Chocolate mint... Me ya faru?"

Kai Khalid yake girgizawa, komai na Nawfal ya fita daban, kamar kullum dalilin da zai sake banbanta da mutane yake nema. Kamar McLean yayi kankara haka ice cream din yake

"Sau daya na sha, na farko kuma na karshe da yardar Allah"

Khalid yace muryar shi na fitowa a gajiye. Dariya Nawfal yayi

"Me ya samu ice cream din? Me ya faru? Ba dai zaka ce babu dadi ba"

Wani irin kallo Khalid yake mishi

"Akwai dadi, a sha lafiya"

Da murmushi a fuskar Nawfal ya nufi kitchen dan ya dauko wani cokalin, daga can dakin su ya wuce ba sai Salim ya dawo falon ya kore su ba. Ko da Salim ba zai fito ba lokacin baccin shi yayi, kome zaiyi da wuri yake yi ya gama, karfe tara idanuwan shi sun fara nauyi, har mamakin Khalid da zai iya kai karfe daya na dare zaune yana kallo yakeyi, kuma washegari ya tashi su tafi sallar asuba kamar lafiyar shi kalau. Shi kanshi zaiyi kamar an dora dutse, bacci na da muhimmanci a wajen Nawfal.

**

"Daada..."

Ya kira muryar shi can kasan makoshi, hannu tasa tana share hawayen da suka kasa daina zuba daga idanuwanta, ya dauka da Julde zaifi samun matsala, sai dai soyayyar da ke tsakanin su da take tasiri akan Julde ko yaushe ita tayi nasara. Nawfal na ganin yanda tafiyar shi wani gari da sunan karatu ne karshen abinda Julden yake so balle kuma ace wata kasa.

"Cikin kudina, kai da Daada kunce ina da kudi, in dai zasu isa..."

Julde bai barshi ya karasa ba, da wani nauyi a muryar shi yace

"Me yasa kake tunanin kudi ne matsala ta da tafiyar ka? Bajjo ina da kudin da zan fitar da ku dukan ku karatu kasar waje, ba kudin bane matsalata, nisan ka, nisan da zakayi ne damuwata"

To ga damuwa fiye da wadda ya gani a tattare da Julde nan shimfide kan fuskar Daada, kukan da takeyi gabaki daya ya kashe mishi jiki, zuciyar shi daya ke tunanin ba mai raunanata kan tafiyar ce yake ji tana mishi rawa

"Daada..."

Ya sake kira kamar hakan zai isar da sakon da baisan ta inda zai fara fada mata shi ba. Yana bukatar tafiyar, jin shi yake kamar yana cikin wata yar karamar kwalba, watakila tafiyar ta fito da shi daga cikinta, duniyar shi yar karama ce, haka ma mutanen da suke cikinta. Ba fadadata yake son yi ba, asalima yana jin wajen mutum daya ya rage mishi, daya cike shikenan. Yana dai son tafiya saboda da dalilai da ba zai iya rabawa da kowa ba.

"Daada makaranta ce kawai fa, zan dawo... Ki daina yi kamar na tafi kenan"

Kai ta jinjina, zuciyarta na wani irin ciwo, tafiya ta rabata da mutane da yawa, tafiya tayi mata sanadin abubuwa da ba zasu lissafu ba. Idan tace ko sunan tafiya bata son ji wasu zasuyi mamaki, amman dalilanta masu karfine. Shi da Madina ne mutane biyu rak da suka rage mata da take jin in dai tana numfashi ba zata bar wani abu ya rabata da su ba. Ko da yace makarantar kwana zai tafi hankalinta ya tashi, sai da Julde ya fada mata makarantar a cikin garin Kano ne, duk da haka sai da taji duk satin duniya Julden na zuwa ya dubasu.

Amman baccin kirki batayi duk asabar din duniya sai Julde ya biyo ya sanar mata da cewa Nawfal din na lafiya take samu nutsuwa. Yanzun kuma yazo mata da zancen tafiya wata kasar amurka, yana tuna mata abubuwan da ba mantawa tayi ba, amman ta samu waje ta adana su idan ba ranaku irin yau ba basa kwacema adaninta sai ta basu damar hakan.

"Dan Allah Daada... Kina daga mun hankali"

Hannu tasa tana sake dauke kwallar da ta taru cikin idanuwan ta

"Naji tafiya da sunan karatu Bajjo, tafiyar da batayi mun dadi ba, naji tafiya da dalili da tafiya babu dalili, duka basuyi mun dadi ba..."

Kai yake girgizawa tunda ta fara magana, ga wani abu daya taso daga zuciyar shi yana tokare mishi makoshi

"Karki hada mu, ko a tunanin ki karki hada mu, ba zan sake cewa daga jikin shi na fito ba.

Amman ni daban ne, ni bashi bane ba, ba zan watsar da ku kamar baku da muhimmanci a rayuwata ba, karatu zan tafi, karatu zanyi in dawo Daada... Zan dawo"

Ya karasa cikin dishewar murya, ba zai ce ga ranar karshe da yayi kuka ba, amman yanzun alamun shi yake ji. Ya san zafin da Daada take ji, amman baya son inda tunaninta yake son daukarta ya kaita balle ta ja shi su tafi tare. Shafine daya dade da rufewa. Abinda ya wuce ko kayi tunani a kai ba zai canza komai ba, shisa yake zabar barin shi inda yake, a matsayin abinda ya wuce.

"Zan dawo Daada... Ni bashi bane"

Ya sake fadi, murmushi tayi mai sauti duk da kukan da take ta kokarin tsayarwa. Yanda Nawfal yake jaddada bambanci da yake tsakanin su da Bukar na karya mata zuciya. Kila tsayin shekaru yasa shi manta muryar Bukar da take ji a cikin tashi muryar, duk idan zai shigo gidan da sallama sai zuciyarta ta doka a cikin kirjinta, ko shigowa yayi fuskar Bukar take gani, ko a dabi'a bambanci da yake tsakanin su ba mai yawa bane ba. Ba ta da karfin fada mishi haka, ko tana da shi ma ta ina zata fara?

"Allah yasa hakan ne mafi alkhairi"

Ta furta tana saka Nawfal sauke numfashin da yake rike da shi

"Duk karshen shekara fa anan zanyi shi In shaa Allah..."

Kai Daada ta jinjina, zuciyarta taki natsuwa da tafiyar, in da zai hakura zata fi son haka. Da tana jin ta isa ta hana shi tafiyar zata hana ko dan gudun da takeyi na kar tarihi ya maimaita kan shi.

"Daada"

Nawfal ya kira, baya son yanayin da yake cikin idanuwan ta da kan fuskarta

"Ina Madina? Ba tace anyi hutun islamiyya ba? Ina taje?"

Ya tambaya cikin son sauya maganar gabaki dayan ta, fuskarta Daada ta goge sosai, dan har gefen zaninta ta kama tayi amfani da shi. Sai da tayi gyaran murya sannan ta amsa Nawfal din

"Nan bayan gida suke taron suna gobe idan Allah ya kaimu, shine taje tayi musu kunshi, tun jiya ma take tayi"

Dan dakuna fuska yayi

"Kin sansu ne Daada, kince jiya ma taje fa"

Kai ta jinjina mishi

"Bata nisa ai, suma dan ana mutunci da sai dai su same ta a gida....baki ma nake gudu, kowa zancen kunshin ta da kuma karancin shekaru yakeyi"

Numfashi Nawfal ya sauke, dole za'ayi magana, idan har kalar zanukan da yake gani tanayi ne a littafi, tun ba yanzun bama idan yazo ya same ta tana aikin da aka basu a makaranta, littafin duk da zai dauka ba zaka rasa yar flower da ta zana a jiki ba. Idan yace

"Madina ana ina kika ga wannan zanen?"

Zata amsa shi da

"Ba ko ina fa, kawai na zana ne"

Yanzun da ta dan fara hankali ne take ware litattafan da take zanen a ciki daban dana makaranta. Yanzun gashi alamu sun nuna kunshi zai iya zame mata sana'a. Kawai baya son ta da zuwa wani waje da sunan kunshi ne, kowa yazo gida ya same ta. Kasa hakuri yayi sai da yayi wa Daada mitar

"Bajjo nace maka dan makota ne kawai shisa taje, karka isheni dan Allah... Ka fita ka tambaya gidan su Salaha, ka kirata ka rabu dani"

Shiru yayi yana gyara zaman shi a kujera, zai dai jira tazo ya ganta sai ya tafi. Alawoyin daya siyo da hannun shi yake son ya bata, ba kwana zaiyi ba, yanda yake lallaba Julde ba zai sake tambayar shi wani abu ba har yabar kasar, ciki kuwa harda kwana gidan Daada.

"Rochester institute of technology"

Sunan makarantar ya fado mishi a rai yana saka shi sake sauke numfashi a karo na ba adadi tun wayewar garin. Wani yanayi yake ji tunda ya ga hotunan makarantar a Café din da yaje domin yin binciken makarantar da zatayi dai-dai da ra'ayin shi, daga hotunan yake jin kamar wani abu mai girma da ya wuce karatu zai faru da shi a kasar New York da take yankin amurka, a cikin makarantar da sunan ta kawai ya sa murmushi kwace mishi.

*

"Sai yanzun kake dawowo Julde? Karfe biyu uku saura? Ka kasa yima kanka fada, idan anyi maka ba zaka saurara ba"

Muryar Saratu ta daki kunnuwan shi, da alama a hanyar da zata hadaka da dakin baccin su take tsaye, sake rakubewa yayi jikin bangon kitchen din yana dana sanin shigowar da yayi. Wani irin kunnuwa gare shi da komin baccin da yakeyi takun tafiya idan akayi kusa da kofar

dakin shi saiya bude ido. Ko dakin da yake kusa da nashi da Lukman ne a ciki yasha shiga da dare ya watsa mishi zagi saboda yana buga kofar bandakin da yake cikin dakin idan ya farka zai shiga.

Fadan su Julde da tun bashi da hankalin gane inda ya dosa ya sha tashin shi cikin dare. Daya fara hankalin gane yawancin maganganun su saiya ke tsintar kan shi da kallon Julde da wasu irin idanuwa na daban, yana kuma cika da mamaki ko da yaushe na yanda yake Daddyn su a gaban su, yake cikin rigar mutunci da kamala idan yana gaban su, amman sai ya cire ta ya yarda daga yayi tunanin sun dauke idanuwan su daga kan shi. Mutuncin da suke tunanin yana da shi, mutuncin da suke ganin zasu daki kirji a kai a waje shine yake zubarwa da duk rana.

"Meye a jikin matan nan da kake bi da ni na rasa?"

Maganganun Saratu kenan da suka kasa gogewa daga cikin kunnuwan Salim

"Idan na miki bayani ba zaki gane ba, idan ba kafafuwan ki kika saka a takalmana ba..."

Shine amsar da Julde ya bata wani dare da ba zai tuna a cikin wacce shekara ko wata yake ba, amman dare ne a cikin dubban darare da ba zai taba mantawa da shi ba. Saboda dare ne da wayewar garin shi ta zo mishi da wani sabon al'amari. Yana son Daddy, soyayya da ba zai taba iya kwatanta yawanta ba, shisa yake so ya fahimce shi, fahimtar da yake kiran Saratu ta kasa mishi ita, tabbas ba zata iya saka kafafuwanta a takalman Julde ba, amman shi zai iya. Ba shi da kyawun sauran yaran gidan, akan ce Khalid duk yafi su kyau. Shima ya yarda, amman ya fi kowa hasken fata, sannan kuma dogo ne, irin dogayen da ko a cikin masu tsayi sai ka dade baka gan su ba.

Kuma da yake da tsayi shi din ba siriri bane, dirarren namiji ne da tun yana sakandire yake kula da yanda yan mata suke son magana da shi, hayaniyar da baya so take saka shi share su. Amman tunda ya samu gurbin karatu a jami'ar Bayaro bangaren likitanci sai hakan ya kara haska shi a idanuwan mutane da yawa, baya mu'amala da kowa a ajin, sallama ce take rabasu, amman tun sakamon jarabawar su ta farko da aka kafe ya zamana shine a saman kowa wajen samun maki yasa mutane suka kara sanin shi.

Yanda duk yakan so zamewa sai sun saka shi yayi musu bitar wasu cikin darussan da sukan yi, musamman ma wa'anda suka hada da lissafi. Mata bashi yake kula su ba, sune suke kula shi. Ranar farko da yayi watsi da duk wani gargadi da zuciyar shi take mishi akan abinda ya kudurci yi tun safiyar da zai fita bayan yace wa Saratu

"Zan kwana a makaranta yau Nanna, akwai abubuwan da zanyi"

Bai san ya akayi bata ji muryar shi na rawa ba, da kuma tsoron da yake shimfide a cikin idanuwan shi, watakila da ta tambaye shi menene abinda zaiyi a makaranta a ranar daya canza komai, amman bata tambaya ba

"Allah ya tsare, kar dai ka zauna da yunwa"

Shine amsar daya samu, daya hadu da Khalid ma a hanyar fitar shi, gefe Khalid din ya rabe ko magana baiyi mishi ba. Shidin ba ma'abocin ciye-ciye a waje bane ba, ko zai yini a makaranta ruwane zai siya yayi ta sha. Ko yana gida idan zaiyi kyakkyawan karin safe zai iya kaiwa dare bai sake saka komai a cikin shi ba

"Dogaye da cikin zani aka sansu, amman kalli dan abincin da ka zubo"

Julde kan tsokane shi, wani lokacin har Saratu na shiga

"Kuma fa tun abincin safe banga ya kara cin komai ba, da abinci ke saka jiki yaron nan tsayin nan ma ba zaiyi ba"

Murmushi yakan yi ya wuce su, tunda da wahalar gaske kaga ya zauna anci abinci dashi gabaki daya, baya son yin zagi a gaban su Julde, to kuma ko Lukman saiya saka shi yayi magana saboda yanda yake tauna abinci kamar yana cin karfe. Duk kudin da Julde zai bashi na kashewa da kuma na hidimar makaranta bai cika amfani da su ba. Idan Adee tazo gidan yafi kashe kudin shi, tunda in taga zai fita ba zata rasa cewa ya siyo mata wani abin ba.

Wata yarinya yar asalin garin Kaduna, kabilar Bajju ce ta manne mishi, yana aji biyu tana aji hudu ko a lokacin, ta sha kai tsaye ta fito mishi da asalin abinda take so daga wajen shi, tunda tasan ko hauka take soyayya a tsakanin su ba zata yiwuwa ba, idan nashi addinin ya amince mishi auren mabiyiya wani addinin, ita nata ba zasu amince ba, kuma ga bambanci shekaru a tsakanin su. Shisa itace zabin farko da yake da shi. Harya gama darasin shi karfe shidda na yamma yana jin shi kamar akan allurai, karfe tara na dare suka yi da ita.

A masallacin makaranta yayi sallar isha'i, da suka hada idanuwa da dalibin da yayi musu limancin da sauri ya sauke nashi, saboda ya tsargu, sai yaga kamar yana mai kallon "Nasan abinda kake shirin aikatawa". Tun daga lokacin da suka fita daga cikin makarantar da Victoria ta saka hannunta cikin nashi tana dumtsewa yake jin kuskuren da yake a cikin duk wani taku da zasuyi. Shiya bata kudin da ta kama musu hotel na kwana daya, sai dai suna shiga cikin dakin ta mayar ta rufe yaji ta rufe da wani abu daya bari a wajen dakin.

Bayan sun fito da safe, kowa yayi wajen shi daban yaji canjin da yayiwa gabaki dayan rayuwar shi. Dararen da kuma ranakun da suka biyo bayan wannan daren na biyu daya hadu dana farko wajen yin jagorar canza gabaki daya rayuwar Salim zuwa sukeyi suna wuce mishi da wani irin yanayi da yake kara dishe wani haske da baisan dashi a kirjin shi ba saida ya fara dakushewa. Dan ya fahimci Julde ya fara, sai ya budema kan shi wata irin duniya da bai taba sanin akwaita ba.

Ruwa ya kare a bangaren su, na famfon gidan kuma burtsatse ne ba dadi gare shi ba, shisa ya

shigo bangaren su Julde da fadan su yasa shi tattara komai nashi yabar musu. Da badan karatun jarabawar da yake yi ba sam ba zai shigo ba, zai hakura da ruwan. Duk maganganun da suke fadama juna a cikin kunnuwan shi suke direwa suna karasawa zuciyar shi da yanayin da yake nisantata da son kusantar aure da duk wani rikici da zai biyo bayan shi. Rayuwar hayaniya ce sam ba zai iya ba, aure kuma cike yake da hayaniya, nashi iyayen babban misali ne.

Sai da ya sauke numfashi da yaji karar rufe kofa, tsaya yayi sai da ya sake jin budewa da rufewar kofa a karo na biyu tukunna ya fito daga kitchen din da robar ruwan daya rike kamar ya sato. A hankali yaja kofar gidan bayan ya fita, iska yake shaka yana fitarwa kamar mai son raba huhun shi da iskar daya shaka a cikin gidan. Yau ya kara fahimtar Julde, akwai shirun da yake tattare da dayar rigar dayake sakawa a wajen gidan aure, ba mai tsayi bane shirun, na kankanin lokaci ne, amman shiru ne, shi da baya tare da hayaniyar aure yakan bukaci wannan shirun. Balle kuma Julde, shisa yanzun da yake komawa bangaren su yake kara hango tazarar da take tsakanin shi da kusantar duk wani abu daya danganci aure.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

05

Ya bude zip din jakar shi ya rufe ya kai sau goma sha biyar ko fiye da hakan, da ba sabuwar jaka bace ba shi kan shi yasan zip din da ya samu matsala. Ba tunani yake ya manta wani abu ba, amman jakar tayi mishi kadan, abubuwan da yake son dauka sun girmi wajen da ya rage a cikin jakar. Daya daga cikin misalin abubuwan ya hada da Khalid da yake tsaye ya jingina bayan shi da bangon dakin

"Har yanzun fushi kake mun Hamma? Jirgi zan hau, komai zai iya faruwa..."

Kallon da Khalid ya watsa mishi yana saka sauran maganar koma mishi, sai da ya hadiyi yawu kafin ya sake cewa

"Idan kasan zakayi kewa ta har haka me yasa da Daddy yace mu tafi tare kaqi?"

Numfashi Khalid ya sauke, shi bai taba tunanin barin gida da sunan karatu ba, asalima banda jami'ar Bayero babu wani waje da yake sha'awar zuwa da sunan karatu. Shima fannin ilimin

kimiyya da fasaha ya karanta, baiyi tunani mai tsayi ba da ya tashi neman gurbin karatu wajen cike bangaren magunguna wato Pharmacy a matsayin zabin shi na farko. Duk lokacin da zai ma Nawfal din zancen zabin makaranta sai yayi kokari wajen canza maganar kamar baya son amsawa.

Shisa ya kyale shi, a zaton shi Nawfal na daya daga cikin mutanen da sukan kasa tsaida hankalin su waje daya akan zaben makaranta ko kuma fannin da zasu karanta. Akwai su a ajin su, dan da yawa har suka siyi Jamb suna tararrabin abinda zasu cike, wasu suna da zabi fiye da biyu, wasu kuma basu da ra'ayin kansu ne sai abinda iyaye suka cusa musu tun tasowa. Ya san Nawfal baya daya daga ciki, banda shi baya tunanin wani ya taba tambayar shi abinda yake son zama ko inda yake son yin karatun shi.

Nawfal ya sani, shine mutum na karshe da zaiki goyon bayan shi akan duk wani zabi da zaiyi, in har zabin ba wanda zai cutar da shi bane ba. Zai karya idan yace jin zancen zabin Nawfal din daga wajen Julde bai mishi ciwo ba

"Kasar waje Bajjo yake son tafiya, ko zaka duba makarantar kaga idan akwai abinda kake son karanta sai ku tafi tare, bana son ya tafi shi kadai"

Shine abinda Julden ya fadi da Khalid bai ma bari ya karasa ba ya fara girgiza mishi kai

"Daddy ni bana sha'awar zuwa ko ina, anan zan zauna. Shi Bajjon da ya zabi tafiya Allah ya taimaka, ba yaro bane ba, na tabbata zai iya kula da kan shi"

Amsar da ya ba Julde kenan yana mikewa yabar wajen zuwa bangaren su. A ranar ko da Nawfal yabi bayan shi ya bude baki bai barshi ya furta komai ba

"Kar mu fara maganar nan Nawfal, baka so in sani ba, Daddy bai san baka so in san tsarin da kayi wa rayuwar ka ba shisa ya fadamun, karka damu, in da akayi maganar nan na barta..."

Rubutun shi ya ci gaba da yi duk da a lokacin in zaka saka mishi wuka baisan me yake rubutawa ba, Nawfal ya dade a tsaye kafin ya fita daga dakin. Duk wani shirye-shiryen tafiyar Nawfal din da ake tayi baya saka baki a ciki. Kwanakin dai ne bai kula suna ta gudu tare da su a ciki ba sai yau da tun safe yake jin zazzabi ya rufe mishi jiki ganin Nawfal na ta hada jaka. Zazzabi ne mai hade da dana sani na satikan daya dauka yana fushin da ya ga rashin amfanin shi a yanzun.

"Ban ki fada maka ina son barin kasar ba dan bana son kasan plans dina Hamma, wallahi ba dan bana so ka sani bane ba...na kasa ne saboda zan dinga hango yau, bana son idan na kalle ka in dinga jin ba kasar nan kawai zan bari ba har da kai..."

Iska Nawfal ya furzar ta bakin shi da yake jin kamar idan yaja numfashi maimakon ya wuce inda ya kamata sai iskar ta dawo tana taruwa cikin bakin na shi, ga zufa da yake ji har a bayan

kunnuwan shi da tafukan hannuwan shi

"Kuma kana fada, ba zakayi ni sa da gida ba, ko da sunan aiki ba zaka iya barin gida ba shisa kake mamakin yanda bi da Adee muka iya tafiya makarantar kwana, ban san ya zan fara fada maka batare da na roke ka mu tafi tare ba, Hamma ba zan so kaina da yawa ba, dan Allah kayi hakuri..."

Gyaran murya Khalid yayi dan bai yarda da kanshi yayi magana kai tsaye ba, yanda yaga zuciyar Nawfal shimfide a cikin idanuwan shi, ya kuma ganta a karye, idan ya nuna alamar rauni bai da tabbas kan abinda zai faru

"Me yasa sai wata kasar? Wani garin bai isa ba?"

Dan daga kafadu Nawfal yayi

"Kullum jina nake kamar tsuntsu, ina da fuka-fukai, amman ina tsare cikin keji tun haihuwata, nasan suna da wani amfani tunda an halliceni da su, amman babu sarari a kejin da nake balle in gwada miqe su har in san ya kamata in tashi..."

Sosai Nawfal yake kallon Khalid, kalaman shi yake zabe iya yanda zai iya, yana so koda kowa bai fahimce shi ba Khalid ya fahimta

"Hamma ina numfashi kullum, amman bana jin yana kai mun inda nake so, idan ina tare da Daada nakan ji kokawar da nake da numfashi na ya danyi sauki, idan muna tare da kai ko Adee ma haka, ina bukatar in fita daga kejin da nake ciki ko zanji, banda tabbas amman ina ji a jikina barin kasar zai iya cike ramin da yake tare da ni"

Wannan karin ta baki Khalid yake jan iska yana fitarwa ta hancin shi a hankali, ga idanuwan shi da yake kiftawa da sauri-sauri ko ruwan da yake jin ya taru a cikin su zai koma, babban dan yatsan shi ya kai yana goge gefen idan shi

"Kamar wani abu ya fada mun a ido"

Ya furta a hankali, muryar shi na fitowa a karye

"Ka dauki duk abinda kake bukata kuwa?"

Kai Nawfal ya iya jinjina mishi

"Sai karfe goma naji Daddy na cewa zamu tafi kaika airport"

Kan dai Nawfal ya sake jinjina wa cikin alamar eh. Numfashi mai nauyin gaske Khalid yaja yana fitarwa

"Bari in dawo"

Ya furta yana juyawa ya fice daga dakin hadi da ja ma Nawfal din kofar. Dan dafe kai Nawfal yayi kafin ya sauke hannun nashi yana mayarwa kan tsintsiyar hannun shi dan ya murza agogon shi, ya riga da ya saba in dai tunani yayi mishi yawa idan yaja iska ya cika bakin shi, to zai fitar da ita ne bayan ya dora hannun shi kan agogon ya dan murza shi, shisa baya daure shi gam gam, lokutta da yawa da shi yake alwala, har wanka ma. Sai ya manta cewa yana hannun shi. Duk agogunan shi haka zaka ga basa aiki, sai da Julde ya bashi wani fari, da alama mai tsada ne

"Ruwa baya lalata shi, ga ka da agogo a hannu, sai an tambaye ka lokaci kace ba yayi, yan gayun zamani"

Dariya yayi yana mika ma Julde hannun shi maimakon ya karbi agogon kamar yanda ya miko mishi, da kan shi kuwa Julde ya zagaya agogon yana daura ma Nawfal din. Tun lokacin zai kirga ranakun daya cire agogon daga hannun shi sai jiya da yaje yi wa Daada sallama, dan suna gaisawa yace

"Dan Allah Daada banda kuka, in kikayi kuka zaki sa inji kamar na tafi kenan, bayan da anyi hutu In shaa Allah zan dawo"

Yana kuwa ganin yanda take ta kokawa da hawayen ta har ta raka shi bakin kofa, inda kamar fitar su Madina take jira ta karyo kwana jikin ta sanye da uniform din islamiyya. Hango sun da tayi yasa ta taho da gudu

"Na hanaki wannan gudun Madina, amman ba zaki daina ba"

Daada ta fadi cikin fada, muryarta dauke da kulawa, dariya Madina tayi, dimples din da suke a kuncinta duka biyun suna bayyana, da murmushin ta kalli Nawfal da yayi dariya mai dan siririn sauti, babu yanda za'ayi Madina tayi murmushi a gabanka baka iya mayar mata ba, ko da kuwa baka santa ba. Da take yar karama tayi haske, amman yanzun a hankali asalin kalarta take fitowa tana nuna alamar cewa ita sam bata dauko hasken fatar da su duka suke dashi ba. Ita ce mutum ta biyu daya sani da take murmushi da duka hakoranta a waje, idanuwanta ba su cika girma ba, idan tayi murmushi sai su kankance, kusan ma baka ganin su gabaki daya.

Yanayin fuskarta idan tayi murmushi shine zai sa fara'a ta kwace maka batare da kama sani ba, sai dai ya dauka kankanta a zuri'ar su zata tsaya ne akan Adee, sai ga Madina kuma yanzun da take son ce musu da duk sun adana tsokanar da suke wa Adee sun jira sun ga yanda nata girman zai kasance in yaso sai su kamanta idan ita kadai zasu tattara wa tsokanar ko kuma zasu rabata ne tsakanin ta da Adee.

"Hamma..."

Ta kira kafin lokaci daya murmushin da yake fuskar ta ya bace, baki ta turo

"Da tafiya zakayi ba zaka jira in dawo ba?"

Daada ta kalla

"Ko anan zai kwana?"

Kai Daada ta girgiza mata

"Sallama yazo mana daman, gobe zai tafi makaranta"

Kallon shi Madina tayi

"Baka ce ka gama ba?"

Dan murmushi yayi yana mata bayani cikin yanayin da yake tunanin zata fahimta a shekarun ta, yayi mamakin ganin yanda take kallon shi idanuwanta cike da hawaye, wani abu ya taso yayi mishi tsaye a kirji ganin hawayen ta ido daya ya fara zubowa kafin dayan, yanda zubowar su ta budema yan uwan su hanya, muryar ta dauke da wani yanayi da ya kasa barin kunnuwan shi tace

"Ba zaka dawo ba ko? Shisa baka fada mun ba? Saboda ba zaka dawo ba?"

Kai yake girgiza mata ya juya wajen Daada dan ta taimaka mishi, amman sai yaga tabar wajen da sauri, hakan yasa shi karasawa yana riko hannun Madina da ta fisge ya sake riko shi da sauri, yana ganin yanda take kokarin sake kwacewa

"Waye yace ba zan dawo ba? Makaranta fa, ko wadda na gama baki ga ina dawowa ba?"

Kafada ta makale

"Zaka bar kasar, jirgi fa zaka hau, ba dawowa zakayi ba ni na sani"

Ta karasa tana fashewa da kuka me sauti, baisan yanda zai fara lallashin ta ba, janta yayi yana hadata da jikin shi

"Wallahi zan dawo Madina, kinji na rantse ai"

Shesshekar kukanta duk da babu sauti yana ji ta yanda jikinta ke amsawa, dagota yayi yana rike fuskarta, amman hawayen da takeyi ya hana ta tsaya ta kalle shi

"Ki kalleni mana, Madina, na taba miki karya? Zan dawo, me yasa ba zan dawo ba? Wa nake da shi acan din? Dole zan dawo...kina jina, zan dawo"

Duk da ta saka idanuwan ta cikin nashi yana kallon rashin yarda a cikin su, fuskarta ya saki yana kai hannu ya kwance agogon da yake daure da shi ya kama hannunta ya saka a ciki

"Ga agogo na ki ajiye mun, idan na dawo zan amsa..."

Ganin ta dumtse agogon yasa shi saurin dorawa da

"Mai tsada ne, Daddy ya bani, ki adana mun kar komai ya same shi, idan ya fashe cikin kudin kunshin ki na wajen Daada za'a biyani"

Dan murmushi tayi da yasa shi sauke ajiyar zuciya, hannuwa yasa yana goge mata fuskarta

"Kin girma ba zaki daina kukan nan ba..."

Hannuwan shi ta ture

"Da ka tafi baka yi mun sallama ba ko Hamma..."

Dariya yayi

"Kashe di ne haka Madina? Ni ake ba kashe di yau?"

Wannan karin tare sukayi dariya. Da nauyin zuciya yabar gidan Daada, amman kamar yanda ya fadawa Madina ne, bashi da wani dalili na zama inda zai tafi, bashi da kowa a can, duk wani da yake da kusanci da zuciyar shi yana nan inda zai bari. Jakar shi ya sake budewa yana zira hannu a cikin aljihun da yake daga can gefe ya laluba yana zaro agogon da Adee ta bashi, ita kalar bula ne ta siya, makaranta ma ya same ta dan yayi mata sallama

"Na rasa me zan siya fa, tunda watan nan ya kama nake tunani, kaga inda karshen tunani na ya kaini"

Karba yayi yana dariya

"Kinsan ba sai kin sai mun komai ba"

Harar shi tayi

"Kanina zai bar kasar ace ba abinda na bashi"

Sosai ta bashi dariya, idan wani ya hango su a inda suke zaune zai iya dauka saurayin ta ne

"Kina da son girma Adee"

Kallon shi takeyi

"Kasan har goya ka nayi ko?"

Da murmushi a fuskar Nawfal yace

"Ko da can Adee kafafuwan ki sunyi gajarta su iya dauka ta"

Duka ta kai mishi a kafada yana rike wajen

"Ouchh... Hannun ki yayi kankanta ace yana da zafi haka"

Wani dukan ta sake kai mishi

"Adee... Da zafi fa..."

Ganin ta daga hannu yasa shi mikewa tsaye yana murza inda ta daka, ganin yanda take harar shi yasa shi yin dariya

"Yi hakuri babbar Yayaa"

Itama dariyar tayi ya koma yana zama

"Sai ka cire agogon Daddy kasa nawa"

Noqe kafada yayi

"Me yasa? Zan ajiye naki dai in ta kallo, amman agogon Daddy ai ba zai ciru ba kema kin sani"

Kai Adee ta jinjina

"Laifina ne dana bata baki na, bani agogo na tunda ba zaka sa ba"

Ta karasa tana kama hannun shi daya janye yana saka agogon a aljihu. Da gaske yake a lokacin zai ajiye ne ya dinga daukowa lokaci zuwa lokaci amman ba yanda za'ayi ya cire agogon da Daddy ya daura mishi da hannun shi, bai taba dauka akwai dalilin da zaisa ya cire agogon nan ba sai jiya da Madina ta hargitsa mishi duk wani lissafi da yake tunanin yana tare da shi. Agogon da Adee ta bashi ya daura yana ganin yanda ya amshi farar fatar shi.

*

"Malam sake jakar nan"

Salim ya furta kamar zai kai mishi duka yana fisge jakar daga hannun shi ya wuce, bin shi da kallo kawai Nawfal yayi, bai ma yi tsammanin yana falon a zaune sai da ya fito daga daki, ba dan tafiya zaiyi ba sam ba zai ko kalli inda Salim din yake ba

"Hamma na tafi"

Shine abinda ya furta, sai da ya dan tsorata da yaga Salim din ya mike, yaga duk yanda ake kiran shi dogo sai da ya daga kan shi sannan ya iya ganin fuskar Salim din daya miko hannu da nufin karbar jakar da take hannunshi, shi kuma ya girgiza mishi kai.

"Ba zaka taho ba?"

Salim ya fadi daga bakin kofa yana saka Nawfal din bin bayan shi da sauri. Duk da haka takun Salim daya shine kusan na shi guda uku saboda kafafuwan Salim din, yanzun da Nawfal ya ke bayan shi sai da murmushi ya kwace mishi, randa Khalid yace

"Bajjo kaga kafafuwan Hamma? Ban san me yasa ya ke karantar aikin likitanci ba, kaddarar shi na ga aikin nepa, ba sai ya taka komai zai dinga yanke wayoyi ba"

Dariyar da ta sake kwacewa Nawfal din mai sauti ce dan har sai da Salim ya juyo, sai yayi saurin boye dariyar da yin tari har sau biyu. Duk da haka murmushi bai bace mishi ba har suka karasa wajen motar Daddy da Salim ya zagaya ya bude gidan gaba yana zama da jakar Nawfal din a hannun shi. A bakin motar Nawfal ya tsaya yana dube-dube, ta inda Khalid zai bullo yake nema, da ya kalli hanyar bangaren Saratu sai zuciyar shi ta rage gudun da takeyi a kirjin shi. Kwakwalwar shi ta fara ce mishi ya bude mota ya shiga, amman zuciyar shi sai ta kasa, kamar na umarni tayi wa kafafuwan shi da su fara takawa zuwa bangaren.

Wata murya cikin kan shi tana fada mishi

"Saboda Khalid da Adee, ko ba dan kowa ba dan su biyun"

Da ya shiga ma ya ganta zaune a falo, bayan yayi mata sallamar da ta bishi da kallon "Lafiya? Me ya faru?" a maimakon ta amsa abinda yake fadawa kan shi kenan, saboda Khalid da Adee.

"Nanna zan tafi..."

Ya furta a hankali, kallon shi takeyi zuciyar ta na kara tafasa fiye da yanda takeyi kafin ya shigo. Yau kwana na takwas kenan da Julde baya mata magana saboda shi. Akan tayi magana kan tafiyar shi kasar waje

"Duka cikin yaranka babu wanda kayi tunanin turawa karatu wata kasar? Sai shi? Komai na rayuwar ka akan Nawfal zai kare ne Julde?"

Kai ya daga mata, a karo na farko yana dorawa da

"Akan shi zan kare Saratu, me zai faru? Nace akan Nawfal rayuwata zata kare idan kina da matsala da hakan kofar gida a bude take zaki iya kama gaban ki, ban taba rike ki ba, ban taba hanaki ba, saboda Daada ne ban taba ce miki ki tafi ba, wallahi zaki saukake mun abubuwa da yawa idan kika tafi da kanki"

Maganganun shi sun mata zafi

"Nawfal ya fini kenan?"

Wani irin kallo yake mata

"Da hada kanki kike yi da shi? Ban taba fada miki ya fiki ba? Duk tsayin zaman shi a gidan nan ban taba ce miki ya fiki ba daman?"

Wasu hawaye masu zafin gaske ne suka zubo mata, tsaki kawai Julde yaja ya fita ya barta a tsaye. Maganar duniya babu kalar wadda bata yi mishi ba a kwanakin nan, in da take ma baya kallo. A cikin kwanakin wata irin tsanar Nawfal take ji fiye da wadda take mishi a da.

"Kar ka dawo... Dan Allah idan ka tafi kar ka dawo"

Ta furta tana saka shi tsayar da idanuwan shi a kan ta. Tsanar shi yake gani karara a fuskarta, bai zaci zuciyar shi zatayi mishi zafin da takeyi yanzun ba. Saboda bai taba tsamannin wani abu daga wajen ta ba, ya san ta tsane shi daga ranar farko da kafafuwan shi suka taka cikin gidan ta

"Me yasa?"

Ya tambaya yau a karo na farko yana saka idanuwan shi cikin nata

"Me yasa Nanna? Me nayi miki haka? Me yasa kika tsane ni?"

Tabe baki tayi jin yanda muryar shi ta karye a karshen tambayar kamar shi dinne wanda aka yiwa wani abu, kamar zuwan shi bai kara mata matsaloli ba, kamar ita din bai kamata a tausaya mata ba saboda duka laifin nata ne

"Matsala ka kara mun Nawfal, zuwan ka matsala ya kara mun, shisa bana so ka dawo. In ka tafi karka dawo"

Iskar dai yaja yana cika baki da ita kafin ya fito da ita a hankali, kirjin shi na kara daukar dumi, juyawa yayi yana cin karo da Salim da ya rike mishi kafadu dam, da yake bai tsammaci zaiyi karo da wani abu ba, da Salim din bai rike shi ba baya zaiyi ya fadi, gefe Salim ya janye shi batare da yace komai ba ya nufi hanyar kitchen, shi kuma Nawfal yana ficewa. Tsaye yayi bakin kofa ya sa hannu ya dafe kirjin shi da yake zafi, anan Salim ya fito rike da robar ruwa

"Muna ta jiran ka"

Ya fadi yana wucewa, bin bayan shi Nawfal din yayi har wajen mota. Sai da ya bude baya ya shiga sannan ya ga Khalid a ciki. Zama yayi yana jan kofar ya rufe. Ba zaice ga abinda Daddy yake fada ba dan hankalin shi yayi wani wajen, hannun Khalid da yaji kamar yana saka mishi wani abu a cikin na shi ne ya saka shi kallon hannun na shi yana dago abinda yake ganin kamar wata silver, dubawa yayi, abin hannu ne da ake kira da bracelet a turance, tsuntsu ne ya bude fuffuke a tsakiyar abin hannun, Khalid ya kalla da yaki yarda su hada idanuwa

"Ya zama mukullin kejin ka..."

Khalid ya fadi cikin sanyin murya

"Fly Bajjo, iya inda zaka iya"

Kai kawai Nawfal ya jinjina mishi, su duka babu wanda ya sake cewa komai har suka isa Airport din, ba zama sukayi ba tunda jirgin karfe sha daya na dare zai tashi.

"Kana sauka saika samu ka kira ni, ka dai rubuta lambar wayar ko?"

Cewar Julde da alamu suka nuna baya cikin wata nutsuwa mai yawa, dan murmushin karfin hali Nawfal yayi

"Na haddace fa Daddy, zan kira dana sauka"

Kai Julde ya jinjina, Nawfal din yana mikawa Khalid hannu, shima hannun ya mika mishi yana jan shi bayan ya rike suka rungume juna, Salim da yake tsaye ya dakuna fuskar shi yana furta

"Ewww"

Sakin juna sukayi suna dariya, Nawfal ya juya ya kalli Salim din da yake ta bata fuska har lokacin

"Marin ka zanyi sai ka ga taurari"

Dariya Nawfal yayi

"A gaban nawa zaka marar mun yaro?"

Daddy ya fadi yana murmushi

"Allah ya tsare mana kai Bajjo, dan Allah ka kula da kyau kaji ko?"

Julden ya nanata mishi ya kula idan wani yaji saiya dauka yaron goye ne shi din. Kai kawai ya jinjina yana kallon Khalid da yake bin shi da ido

"Zan kira ku"

Ya furta su duka suna daga mishi kai, kafadar shi yaji Salim ya dafa yana dan tura shi, hakan na sawa ya juya suka dan taka, kafadar shi Salim ya saki yana kamo hannun shi ya saka mishi jakar shi da yake rike da ita a ciki yana hadiye yawu, sosai yake kallon Nawfal din

"Abin da Nanna ta fada..."

Yace yana saka Nawfal ware mishi idanuwa dan ko kadan Salim din bai nuna alamar yaji zantukan da sukayi da Saratu ba

"Kar ka saka su a zuciyar ka, idan nace maka bata nufin abinda ta fada karya zanyi, ka san karya zanyi Bajjo..."

Kai Nawfal yake dagawa

"Nanna ta fada maka maganganu da yawa, baka saka su a ranka ba, wannan ma ka watsar. Dalilin ta na ce maka karka dawo nata ne ita ka dai, karka watsar da kowa saboda ita"

Kokari yake kar yayi kuka tun safiyar yau, ya dauka Khalid ne zai saka shi kuka, hakan bai faru ba. Maganganun Salim ne suke karya mishi zuciya, saboda Salim ba mai yawan magana bane ba, asalima Salim baya shiga rayuwar kowa a gidan shisa bai taba tunanin ya damu da ko Khalid ba balle shi, balle ya kula da wani abu daya danganci rayuwar shi

"Ka yi abinda zaka yi ka dawo, idan zaka zauna ka tabbata ba saboda abinda Nanna ta fada bane ba, saboda kana da naka dalilin ne... Khalid da Adee zasu so ka dawo, ga Daddy ma, ba saina fada maka Daada ba... Ni ma ina so ka dawo saboda in kama ku kuna zagina da Khalid in muku dukan dana dade ina tarawa"

Yanda ya karasa maganar yasa Nawfal yin dariya, duk da hawaye ne cike taf da idanuwan shi, jakar Salim ya sakar mishi yana fadin

"Allah ya tsare ya dawo mana da kai lafiya"

Kai kawai Nawfal ya iya dagawa, idan yayi magana kukan da yake tarbewa ne zai kwace mishi. Takawa yayi kawai yana cigaba da tafiya kafin ya juyo ya hange su tsaye, hannun shi ya daga musu, da Khalid da Daddy ne suka daga mishi hannu suma. Salim kai kawai ya jinjina, baya shiga harkar kowa saboda baya son jin wani abu kusa da zuciyar shi, baya son saka kowa da komai cikin ran shi, duk wani abu daya danganci hayaniya baya so. Yau yayi ma Nawfal magana saboda kunnuwan shi sun sha kwaso mishi maganganun Saratu da take yiwa Nawfal din da baya son ji.

Yanda yaron yake rayuwa da wannan hayaniyar har mamaki yake yi. Fata daya ya tsinci kan shi da bin Nawfal da shi yanzun da suka juya hanya. Allah yasa da jirgin su ya tashi ya bar duk wata hayaniya da take cikin rayuwar shi, tafiyar ta samar mishi da wani shiru a rayuwar shi.

Sai dai abinda Salim bai hango ba shine addu'ar shi da ta karbu
Nawfal ya bar duk wata hayaniya da tafiyar shi
Ya barta tana jiran dawowar shi
Dawowar da idan tayi mishi maraba sautin ta bashi kadai zaiji ta ba
Har su da suke zagaye da shi sai ta taba.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

06

"Karatu ne ya rike ni Daada..."

Shine uzurin farko daya fara kawo mata a cikin shekaru biyu, a kuma karo na farko da taji muryar shi ba sakon gaisuwar shi a bakin Julde ba. Yanda take kwana tana tashi a cikin shekarun Allah ne kawai shaida, sai kuma ita da ta san kalar damuwar da take ciki, tunani babu kalar wanda batayi. Duk idan Julde yace mata

"Munyi waya da Bajjo, yace a gaishe da ke sosai"

Sai ta dauki dakika tana kallon kwayar idanuwan shi ko zata ga karyar da take tunanin yayi mata. Amman saiya fada murmushin shi da cewa

"Kinsan akwai banbanci awa kusan biyar tsakanin mu da su, sanda zai kira zakiga sai wajen

karfe goma da rabi na dare, da na kira kinji muryar shi"

Tun tana yarda harta fara saka kokwanto a cikin ranta, ta san damuwar da Julde yake karanta a fuskarta yasa shi hada mata wayar tafi da gidan ka ta telephone tunda salular ta hannu da ake yayi tace bata so. Sanyin daya ratsa zuciyar ta bayan jin muryar Nawfal sai da ya saukar mata da wata kasala ta ban mamaki.

"Bajjo"

Ta kira kamar ta kasa yarda muryar shi ce take ji cikin kunnenta kamar yana gabanta. Sai ma da yayi dariyar nan tashi sai taji idanuwanta sun cika taf da hawaye, tsoron da take kwana tana tashi da shi ta nema ta rasa.

"Ka dinga kirana kullum ina jin lafiyar ka kaji ko? Shirun nan shine yake daga mun hankali fiye da rashin dawowar ka"

Ya kuma ji maganarta, kullum karfe tara na dare agogon Najeriya yake kiranta, wasu ranakun sukan dauki fiye da mintina talatin suna hira, wasu ranakun kuma gaisawa kawai sukeyi zaice mata yana da ayyuka da yawa da zaiyi.

"Wata rana ki rike mun Madina da hira mana Daada, kar tayi bacci mu gaisa"

Nawfal ya roke ta, sai dai ta amsa shi da to, dan bata san ta inda zata fara mishi bayanin canjin da Madina takeyi da duk rana ba, a yan shekarun yarinyar komai nata da ka'ida takeyi, in ta dawo daga makaranta karfe shidda zata sake share gidan ko da kuwa Daada ta share, tayi sallar Magriba, taci abinci, a tsakanin ne kafin isha'i zatayi nazarin litattafan ta, ko tayi aikin gida idan tana da shi, tana idar da sallar isha'i take kwanciya. Wani kallo duk yanda take son shi baya shiga tsakaninta da baccin da tasan tana bukata. Yan kunshi yanzun har sun gane, in dai ba alhamis da juma'a ba da yamma, in kazo ma ba zaka samu ba.

Sai dai ko lokacin hutu, kallo kuwa ran asabar da lahadi zata zauna tayi da rana haka, karatu dai dakin Madina cike yake da takardu da litattafai, shisa lokacin da ta fara wani irin ciwon idon da bayan kaita asibiti saida suka yi mata gilashin da gashi nan tana ta fama da shi Daada tace

"Kallon takarda, ace mutum idon shi ba zai huta ba, kullum cikin karatu ba dole ido ya lalace ba"

Yanda duk Madina da Julde suka so fahimtar da ita cewa ba karatu bane ba ya ci tura, sai gajiya sukayi suka kyale ta. Har yanzun bata daina mita lokaci zuwa lokaci idan ta ga Madina manne da littafi, takarda ko ta kosai ce suka siyo suka cinye sai Madina ta dauka ta karanta taga meye a ciki. Littafi duk wanda ta rubuta sai Julde ya siyo mata.

"Hamman ki na gaishe ki, yace in rike ki da hira har lokacin kiran shi yayi dan ku gaisa"

Daada ta gwada fadawa Madina da ta saka hannu tana gyara gilashin daya cinye kusan rabin fuskarta kan karan hancin ta tana yin murmushin da baka raba fuskarta da shi sannan tace

"Hamma baya kira da wuri Daada, kice in yana so mu gaisa ya kira kafin lokacin bacci na yayi"

Shima da ta gaya mishi abinda Madina ta ce dariyar yayi yana amsawa da

"Daada komai na a tsare yake, bana son shigar da wani abu cikin lokacin yin wani abin"

Kai kawai ta girgiza, Nawfal yayi mata nisan da bata ganin canjin da yau da gobe take yi wa rayuwar shi, amman iya hakan ta fahimci sun hadu waje daya tare da Madina, sun dauki wata akida ta kayyadaje yanda ranakun su zasu kasance, har suna ganin ba zasu iya canza hakan dan wani ba. A kauye ta tashi, kauyen da karatun addini ma sai da ta shigo binni ta neme shi da kanta, shisa bata shiga cikin irin wannan rayuwar ta su Madina da tafi karfin fahimtar ta, Madina ma da take gabanta da yawan abubuwa sai dai ta bita da addu'ar neman shiriya ko samun sauki, balle Nawfal da yake wata duniyar.

Sallamar da akayi ta katse ma Daada dogon tunanin da take zaune tana yi, sai da ta sauke numfashi sannan ta amsa tana mikewa jin kamar karar sauke wani abu mai nauyi, tana fitowa kuwa Salim ne ya ajiye buhun shinkafa a tsakar gida

"Karka ajiye anan, ka shigo da shi daga ciki"

A hankali ya daga idanuwan shi yana kallon ta, idan wani yana wajen zaice kamar a takure yake, wani ma idan yaga kallon zai dauka shine karo na farko da ya taba ganin Daada, yana kallon ta ne da mamakin dalilin da zaisa tayi mishi magana, kamar ba zai amsa ba yace

"Akwai wasu kayan..."

Cikin muryar shi da take a bude amman yanayin kalaman sun fito ne cikin sanyi da abinda mutane izzar da tasa mutane da yawa suke daukar ya fito tsatson sarauta, ko da Daada tayi niyyar fadin wani abu Salim bai tsaya ba balle yaji, juyawa yayi abin shi, tana bin shi da kallo, shigar kananun kayane, dogayen kafafuwan shi basu sa yaji akwai bukatar ya dinga suturta su ba, wandon da yake jikin shi ruwan madara da kadan ya wuce gwiwa, sai riga da tayi ma Daada kama da ta sanyi kalar ja, mai dogon hannun da yadan tattare yana ja sama, sai hular sanyi daya tura baya rabin gashin shi a waje, ita kuma kala daya da da wandon shi.

Gashin in da yake a bude, yanzun daya dawo dauke da kwalaye biyu da alamu suka nuna na taliya ne, Daada ta kula da a cukurkude gashin yake, yayi wani irin aski da in ka ganshi cikin masallaci mamaki zai kamaka na kasancewar shi musulmi, ko hausa kaji yayi saika juyo ka kalle shi. Daga yanayin kirar jikin shi, tsayin shi har shigar shi bata nuni da cewar ba bahaushe bane shi, bafullatani ne gaba da baya, kuma mabiyi addinin musulunci. A cikin yaran Julde duka daga Adee sai Khalid ne suke zuwa wajen ta akai-akai.

Da dalili ko babu sukan zo harma su kwana, Salim in ba aiko shi akayi ba, ko kuma motar Julde ta samu matsala yasa ya kawo shi, da kan shi bai taba wanko kafa yace yazo ya gaishe da ita ba. Idan zuwan yayi ma gaisuwa ce take hadata da shi, yanda yake magana kamar an shaqe shi an saka shi dole na daya daga cikin dalilin da yasa ko tambayar shi ya sauran yan uwan shi batayi. Tas ya gama shigo da kayan abincin da suka hada harda doya da mai fari da na ja, tukunna ya kalli Daada yana furta

"Ina kwana"

Murmushi tayi

"Lafiya kalau babban dan aike, sannu da kokari, Allah yayi albarka"

Salim ya amsa da

"Kitchen zan shiga da su?"

Maimakon amsa addu'ar da tayi mishi, ya jita, ya kuma amsa a zuciyar shi, maganar duk da zai motsa labban shi yayi ta in yana da halin takaitata zaiyi. Kai Daada ta jinjina mishi tana komawa cikin dakin dan ta bashi hanyar wucewa, haka ya dinga daukar kayan yana kaiwa Kitchen, ya kuma yi mata magana dan ta nuna mishi inda zai saka mata komai, yana karasawa yace

"Gas fa? Daddy yace in dauka a sake filling"

Kofar da zata hadaka da bayan kitchen din inda cylinder din gas din take Daada ta nuna mishi ya wuce ya kwanto, daman ya kare, ko da safen a risho Madina ta soya musu dankali, basa rabuwa da kalanzir a rishon su tunda gas idan ya tashi karewa babu ruwan shi da ka cika tukunya da shinkafar da ta dauko dahuwa.

"Da ka taimaka in kira Madina sai ka kaimun ita kasuwa tayo mana cefane...siyayyar da dan dama kar in saka yawo a kasuwa"

Numfashin Salim ya fitar yana dan daga mata kai a hankali, in ba ita ba, babu mai saka shi wannan aikin. Shi Madinar ma rabon daya saka ta a idon shi harya manta, idan zai fadi gaskiya ya ma manta da ita ne gabaki daya sai yanzun da Daada ta ambace ta, ba zai manta surutun yarinyar da yake hau mishi kai tun tana yar mitsitsiyarta ba. Balle kuma yanzun da yasan ta fara jin tashen yan matanci, yasan waye shi, tun kafin mata su kara nuna mishi shidin wani ne yasan ko da bashi da kudi yana da kyan da suke bi kamar zasu lashe shi. Yanzun ko matan da yake bi yana da mugun zabe, kuma kashe din shi na farko shine

"Bana son surutu, komai zai mun dai-dai idan zamuyi abinda zamuyi mu gama banji muryar ki ba..."

Manyan mata ma, riqaqqu suna rikicewa a kan shi balle yan yaran nan da yake gani yan aji daya a makaranta suna bin shi kullum da

"Yayaa Salim dan Allah zaka duba mun assignment dina"

Har rasa yanda akayi ya zama Yayaa a wajen su yake yi, yakan karba a wajen ya nemi bango ya dora idan na abin rubutawa ne ya rubuta musu, su kadai kuma yake tsayawa har ya danyi wa bayani wasu lokuttan, saboda 'yan yara ne, saboda yana da kanwa shima, zai so in ta nemi wani ya taimaka mata da abinda ya shige mata ta harkar karatu ya taimaka mata din. Balle kuma Madina da ba zai iya kiyasta shekarunta a yanzun ba, ko yace zai iya hasaso matakin karatun ta.

In da yake tsaye anan Daada ta dawo ta same shi

"Ka zo ka zauna kafin ta fito"

Kai ya girgiza saboda baya son cire takalmin da yake kafar shi, in dai zai karasa cikin falon ya zauna dole saiya cire, ba zai taka mata kafet din da yake shimfide kusan cikin dakin da takalma ba, ko da zai shiga kitchen ta gefe-gefe wajen tayal ya dinga bi. Agogon da yake daure a tsintsiyar hannun shi ya dan daga hannun yana kalla. A cikin kan shi yake hango wasu mintina sha biyar zuwa ashirin kafin Madina ta fito, ya tabbata zata tsaya iyayin kwalliyar nan da yake saka shi kwankwasa dakin Adee ya watsa mata zagi in dai tare zasu fita, baya son jira.

"Banga biro bane ba fa, da zan rubuta abubuwan kar in manta, amman na samu fensiri"

Muryar Madina ta fara dukan kunnuwan shi kafin ya sauke idanuwan shi akan ta, wani dan karamin sauti ya kwace daga makoshin shi da yafi alaka da tsantsar mamaki. Yanda ya ganta yanzun ya goge duk wani hoton yarintarta da yake da shi cikin kan shi balle ya nemo ya gwada ya tabbatar da wannan yar mitsitsiyar halittar ta gaban shi itace Madinar da ya sani. Zai dawo da batun kankantar ta da ya gani, shigar jikin ta, shigar ta ita ce abinda yasa sautin kwace mishi. Wando ne jeans da ta lankwashe daga kasan kusan ninki biyu kamar yayi mata yawa, sai takalmi kafa ciki, rigar da take jikinta yana da tabbacin ko shi ya saka zai iya yawo a ciki saboda girmanta, hijabin da ta saka da alamu yar karama ce fara, sai ta dora rigar a sama ta yanda kanta da wuyanta kawai hijabin ta rufe.

Bai san me zai kira rigar jikin Madina da ita ba, kaurinta yayi yawan da bai kamata ace ta sakata a yanayin zafin da akeyi ba, ga dogon hannaye rigar take da shi da ta dan ja baya kamar yanda yayi. Rabon da yaga kalar yellow harya manta, sai yau da ya ganta a riga da takalman da suke kafar Madina. Ji yayi kalar har shigar mishi idanuwa takeyi, gilashin da yake idonta ya kai kuncinta saboda girman shi. Daga inda yake yana hango maikon da fuskar Madina takeyi ga kurajen da suke fuskarta da ake kira da pimples, ita din gabaki dayanta kamar an cirota daga wani shirin fim din kasar ketare aka direta a inda take yanzun.

Murmushine ya bayyana akan fuskar shi da yake jin girman shi na kara fadada da duk dakika, rabon da wani abu ya saka shi nishadi irin yanda ganin Madina ya samar mishi harya manta, ko matan da yake bi da ya ture su daga jikin shi yake jin wani duhu ya rufe shi ruf, nishadin daya samu ya dishe kamar anyi ruwa an dauke. Dariya ce mai sauti ta kubce mishi da Madina ta kalle shi tana yin murmushin ta daya bayyana duka hakoranta, sannan ta dan daga hannunta cikin alamar gaisuwa tana son tuna in da ta san shi, kafin cikin mamaki ta ja gilashinta kamar zata cire shi tana sake gyara mishi zama

"Hamma Salim... Hamma Salim ne ko?"

Ta karasa maganar da alamar tambaya tana kallon Daada da ta jinjina mata kai, itama murmushin takeyi. In dai akan zabin suttura ne na Madina ta hakura. Ba don ita ta wanketa tun jariranta ka ba, haduwa sukayi a hanya zatayi zaton ko mata-maza ce, sai jinsin namijin yayi rinjaye a kanta, ba kwalliya takeyi ba, mai ma kafafuwan ta kawai take shafawa da Daada zata rantse ko tambayar Madina akayi abinda tafi so a jikinta to kafafuwan zata zaba, fuska kuwa in ba muku-mukun sanyi ya shigo ba da sauran jikinta bata damu da shafa musu mai ba,takance fuskarta da kanta take maiko ko bata shafa mai ba.

Yanda bata kaunar hada hanya da duk wani abu daya danganci kyale-kyalen mata yana ba Daada tsoro. Kafafuwan dai sune matsalarta, kullum cikin safa suke, takan ce

"Daada bakya jin iska na shigar miki kafa?"

Ko

"Daada haka zaki fita baki saka safa ba? Kar wani ya taka miki kafa"

Haihuwa ta fara bambanta Madina da sauran mata, yanzun kuma kaf dabi'unta. Bata son kazanta, kamshine abu daya da tafi so a rayuwarta, ko dakinta ka shiga wani kamshi mai sanyi ne zai fara dukan hancin ka. Sai dai tana cikin mutanen da basu damu da su mayar da duk wani abu da zasu dauko a mazaunin shi ba, kayane akan gadon ta a cike, Daada tayi fadan harta gaji. Banda litattafan ta, babu wani abu da yake a kammale cikin dakin, ga wajen ajiye takalmanta, Madina wani kwali ta samu tana zuba su a ciki, kayan wanki ma kwalin ne ta samu, har kwando Daada ta siyo mata, a store ta tsinto ko sati daya ba'ayi ba tsakani

"Kwandon ne kika watsar Madina? Asarar kudi nayi kenan?"

Ta tambaya

"Wallahi duk ya cika mun dakine fa Daada, ba watsarwa nayi ba, ajiyewa nayi idan na sake shirya dakin sai in masa waje"

Kyaleta kawai Daada tayi, tasan babu wajen da zatayi mishi, duk shirgin da yake dakin ta, kwandon ne bata so a ciki, tafi gane ta zuba su cikin kwali, irin Madina kam, Daada bata jin ko an tona a fadin Kano zasu kai su biyu. Da wahala ma idan ba ita kadai bace ba, kullum cikin neman wani abu nata da bata san in da ta ajiye ba take. Safa kuwa ko makaranta zataje da wahala kaga iri daya a kafarta, hankalinta a kwance zata hada bakar safa da ja taci gaba da hidimarta, idan anyi magana zata ce

"Banga yan uwan bafa, kuma a cikin wata jaka na saka"

Tunda dai taji kafarta a rufe shikenan, shisa duka fata da addu'ar ta akan Madina take zagaye da Nawfal. Burin ta mai girma ne, zata kirga lokuttan da ta taba ganin fara'a a fuskar Salim, amman yau ba murmushi bane kawai, har dariya yayi. Ko ba shiga da yanayin Madina ba, ita din takan saka nishadi a tare da duk wanda zata ci karo da shi. Ko bata sanka ba kuka hada ido zatayi maka murmushinta da zai wahala ka kasa mayar mata da shi.

"Muje kafin rana ta bude da yawa"

Madina ta ce tana wucewa da kara fadin

"Daada sai mun dawo"

Bin bayanta Salim yayi yana mamakin yanda take iya sauri da gajerun kafafuwanta, ko

"Allah ya tsare ya dawo da ku lafiya"

Da Daada ta furta bataji ba balle ta amsa, a bakin mota ya sameta a tsaye. Da kadan kanta ya wuce kugun shi, yar dariya ya sake tsintar kan shi dayi yana zagayawa ya sa mukulli ya bude murfin motar ya shiga. Hannu ya mika ya bude mata itama tana shiga ta zauna hadi da jan murfin motar.

"Wacce kasuwar zamu je?"

Salim ya tambaya yana yin baya da motar, dan jim Madina tayi sannan ta amsa shi

"Kasuwar cefane...in da ake saida su nama da kifi"

Kai Salim ya jinjina, ya kan kai Saratu lokaci zuwa lokaci.

"Hamma Khalid yace likita zaka zama ko?"

Kan dai ya sake daga mata, haka kawai saiya tsinci kan shi da son tambayarta

"Ajin ki nawa? Me kike son zama ke?"

Kallon shi tayi yana ganin girman gilashinta ta gefen idon shi

"Aji hudu uku zan shiga hudu yanzun..."

Kamar tasan gilashin yake tunani a ranshi ta kai hannu tana gyara zaman shi, ya kula takan yi hakan ne saboda ta saba, ya zamar mata kamar habit, bata mintina bata kai hannu fuskarta ta gyara zaman gilashin kamar wanda zai fado ba.

"Ina son zama yar jarida"

Kai Salim ya jinjina

"Glasses dinki..."

Ya soma kafin ya karasa ta amsa da

"Blurred vision...bana ganin abubuwa da kyau sai da shi"

Dan kallonta Salim yayi yana maida hankalin shi kan tukin da yakeyi. Baisan me yasa yake son tambayar ta abubuwa haka ba, rayuwar mutane ba abinda ya shafe shi bace ba. Tauna bakin shi yayi ta ciki don ya gujema wata tambayar kafin ta sake kubce mishi. Shirun ne yayi ma Madina yawa, saboda ita mutum ce da Allah ya halitta da tambaya da kuma son hira, ko bakunta bata iya ba, ko mun girmanka tasan kalar hirar da zatayi da kai da ba zaisa zaman ku ya gundure ka ba.

"Baka jin kida kai a motar ka? Hamma Khalid da kida a motar shi, duk idan yazo zamu je waje yana kunna mana"

Cikin sanyin murya Salim ya amsa da

"Bana son hayaniya"

Bayajin ya taba kunna ko da radio din cikin motar ne tunda Daddy ya bashi ita. Ko TV zai kalla da yawan lokutta sautin gabaki daya a kashe yake, sai dai yayita kallon hotunan

"Ko kai ma kana da matsalar kunne ne kamar yanda nake da ta idanu?"

Murmushi Salim yayi

"Nace bana son hayaniya kina ta mun surutu"

Dariya Madina tayi

"Ni bana so idan ba karatu nakeyi ba inji nayi shiru...baya mun dadi"

Bata kuwa yi shirun ba har suka karasa kasuwa, sai dai a karo na farko a rayuwar shi da surutu bai hau mishi kai ba, asalima ko bai amsa ta ba nishadi take saka shi. Bai fita daga mota ba, anan ya jirata, da yake ta iya wahalar da kanta duk abinda ta siyo sai ta dawo ta kawo sannan ta sake komawa. Da ta siyo kifi harda lemon roba na coke ta hado mishi

"Kana ta zama ko? Yanzun zan gama, saura abu guda biyu"

Ta fadi tana mika mishi lemon

"Ka sha wannan, ko kana jin yunwa in samo maka wani abin?"

Yanda take mishi maganar sai ka rantse yaron goye ne ta bari a mota, dariya ta bashi ba kadan ba

"Wannan ma ya isa, nagode"

Ya fadi bayan ya karba. Ya kuma ji dadin lemon, da ta gama zasu koma hira ta dinga mishi tana bashi labarin yanda sukayi da inda tayi siyayyar ta.

"Me yasa baka zuwa? Ka dinga zuwa dan Allah...kaga ni ban sanka ba sosai"

Madina tayi maganar cike da roko tana kallon shi ta cikin gilashin ta, sai ya tsinci kan shi da daga mata kai, murmushin da tayi na saka shi jin wani bakon yanayi

"Dan Allah da gaske? Ko zaka dawo anjima? Miyar kifi zanyi, da dadi wallahi, Daada tace na iya abinci, ko Hamma Khalid ma yana so inyi idan ya zo"

Kai ya girgiza mata

"Makaranta zanje Madina... Zan dawo ba yau ba dai"

Cike da fahimta tace

"To shikenan, Allah ya baka sa'a, Allah ya tsare ka ya taimake ka"

Addu'ar ta fito mata a saukake

"Amin"

Ya furta yana tsintar kan shi da dorawa da

"Nagode"

Kai ta jinjina tana mishi murmushi, tsaye tayi a kofar gidan kamar tana jiran ta ga tafiyar shi tukunna, shisa yaja motar, ta mudubin shi yake hango tana daga mishi hannuwan ta duka biyun, murmushi yayi, a hankali ya furta

"Madina..."

Batare da ya san girman rawar da madaukakiyar sunan zata taka a rayuwar shi ba.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

07

Sake gyara zaman shi yayi a cikin mota a karo na ba adadi, bacci yake ji ba dan kadan ba, saboda bai samu wadatacce ba da dare. Da ace babu hayaniya lafiya kalau zaiyi baccin shi. Tunda motar a kashe take dole ya sauke gilashin kadan dan shige da ficen iska. Amman hakan sai kwaso mishi surutan da baya bukata zuwa kunnuwan shi yakeyi. Harda yara da a lokacin ya kamata ace suna islamiyya amman sun cika unguwa da hayaniya sun hana kowa sakat. Inda unguwar su Daada yake yana da tabbacin da anyi gangami an tashe su ko da gidan nasu ne sai an sa sun siyar sun tashi.

Yaran da zai jera ya zane ma jiki ya kirga sun fi goma sha daya cikin kan shi daga parking din motar shi zuwa yanzun. Baya son hayaniya, baya son surutu gabaki daya, iya zaman da yayi ya gama tsara kalar unguwar da yake son siyan gida in har ya samu wadatar hakan. Kwankwasa gilashin motar yaji anyi ta gefen da yake, bude idanuwan shi yayi yana yatsina fuska saboda kamar cikin kwakwalwar shi aka kwankwasa haka yaji. Juyawa yayi yana sauke idanuwan shi kan fuskar Madina da take mai dariya da duka hakoran ta a bude

"Hamma..."

Ta fadi cike da fara'a tana saka shi kai hannu ya kara sauke gilashin motar kasa

"Yaushe ka zo?"

Ta tambaya tana dorawa da

"Me yasa baka shiga cikin gida ba?"

Ya san kafin ya amsa tambayoyin biyu in dai Madina ce ta kara jero mishi wasu, shisa yayi shiru yana jiran ta gama. A cikin watanni biyu baya jin akwai wata halayya ta Madina da bai sani ba, don tana cikin mutanen nan da ake ma rayuwar su lakabi da budadden littafi, ba su da wahalar fahimta. Haka kawai idan gari ya waye a tsayin rana bai ganta ba bayajin dadi, tunda ya san makarantar da take wasu lokuttan yakan dai-daici lokacin tashin su sai yaje. Ba zai manta ranar farko daya fara zuwa ba, yana tsaye ya jingina da motar shi ya hango ta.

Duk yaran da suka fito zaka gansu su biyu har fiye da hakan ma, Madina ita kadai ya hango, ba gilashin fuskarta yasa ya fara gane ta ba, uniform din jikinta da yake tunanin zai wahala bai iya shigar da jikin shi cikin kafar wandonta daya ba, bai taba ganin wando irin na jikin Madina ba, har rigarta tasha bamban da ta sauran, hijabinta ce kawai bata ma kai ta wasu tsayi ba, idan iska me karfi akeyi zata iya yawo a samanta saboda girman kayan da suke jikinta, tana hango shi ta washe mishi baki tana kara saurin tafiyar ta, sanda ta karaso kasa rike dariyar shi yayi

"Madina..."

Ya iya kira, bata san dalilin dariyar shi ba ta fara taya shi

"Wanne irin kaya ne wannan?"

Dan juyawa tayi har lokacin dariya takeyi

"Bana so inji kaya sun matseni"

Kallon ta Salim yakeyi, komai nata daban yake, ba zai kirga yawan matan da ya sani ba, amman ko mai shigen muryar Madina bai taba cin karo da ita ba. Bambanci da take da shi da sauran mutane ne abinda yaja shi. Ko yanzun da take mishi murmushi da dukkan hakoranta a waje bambanci yake sake gani

"Yau baki dawo da wuri ba..."

Ya soma a gajiye, kafin ya karasa ta katse shi

"A'a mun tashi fa, ai kullum-kullum karfe biyar da rabi ake tashin mu, akwai wa'anda suke zuwa daga unguwa mai nisa, ni ce na tsaya na siya awara, akwai layi kuma. Ban san ka zo ba da na taho"

Numfashi Salim ya sauke yana nuna mata alama da hannun shi da ta zagaya ta shigo motar.

Sai da ya dakuna fuska dan karta fadi a gudun da tayi tana bude murfin motar, ledar awarar da sai lokacin ya ganta ta ajiye akan kujerar motar tana fadin

"Bari in kai jakata ciki in fada ma Daada na dawo kar ta dauka na tsaya wani waje"

Bata ma jira amsar shi ba, ko murfin motar bata rufe mishi ba ta juya. Numfashin dai ya sake saukewa da murmushi a fuskar shi. Hannun ta da ta dauke ledar awarar ya fara gani dan yanda ta shigo motar kamar an jehota sai da ya sake yin dariya, duk idan yana tare da Madina sai ya dinga jin tamkar yana biyan bashin duka lokuttan daya kamata ace wani abu ya saka shi nishadi bai ji nishadin ba, da wahala kaga fuskar shi babu murmushi duk idan suna tare, ko ita din ya gani kafin ta bude bakinta ta ce wani abu shigar jikinta ta bashi dariya.

"Ga ruwa na dauko maka"

Ta fadi tana sauke numfashi hadi da mika mishi ledar ruwan da ya karba ba dan yana jin kishi ba, ya siyi ruwa har roba biyu a hanya, tsintar kan shi yayi da fasa ledar ya dan sha ruwan yana rike ledar a hannun shi

"Daada tace tana gaishe ka"

Kai ya jinjina mata yana kallo tana bude ledar awarar da tayi mishi kyau a ido, harda albasa da kabeji yankakku a ciki sai yaji kulle a farar leda ta bude tana ajiyewa daga gefe a cikin ledar awarar.

"Ka iya cin awara? Ka san awara?"

Yar dariya yayi mai sauti

"Lallai yarinyar nan..."

Cewar Salim yana sata yin dariya

"Nasan unguwar ku ta yan gayu ce, ba masu sai da awara shisa"

Tayi maganar da dukkan gaskiyar ta, tana daukar awara daya ta saka cikin bakinta.

"Adee tana mana a gida ai"

Tauna awararta Madina takeyi tana mika mishi ledar da ya saka yatsu ya dauki guda daya ya dangwala yajin ya saka a bakin shi

"Hamma Nawfal baya son yaji shi"

Maganar ta kwace mata batare da tasan dalilin da yasa tayi ba, numfashi Salim ya sauke, Nawfal din da ta kira na saka shi jin wani yanayi da bai da fassarar shi. Wani irin shiru ne ya ratsa cikin motar saboda. Ita kanta Madina ji takeyi kamar anyi wasu shekaru ne masu yawan gaske da tafiyar Nawfal din, ba zata ce tunanin shi baya fado mata ba, ko agogon shi da yake ajiye akan gadon ta yana tuna mata shi, da tana sakawa, sai ta cire ta ajiye, ko karatu takeyi wani lokacin zaka ganshi a hannunta tana ta jujjuya shi. Idan zatayi bacci ma lokutta da yawa agogon na hannunta ko da ba tunanin Nawfal takeyi ba ta riga da ta saba dauka.

Daina saka agogon ya zama hanyar ta guda daya ta nuna fushin ta da karya alkawarin shi da Nawfal yayi na cewar shekara daya kawai zaiyi ya dawo. Amman yanzun kam anya akwai wannan fushin?

"Kullum kike siyan awarar?"

Salim ya tambaya saboda yau ne karo na farko da shiru yayi mishi yawa, baisan ko dan in dai tana waje ya saba da hayaniyar ta bane ba

"Um um fa, ni kadai nake ci. Daada wai mai yayi yawa yana saka mata heart burn"

Shima kwara hudu yaci ya kara shan ruwan da yake hannun shi. Yana kallo ta kulle sauran da alama itama ta isheta

"Zan tafi, yanzun za'a kira sallah"

Salim yayi maganar yana mika hannun shi bayan motar ya dauko wata bakar leda yana dorawa akan jikinta

"Komai kika ce kina karantawa, bana karanta duk wani abu da bai shafi karatuna ba, sune suka mun kyau a ido"

Bude ledar Madina tayi tana lekawa, sai da ta gyara zaman gilashinta sannan ta kalle shi da wani yanayi a fuskarta da ya saka zuciyar shi daukar dumi, idan litatttafai zasu bayyana wannan yanayin a fuskarta duk zuwan da zaiyi zai kawo mata ko dan ya gani

"Nagode Hamma, kasan duk na karanta na dakina, maimaita wasu nakeyi. Daddy yace zai kawo mun amman bai zo ba jiya... Nagode sosai sosai"

Murmushi kawai ya iya mata yana kallo ta sa hannu ta zaro littafi daya tana shafa shi a gefen fuskarta kamar akwai wani abu a tare da littafin da ita kadai ce take gani, dayan hannunta ta sa tana bude murfin motar ta fita, harta kai kofar gida ta dawo tana daukar ledar awarar ta hadi da fadin

"Sai anjima...Allah ya tsare maka hanya"

Bata jira amsar shi ba ta sake juyawa, murfin motar ma sai shi ya rufe abin shi, hankalinta gabaki daya yayi kan litattafan. Da murmushi a fuskar shi ya kunna motar da yayi dai-dai da kiran sallar Magriba da akayi. Yana hanya ana tayi a masallatan da yake wucewa, banda sallar asuba da itama dan Khalid na tashin shi baya kowacce sallah a cikin jam'i. Baisan lokacin da hakan ya fara ba, rana daya ya wayi gari za'a kira sallah yana kwance bai mike ba duk da wani duhu da yake ji yana karuwa a zuciyar shi. Wata rana yana aji haka zaiga mutane na fita dan gabatar da sallar su, ko ya fita yana komawa mota ya zauna har sai an idar.

Sai ya hada azahar da la'asar yayi su a lokaci daya. Ko yanzun daya karasa gida ya ajiye motar shi ya nufi bangaren su ya bude ya shiga a falo ya zauna yana sauke numfashin gajiya, saida ya huta ya mike ya shiga kitchen tunda Adee tana nan yasan abincin shi an kawo ba sai yaje ya zubo ba. Ai kam an kawo din, shinkafa da wake da miyar kifi. Daga Magriba har isha'i sai karfe tara na dare ya hada yayi su, ya sake yin wanka yana shirya jikin shi cikin kananun kayan da sukai matukar karbar shi sannan ya sake ficewa daga gidan.

*

Adee da take tsaye a gaban shi ta daga kai cikin alamun son ganin fuskar shi sosai yake kallo

"Dan Allah Hamma, kaji, dan Allah ka danyi fara'a idan zaku gaisa, a tsorace yake wallahi"

Murmushin da zuwa yanzun zaice Madina tafi kowa gani yayi mata

"Good...gara da yake a tsorace"

Kallon shi Adee tayi kamar zatayi kuka. Sau wajen hudu Salim din yana wuce ta tare da Ahmad, cikon na biyar ne tana komawa ta ganshi zaune a falon Nanna, sai da zuciyarta ta buga

"Waye shi? Ban taba haduwa da yan ajin ku fiye da sau biyu a cikin wata daya ba"

Bawai bata so ta fada musu bane ba, ta rasa ta inda zata fara tun satin daya fita da Ahmad din ya matsa mata da yana son ya gaisa da Julde, ko kuma tayi magana da shi a saka musu rana yana son ko gaisuwa ce azo ayi, shine namiji babba a gidan su, kuma kamar yanda Hajiyar shi take cewa babu wani abu da yake jira yayi aure sai lokaci, yana da muhalli, dan kasuwa ne da yake harkokin shi a tsakanin Dubai da kuma nan Kano, suna da shaguna a cikin kantin kwari, inda yake mallakin shine, bai kuma boye mata matakin karatun shi daya tsaya a diploma ba tunda gabaki daya harkar karuwanci ce abinda suka saka a gaba. Diploma din ma yayine kawai dan ra'ayin dan samun karatun boko da abokin shi ya kwadaita mishi.

Da ta fadawa Nanna ta samu Julde da maganar saiya wakilta Salim da yayi bincike kafin a sati dayan da ya sakama su Ahmad na turo manyan shi. A tsorace Adee take dan har ranta tana son Ahmad, irin soyayyar da bata hango kanta a ciki ba, yana da duk wata nagarta da cikar

halittar da kowacce mace zata yaba da ita. Sai dai a irin bincike na aure haka ake binciko halayen mutum da wasu kan toshe kunnuwan su tare da rufe idanuwa wajen kin yarda, sai binciken yayi hannun riga da halayen da kai aka nuna maka.

Ga Salim din yace mata

"Ina son magana da Ahmad, ki kira mun shi"

Batare da yayi mata wani karin bayani ba, tsoron ta shiya kara tsorata Ahmad din. Da yazo din ma ya kirata ya sanar da ita yazo tana jin yanda muryar shi take rawa

"Tunda azahar nake addu'a Adee, idan Yayan ki yace ban mishi ba fa? Ya zan da tarin soyayyar da nake miki?"

Kasa bashi wani kwarin gwiwa tayi saboda itama a tsoracen take. Dariya Salim yake sonyi amman ya danne yana kama hannunta ya janyeta gefe yana fita. Kaf unguwar su Ahmad harma kasuwar su daya shiga babu mutum daya bayar da shaidar banza akan Ahmad, asalima tarin nagarta da alkhairin shi suke fadi. Idan Salim ya kalli Fadila baya ganin shekarunta, yar kanwar shi yake gani, yar mitsitsiyar yarinyar da zaiyi komai dan kareta daga duk wata hatsaniya ta duniya. Dan baya hango aure a cikin jerin abubuwan da yake da niyyar yi a rayuwar shi baya nufin baya son yaga wani yayi.

Musamman kanwar shi da duk idan yaga wani da namiji a kusa da ita sai zuciyar shi tayi tsalle zuwa wuyan shi. Tsallen da bai taba hana shi bin kannen wasu ba, zuwa yanzun ya daina jin girman laifukan shi, baya hango kowa sai nishadin da zai samu na dan kankanin lokaci. Ya dai ji dadi har kasan ran shi da yaga zata nutsu waje daya, ya sake jin dadin samun Ahmad da nagartar da bashi da ita. Har hamdala ya tsinci kan shi dayi da jarabtar su ba zata taba Adee ba don ita dinma mutuniyar kirki ce. Ko yanda suka gaisa da Ahmad yasan a tsorace yake

"Idan nace in ka ci amanarta Allah zai kamaka kamar ina fada maka abinda ka sani ne. Ga kanwata na Ahmad, dani zaka fara haduwa idan hawaye ya zuba daga idanuwanta saboda kai"

Kai Ahmad ya jinjina mishi yana hadiye wani abu da yayi mishi tsaye a wuya. Murmushin da Salim din yayi mishi ma kara tsorata shi yayi, idan yana tsaye da Adee sai ya ganshi babba, amman yanzun a gaban Salim saiya raina girman shi.

"Allah ya tabbatar muku da alkhairi"

Salim ya sake fadi yana mika ma Ahmad din hannu cikin alamar sallama sannan ya nufi bangaren su. Itama Adee data fito bata wani dade ba saboda tasan Julde na gab da dawowa. Ai kam ko mintina goma batayi ba tsakani ya dawo

"Daddy..."

Ta furta cikin sigar sannu da zuwa tana mikewa dan ta karbi ledojin da suke hannun shi

"Adee, sannu da kokari"

Cewar Julde yana mika mata ledojin dai-dai shigowar Khalid

"Daddy sannu da zuwa, yanzun naji motar ka"

Hararar shi Adee tayi

"Shisa ka shigo kenan...to sai ka juya ai tunda ka mishi sannu, bai kawo tsarabar komai ba"

Dariya Khalid yayi yana shiga cikin dakin sosai hadi da kaima daya daga cikin ledojin da tayi saurin janyewa wawura

"Daddy..."

Adee ta kira

"A'a kunga yanzun na dawo ko? Kaina ba zaiyi ciwo ba tunda kamar kaji haka kuke"

Julde yayi maganar yana raba su ya wuce, a gajiye yake jin shi sosai. Dakin su ya wuce yana samun Saratu a kwance, tun daren jiya da tace tana son magana da shi yasa kai ya fice bai saurareta ba take shan kamshi har yau da safe ma da zai fita. Bata gaban shine, in dai zai dawo ya samu daya daga cikin yaran shi to hankalin shi ya gama kwanciya, wucewa yayi ya watsa ruwa ya fito yana neman wani yadi marar nauyi ya saka a jikin shi

"Tun jiya nace maka ina so zamuyi magana kaqi saurarena"

Alamar ciwon kai da yake ji ya sashi zama gefen gadon wajen kafafuwanta da ta tashi zaune ta mike akan gadon

"Ina jinki"

Ya furta

"Akan maganar auren Adee ne, idan suka bukaci ganin dangin mahaifinta fa?"

Wani irin tsalle zuciyar shi tayi har saida kirjin shi ya amsa. Badan ya shafe wani abu dangi daga babin rayuwar shi ba, a'a, bukatar su a cikar neman aure ne ya manta, wani abu da yake neman taso mishi ya danne

"Zan san yanda zanyi"

Ya furta yana mikewa, bin shi da kallo saratu tayi

"Julde kana ganin komai zai tafi dai-dai? Kana ganin laifukanka ba zasu taba yaran mu ba?"

Iskar da ya shaka dakyar ta wuce mishi yana fito da ita a wahalce, baisan me yasa take son hautsina mishi duniyar daya dauki lokaci yana dai-daitawa ba, amman daya kalleta babu komai akan fuskarta sai tarin damuwa, damuwar da tunda zancen auren Adee ya taso ta danne mata zuciya. Akwai sirrikan su da auren nan zai iya bankadowa, abinda tafi tsoron fitowar shi fiye da laifukan Julde da zai iya taba musu yara.

"Nace miki zan san yanda zanyi"

Ya maimaita yanajin yanda muryar shi take rawa. Kafin tace wani abu ya fice daga dakin, duk surutan da su Adee sukeyi iya kunnuwan shi yake tsayawa, baya kaiwa kwakwalar shi balle ya fahimta, abincin ci kawai yake badan yana gane dandanon shi ba, har Adee saida ta taba shi

"Lafiya dai ko Daddy? Fuskarka kamar babu jini"

Dan murmushin karfin hali yayi mata

"Kaina ke ciwo ga shi akwai gajiya a tare da ni"

Sannu sukayi mishi dukkan su, Adee ta tashi ta dauko paracetamol ta balli guda biyu ta bashi, karba yayi ya sha badan zai mishi maganin matsalar shi da ta girmi duk wata kwayar magani ta bature ba, sai dan damuwar da yake gani a fuskokin yaran, har yayi musu sai da safe suna bin shi da sannu. Daki ya koma, Saratu na inda ya barta, zagayawa yayi yahau gadon ya kwanta yana juya mata baya. Har alamun zazzabi saida yaji ya rufe shi. Yau fiye da kowanne lokaci yake jin kewar Mero, yana da yakinin ba zata rasa kalaman da zata fada mishi da zai kwantar mishi da hankali ba, ko jinta a kusa dashi da kamshin nan nata ya isa yasa hankalin shi ya kwanta.

Lumshe idanuwan shi yayi ko da hoton ta ne ya gani a zuciyar shi, amman sai hoton yazo mishi tare da kalamanta

"Yanda kayi mun rami a zuciya, in Allah ya yarda duk lokacin da kake tunanin hankalin ka ya kwanta sai Allah ya aiko abinda zai birkita maka komai Julde..."

Babu shiri ya bude idanuwan shi. Zuciyar shi na ciwon daya dauka lokaci ya saba masa da radadin shi. Mero ce mutum ta biyu da take da muhimmanci a rayuwar shi da ta jefe shi da kalamai masu zafi irin haka, rashin sa'ar shi mai girma ne, batun yanzun ya san haka ba, shisa tunda ya samu su Salim kacokan duk wata addu'a da zaiyi, duk ma wani aikin kirki da zaiyi da

niyyar Allah kar yasa rashin sa'ar da yazo duniya da shi karya taba su. Tambayar Saratu ta tokare mishi kahon zuciya.

Anya laifukan shi ba zasu taba yaran su ba?

Tambaya ce mai nauyin da shi kadai yasan shi, laifuka tace, laifukan shi idan zaiyi waiwaye masu yawan gaske ne, ko daya daga ciki za'a dauka ya isa ya tsaida duk wani jin dadi da yake gani a fuskokin yaran shi. Har Saratu ta mike ta kashe musu fitilar dakin bai ko motsa ba, wani irin tsoro ne yake ratsa dukkan sassan jikin shi, kome zai same shi in dai zai tsallake su Adee mai sauki ne. Bacci a daren ranar barawo ne ya sace shi cike da mafarkin rayuwar da zaiyi komai dan ganin ya shafe babinta.

Sai dai wasu shafukan na kaddara suna da zumunci, ko baka waiwaye su ba sai sun sake kawo maka ziyara.
©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

08

A cikin kunnen shi aka bude kofar dakin duk da baccin da yake mai nauyi ne, kuma da alamu a hankali aka so budewa. Tunda satin bikin Adee ya kama baya samun wadataccen bacci, baisan me akeyi a harabar gidan ba, amman yana jin kai kawon mutanen da ba zaice duk daga ina Nannar su ta samo su ba. In har suna da wasu dangi da suka hada jini dasu a garin Kano daga Daada sai Madina ya sani. Ko da wasa bai taba jin daga Daddy har Nanna sunyi zancen wani dangin su bayan Daada ba. Bai san ko su Khalid ba, amman shi bai taba tambaya ba, ya yarda cewar idan akwai dangin daya kamata su sani za'a nuna musu su.

A ranshi dai yaga kamar wata uku da aka saka bikin Adee yayi kusa, amman Julde na da halin da zaiyi mata komai, watakila shisa basu jashi da nisa ba. Watannin ma sauri sukayi mishi matuka. Yau dai ya daya rage saura kwanaki biyu daurin aure, ya hada yar jakar shi, zai kama hotel ne har sai an gama hidimar bikin gabaki daya kafin hayaniya ta haukata shi. Karar haduwar takalmi da tayals din dakin kamar sukuwar doki ta sa shi jan wani dogon tsaki

"Ubanka kakeyi da baka wuce ba har yanzun Khalid?"

Salim ya fadi yana jin kanshi kamar ba zai bude ba, kamar ma jan kafa Khalid din ya sakeyi

saboda ya mayar dashi sa'an shi, bude idanuwan shi yayi yana sauke su cikin na Nawfal daya kwashe da dariya

"Bajjo"

Salim ya fadi cike da kashedin da bai boye murnar shi ba. Ya dauka Khalid ne, ko da wasa baiyi tsammanin zuwan Nawfal din ba

"Normal mutane ko basu rugo sun tarbeni ba zasu tashi zaune daga kwanciyar su suyi mun sannu da zuwa"

Cewar Nawfal yana murmushi

"Da dariya a muryar su"

Juyawa Salim yayi, yafi son kwanciya akan kujera fiye da yanda yake son kwanciya akan gado. Bai kuma san dalili ba, amman in har yana gida da rana kuma ko da daddare ma zaka gan shi kwance a falo kan kujera

"Hamma..."

Nawfal ya kira da karfi yana saka Salim jin kamar ya saka lasifika ne

"Kayi na bakunta Bajjo...karka kara"

Dariya Nawfal din yayi, tunda ya hau jirgi yake jin shi sama-sama, daya sauka airport ya samu taxi zuwa gida zuciyar shi dokawa takeyi ba kadan ba. Kan shi tsaye bangaren su ya wuce, ranar da aka sa ranar Adee ta kira shi, su tsakar dare ne ma

"Bacci kake ko? Ban tsaya kirga awanni ba yau, sai da naji muryarka na tuna tsakar dare ne"

Tashi zaune yayi, banda Adee a gabaki daya rayuwar shi babu wanda yake kiran shi a lokacin da baya daga waya ya dauka, ko da Daddy ne, kusan zaice saboda Adee ne baya saka wayar shi a silent in ba yana cikin aji ba. Shima daya fito yaga kiranta yake bin bayan shi

"Kace zaka zo bikina Bajjo, idan ba zan takura ka da yawa ba"

Shine rokon da tayi mishi

"Zan zo Adee, In shaa Allah zan zo"

Duk da ba saboda bikinta kawai yazo ba, bikin natane ya karfafa dayan dalilin na shi. Filon kujera da yaji an jefe shi da shi yasa shi rike bayan kan shi

"Kofato ne a kafarka wai?"

Dariya Nawfal yayi, da gaske ya dawo gida. Sai ma daya tura kofar dakin su yana jin kamshin turarukan Khalid sun daki hancin shi, kafin ya hade tunanin shi waje daya yaji Salim ya watsa mishi zagi. Da gangan da yazo tura kofar ya buga ta, mukulli yabi da shi kar Salim din ya same shi cikin dakin, jakar shi ya fara saukewa yana jan karamin akwatin shi ya ajiye gefe daya. Sai da ya shiga wanka ya fito sannan ya bude dakin, akwatin shi ya janyo ya dauki wata farar riga da wani wando fari iya gwiwa ya saka. Shima baccin ne a idon shi saboda jikin shi ya saba da bambanci lokaci. Kwanciya yayi abin shi.

Cikin bacci yaji kamar ana jijjiga shi, inda yake jin hannun ya kama ya ture yana juya kwanciya

"Bajjo... Bajjo... Dalla ka tashi"

Khalid ya fadi muryar shi cike da farin ciki yana sake jijjiga Nawfal din daya daga idanuwan shi dakyar

"Ka barni inyi bacci Hamma..."

Ya furta yana shirin gyara kwanciya Khalid din yana kai hannu ya janye filon da kan Nawfal yake kai

"Tashi zakayi muyi labari"

Wani irin numfashi Nawfal ya sauke

"Kayi missing dina na sani, amman ina nan, ba yau zan tafi ba ko wani abu, ka kyaleni inyi bacci na"

Baki Khalid ya bude zai magana Nawfal ya tashi zaune da sauri yana katse shi da

"Kana da kati a wayar ka? Ara mun..."

Fuskar Khalid dauke da alamun mamaki ya zaro wayar shi kirar Nokia yana mika ma Nawfal din da ya karba yana mika hannu ya dauko tashi wayar, kallon shi Khalid yakeyi yana danne-danne da alamar sako yake turawa. Yana gamawa ya mika ma Khalid wayar

"Nagode"

Yayi maganar hamma na kwace mishi saboda baccin da yake idon shi

"Ka kwanta, zan fita ne nima, Nanna ta aikeni"

Da wani yanayi a fuskar Nawfal yace

"Shine ka tashe ni?"

Dariya kawai Khalid yayi ya mike yana ficewa daga dakin. Kasa komawa baccin yayi, kamar cikin shi jira kawai yakeyi ya farka ya cigaba da tunasar da shi yunwar da yake dawainiya da ita da ta saka shi mikewa zaune babu shiri yana saukowa daga kan gadon gabaki daya. Rigar jikin shi ya kalla, duk ta yamutse saboda baccin da yayi da ita a jikin shi, cire ta yake kokarin yi yaji ana kwankwasa dakin

"Come in"

Ya furta yana karasa cire rigar dai-dai lokacin da Salim ya turo kofar yana runtse idon shi

"Ewwwww, Bajjo"

Dariya Nawfal yayi dan yanda Salim din yayi wani zaiyi zaton babu kayane a jikin shi gabaki daya

"Ka sa kaya, idanuwa na"

Cewar Salim da har lokacin idanuwan nashi suke a runtse, rigar daya cire ya mayar a jikin shi yana dariya, a hankali Salim ya dan bude idon shi daya kafin ya bude su gabaki daya yana mika ma Nawfal ledar da sai lokacin ya kula da tana hannun shi, karba yayi cike da mamaki

"Kifi da dankali na siyo... Bakomai kake ci ba, akwai kayan tea a kitchen"

Kai kawai Nawfal ya iya jinjinawa saboda wani abu da yaji ya mishi tsaye a zuciya

"Idan baka ci...."

Da sauri Nawfal yake girgiza mishi kai

"Zanci, ina ci... Miyetti"

Kallon shi kawai Salim yayi, kafin kaji fulatanci a bakin shi zaka dade, Julde yana musu, Nanna ma lokutta da dama shisa duk suke ji, amman kana iya ma Nawfal magana ya mayar maka da hausa.

"Kar inji motsin ka"

Hannu Nawfal ya daga yana ma Salim din alamar salute hadi da jinjina kan shi. Sai da ya fice

daga dakin sannan ya samu waje nan kasa kan kafet ya zauna ya bude ledar. Harda ice cream har roba biyu, wani irin numfashi ya sauke

"Allah ya biya maka bukatunka Hamma"

Ya furta a hankali saboda har ranshi yaji dadin ice cream din fiye ma da kifi da dankalin. Shi ya fara sha tukunna ya ci sauran, yana cikin shan dayar robar Khalid ya shigo da sallamar da kafin ya amsa ya mika mishi wayar shi

"An maka text"

Karba Nawfal yayi da sauri yana duba wayar yaga Khalid bai bude text din ba, sai da ya dan sake kallon shi yaga waje ya samu ya zauna yana jan ledar da take gaban Nawfal din da kifin da ko rabi bai ci ba, sake mayar da hankalin shi yayi kan wayar yana karanta text din, replying yayi yana ajiye wayar da kamar haka take jira ta fara ruri, kamar ba zai daga ba, Khalid yake kallo da yake cin kifin shi hankali a kwance, daukar wayar yayi yana daga kiran hadi da karawa a kunnen shi, numfashin da bai san yana rike da shi ba ya sauke

"Jaan..."

Ya kira cikin wani irin sauke murya da yasa Khalid daga kai ya kalle shi fuskar shi dauke da alamar tambaya

"Wanne zan fara amsawa yanzun? Bakomai fa, na danyi bacci ne"

Ya amsa kafin yayi jim yana sake fadin

"Um um, ina zaune, naci abinci, muna tare da Hamma Khalid"

Murmushi yayi yana mika ma Khalid din waya

"Ana son magana da kai"

Yanayin fuskar Khalid din na saka shi yin yar dariya, karbar wayar Khalid yayi ya kara a kunnen shi hadi da yin sallama

"Kullum sai naji labarin ka"

Aka furta daga dayan bangaren bayan amsa sallamar shi, cikin wata murya mai sanyin gaske, idanuwan Khalid na kan Nawfal yace

"Abin mamaki ganin yanda ni banji naki labarin ba"

Zunguri Nawfal ya kai mishi

"Hamma"

Ya kira a hankali, kafadu Khalid ya dan daga, yarinyar da har lokacin bai san sunanta ba tayi dariya mai sanyin sauti kamar muryar ta

"Sunana Murjanatu. Yar asalin Nigeria, garin Adamawa, an haifeni a New York, I'm your brother's girlfriend"

Ta karasa maganar cikin harshen turanci, yanayin yanda ta ajiye kowacce kalma na sake tabbatar wa da Khalid din da gasken tashin turai ce, sai dai kalamanta na karshe sun saka shi rasa abinda zai fada ko abinda ya kamata ya fada, har Nawfal ya miko hannu ya zare wayar daga kunnen shi bai ce komai ba

"Hello..."

Nawfal yace yana dorawa da

"Ina da tambayoyi da tarin bayanai da zanyi, muyi magana anjima?"

Kai ya jinjina yana sauke wayar daga kunnen shi yana kallon Khalid

"Ban tabbatar ba shisa ban fada maka ba, da na tabbatar kuma bansan ta inda zan fara ba... Kawai ya faru ne"

Numfashi Khalid yaja yana fitarwa a hankali, soyayya abune da yake hange da nisan gaske a rayuwar shi, duka shekarar shi ta uku yake a jami'a, yana son tsayawa da kafafuwan shi, tsayuwar da idan wata ta jingina da shi ba zasu fadi ba su dukan su.

"Kace wani abu dan Allah"

Nawfal ya fadi yana kallon Khalid din, Murjanatu ce abu na farko da yaji baya bukatar amincewar kowa a kai, amman yana son goyon bayan Khalid, ko yaya ne yana son Khalid ya kara mishi karfin gwiwa

"Ban san me zance ba ne ba"

Khalid ya furta cikin sanyin murya yana dorawa da

"Da gaske na rasa abinda zance, na san abune da zai faru wata rana, amman yanzun baiyi sauri ba?"

Kafadu Nawfal ya dan daga mishi cikin rashin tabbas, mutane na tsoron abubuwa mabanbanta, kananu da manya, duka biyun ne suka hade mishi waje daya, babban tsoron shi bai wuce kasancewa shi kadai a filin duniyar shi duk kuwa da rashin girman ta, yana da su ya sani, amman ba zai kira su nashi shi kadai ba, Nanna ta sha jaddada mishi ita da duka ahalinta ba nashi bane ba, rabasun da takeyi da shi ba zabinta bane ba, dole akayi mata. Yana son ya samu wani abu da zai kira nashi.

"Nawfal..."

Khalid ya kira yana saka shi sauke numfashi

"Ban sani ba Hamma, watakila yayi sauri, kawai ya faru ne..."

Baki Khalid ya bude zaiyi magana aka kwankwasa dakin

"Waye? Shigo?"

Cewar Khalid bayan an sake kwankwasa dakin a karo na biyu

"Nanna tace ka fita da motar ta a duba za'ayi abu da ita yau"

Kai Khalid ya jinjina

"Ka karbo mun mukullin..."

Sanin halin Lukman ya sa shi mikewa ya bude kofar yana kiran Lukman da har ya kusa kofar da zata fitar dashi daga bangaren nasu

"Yanzun fa, ka dawo yanzun ka kawo mun"

Juyawa kawai Lukman yayi cikin sanyin yanayin shi da baisa tafiyar shi ta kasance ta malalata ba. Yana da kazarniya sosai, kawai hayaniya ce bayayi, dan ta Lukman duniyar bata tashi ba, babu wanda zaice ya taba ganin ran yaron a bace, ko a ranakun da babu makaranta ba kullum kake ganin shi ba. Komawa cikin dakin yayi, kallon ledar kifin da yake ci yayi cikin wani yanayi da yasa Nawfal fadin

"Ka sa a fridge mana, in ka dawo sai kaci a nutse..."

Dan jim Khalid yayi

"Bafa harshen kowa bane irin naka...zaiyi sanyi, bari dai in kai Kitchen kawai. Muyi magana idan na dawo?"

Ya karasa yana tsugunna ya tattara ledar kifin

"Ni ma zanje wajen Daada, na so inga Adee, naga kaman akwai mutane da yawa a bangaren"

Kai Khalid yake girgiza mishi tunda ya kira sunan Adee din

"Bata gidan ma, ni na kaisu wajen gyaran gashi ne ko meye ita da kawayenta tun dazun, tace in sun gama zata kira ni...ka shirya, bari in bi Lukman in karbo mukullin sai in sauke ka"

Khalid ya fadi yana fita daga dakin da ledar kifin shi a hannu. Shima tashi yayi yana hada duk wani abu da yake son tafiya da shi gidan Daada din a jakar shi ta goyo, dan sai da Khalid ya dan jira shi da ya dawo, ko rigar da yaso ya sake bai samu ya saken ba suka fita.

**

Daga bakin titi Khalid ya sauke shi saboda motar nata ririkewa, da kafafuwan shi ya taka ya karasa shiga, yana hango gidan yana jin zuciyar shi na tsalle har cikin tafukan kafafuwan shi, dan duk wani taku da zaiyi sai ya kara gudun zuciyar shi. Bai san yayi kewar Daada har haka ba sai da ya taka soron gidan yaji tsalle-tsalle da zuciyar shi takeyi, rabon da ya ji shi kamar yaro dan shekara uku da yake dokin ganin wani nashi haka harya manta. Kamar ya karasa da gudu ya shiga cikin gidan haka yake jin shi

"Daada...Daada Am..."

Shine abinda ya iya furtawa a madadin sallama, sunan na fitowa daga wani lungu na zuciyar shi inda yake jin kewar Daada kamar yasa ihu

"Daada..."

Ya kara kira yana jin kafafuwan shi sun gaji, kamar dakin nata ya kara nisa. Daada da take daki a zaune, hankalinta yana kan labaran da take kallo a talabijin dinta ta jiyo muryar shi a kiran farko da yayi mata, kira na biyu ne yanayin yanda ya furta "Daada Am" din ya saka taji kamar ruhinta ne yake shirin kubcewa daga gangar jikinta saboda yanda muryar ta dake ta

"Bukar..."

Ta furta da wani irin yanayi mai wahalar fassarawa tana dafa kujera ta mike dakyar, kira na ukku ne ya mayar da ita ya zaunar tana wani irin maida numfashi, zuciya kenan, babu abinda ya kaita wahala a kaf halitta ta tsarin jikin dan adam, da bata yaudare su haka ba. Kafin tunanin ta ya tsawaita Nawfal ya karasa bakin kofar inda yayi tsaye kamar yana son daukar sababbin hotunanta ne cikin kan shi ya adana a kusa da tsofaffin da yake da su

"Daada..."

Ya sake kira cike da tsantsar kaunar ta, ya manta yanda ita kadai take saka shi yaji abinda yake ji haka, yanda matsayinta ba zai taba haduwa da na kowa ba a wajen shi

"Bajjo"

Ita ma ta kira shi, sai dai nata idanuwan ba kaunar jikan nata bane da kewar shi kawai, harda hawaye taf a cikin su da wani yanayi a shimfide da ita kadai zata iya fassara shi. Ko takalma bai cire ba ya karasa cikin dakin, itama mikewa tayi yana samunta a tsaye, batare da tunanin komai ba ya zagaya hannuwan shi yana riketa a jikin shi

"Ina kaunar ki Daada, ban taba fada miki ba ko? Yau dai na fada, nayi kewar ki da yawa... Ba kadan ba fa, da yawa sosai har bansan ya zanyi in fada ba"

Dariya tayi, hawayenta na samun damar zubowa, yayi girma saboda ba zaka kirata gajera kai tsaye ba, amman kanta da kadan ya karasa kirjin Nawfal din, sake riketa yayi kamar zai cike gurbin kewarta da yayi na shekaru biyu

"Kashin tsufa Bajjo, karka karyani"

Dariya sukayi a tare yana sakinta dakyar, dan har lokacin wata irin kewarta yakeyi kamar bata tsaye a gaban shi

"Ina Madina?"

Ya tambaya yana kallon cikin dakin da bai canza mishi ba sam

"Tana dakin ta da littafi, in dai da littafi a hannun ta bata ji bata gani"

Dariya ya sake yi yana zame jakar shi daga kafada ya ajiye akan kujera, sai lokacin kuma ya kula da takalman da suke kafar shi, dan murza goshin shi yayi, yana rankwafawa ya zare takalman ya dauke su ya mayar bakin kofa, da hannu ya nuna inda yake tunanin dakin Madina ne cikin alamar neman tabbaci, kai Daada ta daga mishi, kai tsaye ya nufi bakin kofar yana kwankwasawa, jin shiru ya saka shi sake Kwankwasawa da karfin wannan karin, yanda ya kasa kunnen shi yasa shi jin takun tafiyar ta, shekaru biyu kamar wasa.

Zuciyar shi bata doka ba sai da yaga ta murza kofar alamun budewa zatayi, idan yace yanayin da yake ciki yana da fassara zaiyi karya. Numfashin shi ne ya dan tsaya na dakika kafin yaja iskar da itama baiji inda ta tafi ba bayan Madina ta bude kofar, wandone a jikinta ta nannade shi har kusan gwiwarta, sai rigar sanyi marar nauyi, mai hade da hula da ake kira da hoodie a turance, dogon hannu ne shima ta ja shi kadan, hular nada zaren da ta kama ta kulle shi dan hular ta zauna mata a kai sosai, sai gilashin ta da ya rufe rabin fuskarta.

Ko ya hasaso yanda Madina ta koma a shekaru biyu rak yanzun daya ganta tsaye a gaban shi komai ya goge, su duka kallon juna suke, ita tana mamakin yanda akayi ta gan shi a kofar dakinta, karatu take na wani littafin kimiyya da Salim ya siyo mata, da highlighter a hannunta tana shaida a duk wajajen da take da tarin tambayoyin da idan yazo zata tsare shi ya amsa mata taji an kwankwasa dakin, zaton ta Daada ce zata tambayeta wani abin da ta ajiye ta rasa inda ta kai shi. A nisantaccen mafarki bata hango kasancewar Nawfal cikin gidan ba, shisa ganin shi ya zama kamar an kwada mata guduma a tsakiyar fuska.

"Madina"

Ya kira, muryar shi na dira cikin kunnuwan ta, tana nan yanda take, muryar shi, sam bata canza ba duk da ta dade bata jita ba, shi dinma banda tsayi bata jin ya canza

"Madina..."

Ya sake kira ganin kamar ta kasa yarda shi dinne a tsaye, dariya yayi mai sauti yana kai hannun shi ya taba goshin ta da tayi kokarin karewa tana murmushi

"Kin canza"

Ya furta saboda ya kasa rikewa a cikin shi, ta canza ba kadan ba, wani irin canji da bai taba tunani ba

"Hamma... Da gaske kaine?"

Tace tana kasa daina murmushi, kai Nawfal ya daga mata shima ya kasa daina murmushi, ganin yana kara takowa cikin kokarin hade space din da yake tsakanin su yasa ta daga hannun ta tana matsawa, kai take girgiza mishi, duka alamu sun nuna rungumarta yake sonyi, shi din dan uwanta ne, duk da na rana daya Daada bata taba mata bayanin dangantar da take tsakanin su ba. Ta san shi din baya cikin jerin mazan da suka halarta su rungumeta, tana zuwa islamiyya, tana kuma iya kokarin ta na ganin bata tsallake wasu layuka da zasu iya wasa da lahirarta ba.

Babban abinda take tsoro bai wuce kwanciyar kabari ba, lahira na ba Madina tsoro fiye da zaton mai zato, ko mutuwa taji anyi duk yinin ranar bata da sukuni, musamman idan a cikin unguwar sune, sai ta kasa cire tunanin yanda mala'ikan mutuwa ya kasance unguwa daya da ita, amman ba wajenta yazo ba, tuni dai yayi mata na zuwan shi babu sanarwa.

"Madina..."

Nawfal ya kira wannan karin yana jan sunan nata, dariya tayi, mamaki yake ba kadan ba, har tayi girma haka, girman da take kokarin jan layi a tsakanin su. Hango ranar daya bar kasar yakeyi, yanda dakyar ya bambare Madina daga jikin shi, dakyar ma ta bar shi ya tafi, amman

yanzun har tayi girman da take ganin ta wuce ya rungumeta, shekaru biyu suna da nisa ne har haka? Yayi tambayar cikin kan shi yana neman amsa duk a waje daya.

"Fito to... Nayi kewar ki"

Dariya tayi sosai

"Ni ma haka, baka kira sai nayi bacci"

Kallon ta yayi

"Ke kuma ba zaki jira ni ba"

Dariyar dai ta sake yi, har lokacin ta kasa yarda shine a gabanta, wani irin yanayi take ji har jikinta na daukar dumi saboda murna. Tare suka jera zuwa falon, sam ya kasa daina kallon ta, sosai ta canza mishi kamar ba Madinar da ya sani ba, dariyar ta ce kawai bata canza ba, har yanzun idan tayi dariya duka idanuwanta sai sun rufe, sai su kansu idanuwan, basu kara girma ba. Kallon ta kawai na saka shi jin lallai yazo gida. Wani numfashi da baisan yana rike da shi ba ya sauke bayan ya zauna

"Daada baki ce mun zai zo ba"

Kallon shi Daada tayi

"Nima ban san zai zo ba Madina, yanda kika gan shi haka nagan shi"

Kai Madina ta jinjina tana murmushi

"In kawo maka ruwa?"

Ta tambaya saboda ta ma rasa abinda ya kamata tayi, kai Nawfal ya daga mata badon yana jin kishin ruwa ba, shima zuciyar shi ta cika taf da farin ciki. Yana son ganin Adee da Daddy, amman anya kuwa zai iya barin gidan Daada a yau? So yake ya kwana suna labari, in sun gaji suyi shiru su zauna tare da juna kawai, wannan yanayin na yau yana son ya adana shi a wajaje fiye da zuciyar shi yanda in ya tafi zai dinga ziyartar wajajen suna saka shi nishadi. Ruwan kuwa ta kawo mishi a kofi ya karba

"Abinci fa?"

Kai ya girgiza mata yana saka dayan hannun shi ya bubbuga gefen shi kan kujera

"Ki zauna muyi labari... Nayi kewar ku da yawa..."

Zaman kuwa tayi, Daada na bin su da kallo zuciyar ta cike da farin cikin, tsoron da take kwana da shi tana tashi yana barinta da ganin Nawfal din. Idanuwanta ne kawai akan su, tunaninta yayi nisa, ba zatace ga abinda suke fada ba, amman dariya sukeyi, sosai dariya suke kamar basu da wata damuwa a fadin duniya

Haka take son ganin su
Tare da juna
Cikin farin ciki
Haka take fatan rayuwar su ta kasance
Sai dai kaddara ta riga fata.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

09

"Adee..."

Nawfal ya furta bayan sun shigo dakin ita da Khalid suna gaisawa da Daada,wata irin kewar ta na tsirga mishi, dariyar da takeyi bai hanata hararar shi ba

"Bawani nan..."

Murmushi yakeyi yana mika mata hannun shi daga inda yake zaune, karasawa tayi ta kama tana zama gefen shi kafin ta zare hannun nata tana daka mishi duka.

"Ouchhh... Adeee"

Ya fadi yana murza wajen dan yaji zafi sosai

"Ka zo ba zaka iya kirana ba Nawfal, ba sai kazo inda nake ba in ganka..."

Har lokacin murza wajen yakeyi

"Saboda ke fa na zo, yanzun nake so in kira inji ko kin dawo..."

Tabe baki Adee tayi, Nawfal na gyara zaman shi kan kujerar yanda zai fuskance ta, fuskarta fayau take babu kwalliya, amman sai yaga har wani kyalli-kyalli takeyi mishi

"Kinyi kyau sosai"

Murmushi tayi, kowa haka yake ce mata tun bayan sati daya da fara mata gyaran jikin da bata san nawa Nanna ta kashe a kai ba. Kuma itama tana jin santsin da fatarta tayi, daman fuskarta tunda can babu kurji ko daya, tana dai gani a fuskokin mutane, ita wannan zumuncin ne bai taba tsallakowa kanta ba.

"Nagode"

Ta fadi, kai ya jinjina mata yana sata girgiza mishi nata, ita ba dan yace tayi kyau take mishi godiya ba

"Ina nufin nagode da kazo..."

Wani sauti Khalid ya fito dashi daga kasan makoshin shi yana dorawa da

"Karku fara dan Allah..."

Cikin yanayin da yasa su yin dariya

"Daada ina Madina?"

Cewar Adee

"Sallah ta shiga daki tayi. Na san yanzun zaki ga ta fito"

Ai kam Daada na rufe bakinta Madina tana fitowa daga daki

"Adda..."

Ta kira tana karasowa ta zauna daga gefen Adee

"Hamma ina wuni"

Ta gaishe da Khalid da yake daddana wayar shi

"Lafiya kalau Madina... Kwana biyu"

Kallon shi tayi

"Ina cewa Hamma ya gaishe ka fa"

Shima nashi idon ya raba da waya yana kallon ta cike da alamar tambaya

"Wanne Hamman?"

Murmushi tayi

"Hamma Salim, ko shekaranjiya na ce ya gaishe ka, kullum ma idan mun hadu ina cewa ta gaishe ka"

Wannan karin Adee ta kama Madina tana juyo da ita dan su fuskanci juna

"Hamma Salim naji kince Madina... Hamman mu... Salim na mu wanda duka muka sani?"

Yanayin da yake fuskokin su ne ya ba Madina dariya, yi suke kamar abune da ko a mafarki basu hango zai faru ba, kai ta jinjina

"Hamma Salim kike gani? Kina magana da shi, shima yayi magana da ke?"

Kai ta sake jinjina ma Adee, Khalid da ya ajiye wayar shi kan hannun kujera fuskar shi dauke da tsantsar mamaki yace

"Ya sunan bokon ki Madina?"

Har Daada sai da tayi dariya

"Da gaske nakeyi... Tafdin... Hamma fa... Bajjo kana jin ikon Allah"

Kai Nawfal ya jinjina musu, dan shi ya gama nashi mamakin tun kafin su zo

"Har daga makaranta yana dauko ta ya dawo da ita gida wasu ranakun..."

Sai da yaga hankulan Adee da Khalid sun koma kan shi tukunna ya dora da

"Suna labari da juna har suzo gida... More like Madina tana labari da shi kuma bai taba sauke ta a hanya ba"

Baki Adee ta rike

"Ashe zanyi tsahon ran da zan ga ranar nan... Madina anya ke mutum ce?"

Dariya suke bata sosai ma

"Yanzun idan ya shigo fa?"

Daada ta fadi tana saka wani shiru ya ratsa dakin, Khalid na daukar wayar shi daya ajiye, Nawfal ya koma cikin kujera ya zauna. Adee ma gyara nata zaman tayi tana kallon Madina

"Maganar kunshin, gobe idan Allah ya kaimu ne fa..."

Kai Madina ta jinjina mata

"Ban manta ba, wajen karfa tara In shaa Allah zan taho sai in fara ma wanda suke nan kafin sauran su zo..."

Ganin sabuwar hira zasu dasa yasa Daada cewa

"Abinci fa?"

Adee ta fara amsawa

"Ni dai ina ci, sau daya naci abinci duk yau wallahi, cikina sai kullewa yake tun dazun"

Abincin kuwa Madina ta tashi ta zuba musu banda Nawfal da ya shiga kitchen din da kan shi yana dafa ruwan zafi ya hada shayi, kankara ya dauka a fridge ya fasa ya zuba cikin kofin yana karasa cika shi taf ya dauko ya fito. Banda Daada babu wanda yayi mishi magana tunda duk ba bakon abu bane a wajen su. Musamman Khalid da ba zaice ga rana daya da yaga Nawfal yasha shayi mai zafi ba. Sam baya so, suna nan suna hira Julde ya shigo ya same su, shima abincin aka zubo mishi suna dasa sabuwar hira kamar lokacin gari ya waye musu ba dare bane ba.

Shikam Julde hankalin shi yana kan Adee da su Khalid suka saka a gaba da tsokana. Haka yake son ganin su kullum, yaran shi, farin cikin shi. Yanda maganar auren ta ya tafar mishi batare da wata matsala ba abune da zai jima yana nutsar da shi duk idan ya tuna. Akan ce mutane na daya daga cikin Rahmar da Allah zai maka, bai kara yarda ba sai akan bikin nan na Adee, yanda abokan arziki suka mishi tsaye ta yanda wani dan uwa na shi bai taba mishi ba tunda yake. Daga tambayar auren har daurin shi da ya wakilta abokin shi ya kuma karba. Tabbas yaga halaccin mutane, a tare da dangin mijin Adee kuma yaga wautar mutane ta yarda da wani kamar yanda suka yarda da shi.

Dan shi bai basu wannan yardar ba, kaunar da yake ma Adee tasa sai da yayi cikakken bincike a kan su kafin ya amince. Ba zai dauki yar shi ya kai inda wata matsala zata biyo baya ba. Sauran maza ne, yana da tabbacin babu wani abu da zai taba su da zasu kasa dauka. Adee ce yake son karewa da dukkan kumajin shi. Kuma hankalin shi ya kwanta da kalar mijin da zata aura.

"Karfe goma da wani abu, in dai ba anan zaku kwana ba ya kamata ace kun tashi kun kama hanyar gida yanzun"

Julde ya fadi yana kallon agogo, sake shigewa cikin kujera Nawfal yayi yana dauke idon shi daga cikin na Khalid da yake kallon shi

"Da gaske Bajjo?"

Adee ta fadi bayan ta mike

"Gobe da safe zan taho, sai mu taho da Madina..."

Yace yana kin hada ido da su, su yake son gani daman, kuma ya gan su, ko da can kalar baccin da yakeyi a gidan Daada ya sha bamban da na ko ina, bacci yake batare da tunanin komai ba. Yana son ko da na yau ne kawai kar ya hadu da Nanna.

"Muje Khalid, Allah ya kaimu goben. Daddy sai da safe"

Adee ta fadi tana kallon su Daada

"Daada sai Allah ya kaimu... Madina ina jiran ki"

Kanta da yayi mata nauyi Madina ta jinjina, bacci takeji ba dan kadan ba, ba zata tuna ranar karshe da tayi wannan daren ba. Julde ma mikewa yayi

"Nima ai tafiyar zanyi"

Dan tunda aka fara hidimar bikin ya tattara ya koma hotel da zama, har fada sukayi da Saratu kan hakan

"Daman kofa kake nema, in ba haka ba ko bangaren su Khalid ai zaka iya komawa"

Shine abinda ta fadi da ko amsa bata samu ba, saboda ba sai da biki ba, idan yaga dama zai iya kwanakin shi a hotel tunda ba zamanta yakeyi ba. Sai da Nawfal yaga Julde ya mike tukunna ya raba nashi jikin da kujera, tare duk suka fita, Daada iya bakin kofar daki ta raka su, Nawfal ne ya fita har kofar gida. Sai da su Khalid suka fara sannan Julde ya kalli Nawfal

"Menene? Me kake son fada mun?"

Da mamaki Nawfal yake kallon shi, murmushi Julde yayi

"Na sanka Bajjo, kana ta kallo na da na shigo, na san akwai abinda kake son fada mun..."

Murmushi Nawfal yayi, shisa a duniyar shi gabaki daya babu kamar su, sune kawai suke kula da kananun abubuwa haka a tare da shi

"Zai iya jira Daddy, abinda nake so in fada maka din... Zai jira sai an gama hidimar Adee..."

Numfashi Julde ya sauke

"Ka tabbata?"

Ya tambaya a idanuwan Nawfal din yaga ko wacce irin magana ce ba ta rashin dadi bace ba, babu damuwa ko daya a tattare da yaron na shi

"Daddy... Allah da gaske"

Murmushin dai Julde ya karayi

"To shikenan. Ka koma ciki, sai da safe"

Kiyawa Nawfal yayi, sai da yaga tafiyar Julden tukunna ya koma yana mayar da kofar gidan ya kulle hadi sa sauke wani numfashi da baisan yana rike da shi ba. Kamar yanda ya fada ne, tashi maganar zata iya jira har a gama bikin Adee.

*

A tsaye ta fito ta same shi, ya mika mata hannu ya karbi jakar da take rike da ita, batayi musu ba ta mika mishi tana rugawa ta shiga kitchen, numfashi kawai Nawfal ya sauke, ya kai minti talatin yana jiranta, sai yanzun ya gane me yasa Daada tace mishi

"In dai Madina ce da ka samu waje ka zauna..."

Ko Salim ya kai minti sha biyar yana tsaye kofar gida, dan da tace ma Nawfal shi zai zo ya dauketa bai yarda ba har sai da yaga zuwan na shi, ita take kara bata lokaci shi gaban shi yake faduwa saboda Salim ne, Salim ne a waje yana jiran su. Zai fara tsayawa a cikin soron gidan Daada, idan yaji Salim din baiyi fada ba saiya fita, dan bai shirya a sauke mishi hayaniya da sanyin safiya ba. Ba zaice ga abinda ta kara tsayawa yi ba, amman a tsakanin kitchen da kuma dakinta sai da ta kara bata kusan mintina goma. Sannan ta sake komawa kitchen tana dauko wata karamar roba mai murfi ta fito.

Kai kawai Nawfal ya girgiza yana sata yin dariya

"Daada... Mun wuce"

Ta furta saboda Daada ta koma daki, daga can tayi musu Allah ya tsare tana fada musu su ja mata gidan idan sun fita. Daga baya Nawfal ya tsaya dan ya hango Salim ya jingina kanshi da kujerar motar da alamar ya gaji da jira, yana kallo Madina ta bude gaban motar, sai da yaji gaban shi ya fadi, musamman da Salim din ya dago yana kallon ta a kasalance.

"Oh goodness"

Nawfal yace yana matsawa baya, jira kawai yake yaji Salim din ya fara fada, amman ga mamakin shi zama ya gyara yana tashin motar, juyowa Madina tayi

"Hamma ka taho"

Kai ya daga mata yana takawa, kafin tayi wani motsi ya bude bayan motar ya shiga yana mayar da murfin ya rufe, dan babu wanda zai saka shi zama gaban motar Salim, yana kallo Madinar ta shiga ta zauna ta rufo kofar. Sai da Salim ya fita da motar tukunna ta fara korar shirun da fadin

"Doya da kwai na soya, ga naka na dibo maka..."

Dan kallon ta Salim yayi yana mayar da hankalin shi kan tukin da yake yi

"Shisa kika bata mun lokaci?"

Kai ta girgiza tana dariya

"A'a Allah, inata sauri fa, ko Hamma?"

Ta karasa maganar tana dan juyawa ta kalli Nawfal da ya sadda kan shi kasa, wannan labarin ba dashi za'ayi ba. Baya son ta fara tsoma shi ciki. Baisan me yake faruwa ba ko yanda akayi ta sa bakin Salim ya bude, ko yanda maganar ta bata mishi hayaniya cikin kunnuwa, amman shi yasan yana bude idon shi zaice yana ihu. Hirar Madina ta cigaba da yiwa Salim da yake amsata dai-dai. Suna karasawa cikin gida Nawfal na budewa ya fice daga cikin motar, yana sane da ko gaisawa basuyi da Salim ba, amman Salim ne in zaku hadu ka wuce ya wuce yafi mai wata gaisuwa da zakayi mishi.

Madina ma bai mata sallama ba ya wuce abin shi. Murfin motar ta kama da nufin fita itama Salim yace

"Ina zaki?"

Kallon shi Madina tayi

"Su Adda na ta jira na nasan"

Dan daga kafadun shi yayi

"Nima na jira ki ai, ina doyar?"

Inda ta ajiye ta dauko robar tana mika mishi

"Allah suna ta jira, karfe tara nace musu...na san zan kai dare kilan ban gama ba, zan ara wayar Adda in kiraka idan na gama"

Ta karasa maganar tana bude murfin motar ta fice kafin ma yace wani abu, baya ta sake budewa ta dauki jakarta da Nawfal yabar mata. Sannan ta wuce cikin gidan, numfashi Salim ya sauke yana juyawa ya ga har ta bace ma ganin shi, yanda gajerun kafafuwanta suke da sauri har mamaki yake bashi. Haka kawai yaji ganin tan da yayi ya mishi kadan, ko hirarta baiji da kyau ba. Sake kunna motar yayi yaja ta yana kara ficewa daga gidan dan ba zai zauna ba, hayaniyar tayi yawa. Gara yaje ya samu wani hotel din ya kira wata ko zata taya shi ya rabu da yanayin kewar Madina da ya dabaibaye shi.

Ita kuwa cikin gidan ta wuce, tana shiga cikin falon da sallama, Saratu ta fara gani da ta amsa sallamar da fara'a a fuskarta. Ko a cikin yaran idan taji ana cewa Salim baya son mutane abin baya bata mamaki, itama din ba wai mutane sun dameta bane ba, kafin jinin ku ya hadu akwai aiki. Idan wani ya ce mata me yasa take son Madina zata karyata, amman yarinyar ta shiga ranta tun ba yanzun ba, bata san me yasa bata zuwa gidan ba, lokaci zuwa lokaci tunanin ta yakan fado mata. Banda su Salim babu wani da zataji alkhairi zai shiga tsakanin shi da Julde da zataji ranta bai mata bakikirin ba sai Madina.

Tana kaunar yarinyar, irin kaunar nan da bata da dalili. Share muryar da taji a cikin kanta tana tambayar ta

"Anya kuwa? Kin tabbata babu wani dalili? Kaunar da kike mata bata da alaka da Yelwa?"

Tana kokarin dishe sautin muryar da yiwa Madina magana

"Madina ana ganin ki daman? Adee ta jawo mana ke ko?"

Dariya Madina tayi

"Nanna... Makaranta fa. Ina kwana... Ya hidima?"

Murmushin ta Saratu ta kara fadadawa, duk da yanayin muryar Madina din na son daukar tunanin ta zuwa abubuwan da ta zabi ta adana

"Alhamdulillah...suna ciki suna jiran ki, amman da kin fara cin wani abu, an kawo waina yanzun nan"

Kai Madina take girgizawa

"Sai dai anjima Nanna, doya naci wallahi"

Dan har bayan wuyanta take jin ruwan shayi na taso mata, wani irin koshi tayi na ban mamaki

"To shikenan..."

Har Madina ta wuce ta dan juyo

"Daada tace a gaishe ki"

Fara'arta dake fuskar Saratu sai da ta dan ragu, kai ta jinjina kafin dakyar ta iya cewa

"Tana lafiya?"

Da murmushi Madina ta amsata tana juyawa, karancin shekarun ta bai hanata fahimtar babu wani shiri mai karfi tsakanin Daada din da Saratu ba, kawai wasu tambayoyin bata san ta inda zata fara su ba, wasu tambayoyin tsoron amsar su na sakata sake adana su a cikin kanta. Amman kam tana da tarin tambayoyi, masu yawan gaske

"Sai yanzun? Karfe tara fa mukayi dake"

Muryar Adee ta katse mata tunaninta

"Afuwan Adda, inata hidima ne ashe lokaci yana tafiya"

Cewar Madina tana ajiye jakar hannunta a kasa dan duka kayan lallen suna ciki, tsugunnawa tayi ta kwance takalman da suke kafarta da sam sai lokacin ta tuna bata cire su ba. Kafin ta dago har Adee ta daukar mata jakar

"Ki kawo Adda"

Harararta Adee tayi

"Ni dai muje, ki dauko takalmin ki kafin a dinga bi takan shi ana wucewa"

Juyawa kuwa tayi tana daukar takalman nata ta rike su a hannu tabi bayan Adee har zuwa dakinta da alamu suka nuna duk an kwashe kayan ciki an bar gado kawai, dan dakin yayi fili sosai. Yan matane kusan su sha biyar, in dai kallo ne Madina ta saba da shi tunda inta fita har ta dawo bata cin karo da mace mai kalar shigar ta. Yau ma riga da wando ne, wandon na jeans ne baki, kamar ko yaushe ta nannade kafafuwan har kusan kwaurinta sai safa baka a kafarta.

Akwai farar riga kal daga ciki, ta dauki mai dogon hannu ta dora a kai, tana jan hannun baya, sai yar karamar hijab da ta saka.

Ko gilashin fuskarta abin kallo ne, waje ta samu gefe ta zauna tana karbar jakarta a hannun Adee bayan tace ma yan matan da suke cikin dakin

"Sannun ku"

Rigar saman yellow ce, ita babu yanda za'ayi ta bata ta da lalle, amman tabbas a cikin yan matan nan ko wajen wucewa ne wata na iya shafar ta. Kunshin gidan biki ba bakonta bane ba. Shisa ta mike tsaf tana cire rigar tabar farar da tayi zanzaro da ita, ganin tana neman inda zata ajiye yasa Adee karba, saida ta ninketa sannan ta fice da rigar tana barin Madina da ta zauna zata fara hada lallen ta.

*

Sai wajen tara da rabi tukunna ta samu suka barta, shima dan Salim da yake ta kiran wayar Adee ne, ita nata kunshin sai washegari ma da sassafe idan Madina din tazo ita zata fara yiwa tunda ranar ne ya kama alhamis kuma shine za'a fara bikin gadan-gadan, za'ayi kamu. Sai dai kowa yazo ya ga kunshin wasu sai yace shima za'ayi mishi, duk ta bar su a zuwan washegari idan ta gama yiwa Adee duk sai ta samu tayi musu. Nanna ta so ta kwana anan din tace mata tabar Daada ita kadai. Tunda take a rayuwarta bata taba kwana wani waje banda gida ba, bata ma jin zata iya kwana wani wajen.

Wata babbar leda Nanna ta cika mata da kayayyakin da batasan ko meye a ciki ba. Adee ta rike ledar tana rakata har wajen motar Salim din sannan ta bata kayayyakin tana mata godiya sukayi sallama, bayan motar Salim ta bude ta saka kayan ta rufe tana kowama ta bude gaban motar da kamar jira Salim yake ta zauna

"Ke ba zaki iya ce musu dare yayi ba? Ba zaki ce kin gaji kina so ki tafi gida ba, ko baiwar su ce ke?"

Saboda yanayin ta kawai ya nuna a gajiye take, ko wayar farko daya kira wajen karfe bakwai aka bata yanayin muryarta akwai gajiya

"Mutanen suna da yawa ne Hamma, shisa na tsaya na kara rarragewa, kanata kira da na kara yiwa ko mutum biyar ne kafin mu tafi tunda kai zaka mayar dani gida"

Kallon ta yakeyi kawai, itama kallon shi tayi, yanayin fuskar shi na sata kai hannu ta gyara gilashin ta

"Dan Allah kar kamun fada Hamma, nagaji sosai Allah, kaji..."

Numfashi kawai ya sauke, ba fada bane baya son yi mata, surutun ne ba zai iya ba. Yana kallo ta rufo murfin motar tana yarfe hannun ta na dama tana mikar da shi kafin ta sake yarfe shi, tsintsiyar hannun take ji kamar bata tare da hannun ta saboda yanda yayi mata sanyi, kafin tayi wani motsi sai ganin hannun tayi cikin na Salim ya rike shi yana gyara zaman shi ya saka dayan hannun shi yana murza mata dai-dai tsintsiyar hannun, kafin ya bude daga gaban motar yana dauko wani abu cikin yar roba, sai da ya dangwalo taji yajin abin har cikin idanuwanta, murza mata yayi sosai a gabaki daya hannun nata har yatsu sannan ya sakar mata hannu.

Man ya rufe ya mayar inda ya dauko, wuyan shi yana yawan rikewa idan yayi zaman karatu shisa baka raba shi da irin wannan magungunan na shafawa, sai daya tayar da motar sannan yace mata

"Saura ki murza idon ki"

Dan yasan abinda zata iya ne, murmushi kawai tayi tana jinta wani iri, ko dan yau dinne ranar farko da hannun shi ya taba nata. A kasan zuciyar ta take jin rashin kyautuwar da yake cikin hakan duk da Salim din Yaya ne a wajen ta, amman ba muharramin ta bane ba.

"Kishirwa nake ji Allah"

Ta fadi tunda zasu fito taso ta cewa Adee zata sha ruwa sai ga Nanna kuma, sai ta manta

"Akwai ruwa ki dudduba"

Salim ya furta yana jin muryar shi ta fito a bude. Sake rike matukin motar yayi gam ko zai samu zuciyar shi ta natsu waje daya. Mata ne kalar duk da yaso zai samu, daga lokacin daya fara binsu zuwa yanzun ba zai kirga hannuwan da ya murza ba. Ko yau hannun mata biyu ne suka shiga cikin na shi, zuciyar shi batayi tsalle irin haka ba. Baiji kamar yana murza wani abu a cikin kirjin shi ba.

"Madina ce, Madina... Madina ce"

Shine abinda yake fadi cikin kanshi, ko bai duba komai ba zai duba karancin shekarun ta. Gudun motar ya kara ko zasu karasa da wuri

"Hamma gudu kakeyi yau, sosai"

Ta furta muryarta na dan rawa saboda bata son gudu a abin hawa ko kadan, hankalinta tashi yakeyi, yanayin yanda sautin muryarta ya fito yasa shi rage gudun motar, badon tsoron ta ba sai dan nutsuwar shi da take neman rabuwa da jikin shi. Bai taba jin dadin hango kwanar gidan Daada irin yau ba, hannuwan shi har rawa sukeyi da ya sauke ta kofar gidan, tsaye yayi ta bude bayan motar ta dauki kayanta, sai da safen da tayi mishi ma da kai ya amsa mata ita. Sai da yaga shigar ta gida tukunna ya ja motar yayi kwana yana hawan titi da wani irin yanayi da bashi

da kalaman da zai fassara shi.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

10

"Gashi nan Daada, ya fadi me yake ce mun a gabanki kiji, watakila ke kina da kalaman da zaki fada mishi ya fahimci wannan bashi bane lokacin da ya dace..."

Julde ya karasa maganar yana kallon Nawfal da yake zaune cikin kujerar da take kallon tashi da yanayin babu abinda zai canza ra'ayina kwance cikin idanuwan shi. Taurin kai ba bakon abu bane ba, asalima in za'a koma wasu shekaru baya, tabbas da yawan mutane zasu iya cewa ko kafar shi Nawfal bai kama a taurin kai ba, in harya saka ma ranshi yin abu to babu wanda ya isa ya sauya mishi ra'ayi

"Idan kuskure ne kubarni, kuskure na ne, ni zanyi dana sani akan duk abinda zai biyo baya. Kunyi naku bangaren, kun fada mun gaskiya nine dai ban dauka ba"

Yakan fada duk idan an nemi hana shi abinda yayi niyya, shima din idan yana dan ganin kanka da gashi. Sai dai yau a karo na farko baya son ace taurin kai a ahalin sune, kar ace wannan ra'ayin rikau din jini yake bi. Saboda Nawfal ya dauko mishi abinda bai taba hangowa ba ko a tunani balle kuma yasan yanda zai shiryama daukar shi

"Aure nake sonyi Daddy, ina so a daura kafin in koma"

Kalaman Nawfal din suka dake shi kamar wanda babbar mota tayi sama da shi tana sauke shi da wani irin yanayi da bayajin akwai kalaman da zasu kwatanta shi. Kallon Nawfal yayi yana so yaga ko zolayar shi yake, sai yaga wani yanayi shimfide cikin idanuwan Nawfal din kafin ya dora zancen shi da

"Tun a waya zan fada maka, sai na bari tunda zan zo bikin Adee, da na zo din ma ina neman ta inda zan fara fada maka ne..."

Yar dariya ce da Julde ba zaice ga ta inda ta fito ba ta kubce mishi, sosai yake kallon Nawfal

"Shaye-shaye ka fara Bajjo?"

Idanuwan shi Nawfal ya saka cikin na Julde yana fadin

"Daddy..."

Wani numfashi Julde yaja yana saukewa, kwata-kwata ya rasa inda zai ajiye kalaman Nawfal balle yayi tunani akan su harya sami kalaman furtawa

"Daddy karka ce inje inyi tunani, kar kace in sake dubawa, ko kace shekaru na sunyi karanci..."

Cewar Nawfal din shima yana fitar da numfashi kafin ya dora da

"Watakila duk hakane, amman ina son ta, ko yanzun, ko nan da wasu shekaru babu abinda zai canza, me yasa zamu jira wasu shekaru in muna da wannan tabbacin?"

Kallon shi kawai Julde yake, cikin tashin hankali yace

"Baka da hankali ko Bajjo? Aure? Kasan meye aure? Yaushe ka fara karatun? Duka nawa kake da zaka rungumo maganar aure? Da me zaka rike ta? A ina zaka ajiye ta? Ko soyayyar ce ta hana kai da ita yin wannan tunanin?"

Kai Nawfal yake girgiza mishi, ya bude baki zaiyi bayani Julde ya katse shi

"Waye zai dauki yarinya ya baka? Kana fadamun kafin ka koma kake son a daura aure? Sati biyu kace zakayi, yau kwanan ka shidda, a cikin sauran kwanakin za'ayi maganar aure har a daura... Kaga Bajjo baka taba batamun rai ba kar yau ya zama na farko"

Julde ya karasa maganar yana ma Nawfal din wani irin kallo mai cike da tarin ma'anoni. Saboda tun tasowar Nawfal yana da manyance, yaune rana ta farko daya fara ganin haukan yaron, rashin hankali na sa'annin shi da kuruciya duk Nawfal baiyi ba, duk da a baya yana danganta hakan da rashin iyayen shi a kusa, duk da yana iya kokarin ganin ya bashi duk wata kulawa da zai bukata gwargwadon yanda lokaci ya ara musu

"Zasu bani, sunce zasu bani, kawai zaka ga Kawunta da yake Abuja ne, saboda suna son sanin ina da dangi a Nigeria, ba wani abu za'a kai ba banda sadaki..."

Kallon da Julde yayi mishi wannan karin na kashedi ne

"Bajjo.."

Haka ma yanda ya kira sunan shi da bai hana shi cigaba da magana ba

"Ina aiki, kudin bamai yawa bane ba, saboda yanayin karatu ba wasu awanni nakeyi ba, itama kuma tanayi, duka karatu muke, zamu gina kalar rayuwar da muke so a tare... Daddy kar kace banda hankali, karka ja layi akan abinda addini bai haramta mun ba"

Mikewa Julde yayi

"Daddy..."

Nawfal ya kira muryar shi na karyewa

"Ka taso muje"

Yanda yayi maganar ne yasa Nawfal din bai mishi musu ba ya bi bayan shi, babu wanda yake magana a motar har suka karasa gidan Daada, ko da ma suka shiga banda sallama babu abinda Nawfal ya kara cewa ya nemi kujera mai zaman mutum daya ya zauna. Yana kallon yanda Julde ya amsa tambayar

"Julde, lafiya dai ko?"

Da Daada tayi mishi, da kuma yanda ta kalle shi bayan Julde ya gama magana.

"Idan kaga ban aure ka ba, matsalar daga bangaren ka ne. Zasu tambayeni idan ina son ka, idan aure ne abinda nake sonyi a yanzun, zasu bani shawara bayan jin amsata, daga karshe zabi na zasuyi amfani da shi. Haka rayuwar ahalina take, shekaru na sha takwas, sun yarda ina da 'yan cin da hankalin sanin me ya dace da ni"

Maganganun Murjanatu suka dawo mishi, da gaske matsalar daga bangaren shi ne, shakkun da yake cikin idanuwan Julde kawai ya isa ya tabbatar mishi da haka, bai kuma son kalmomin da zaiyi amfani da su wajen gamsar da shi ba. Bayan tsayawa da kafafuwan shi, aure ne abu na biyu a cikin jerin abubuwan da yake son yi, saboda yana son samun nashi ahalin, wanda duk ruwa duk rana yasan zasu kasance da shi. Ta ina zai fara fadawa Juldea da Daada cewa babban tsoron shi a duniya shine kadaici. Shine ranar da duk zai neme su a duniyar shi ya rasa?

Yanda duk yake son ace ya kira su da nashi shi kadai kaunar su rabata yake da sauran mutane, yana son abinda zai kira na shi, yana bukatar a kaunace shi, kaunar da ba zaiji tsoron rabata da kowa ba balle har azo a ture shi daga dan inda yake a tsugunne.

"Idan na tambayeka me ka dawo yi zakace mun bikin Adee, kana da naci Nawfal, bana kaunar ganin ka kusa da ahalina, in zan iya rabasu da kai ba karamin dadi zanji ba, amman ba zan taba daina kokarin hakan ba..."

Maganganun Saratu ne suka kara mishi karfin gwiwar tunkarar Julde da tun bayan bikin Adee

yake juyayin yanda zai same shi. Yanda duk yake kaunar su yana da tabbacin soyayyar da take tsakanin su da Saratu ta girmi wannan, kauna ce da ba zai kwatanta dorata a sikeli da tashi ba sam

"Aure zanyi Daada..."

Yayi maganar muryar shi na fitowa da wani irin sanyi yana sa Daada jin kamar ya juye mata bokitin ruwan kankara kafin wani irin zafi ya maye gurbin sanyin da ya ratsa ta, jikinta gabaki daya ya dauki dumi, zuciyarta na soma wani irin tsalle-tsalle kamar tana neman sabon wajen zama a sauran jikinta, yanayin bugawar da take har cikin idanuwanta da take kallon Nawfal da su take jin karfin shi

"Kema kina tunanin banda hankalin ko Daada? Wannan ba shi bane lokacin daya kamata in zo da maganar aure ba..."

Nawfal ya fadi yana dora da

"Dan Allah idan kina da dalili ya sha bamban dana Daddy..."

Kallon shi dai takeyi zuciyarta na cigaba da dokawa kamar zata fito waje, dalilinta ko daya bashida alaka da duka tunanin su, dalilinta bata san ta inda zata fara furta shi ba

"Kina jin shi ko Daada, kice wani abu"

Julde ya fadi yana kallonta, da idanuwan shi yake rokonta da ta taimaka mishi don yanayin Nawfal din kawai ya tabbatar mishi da cewa bawai ya fada mishi bane saboda yana neman izini, goyon baya yake so kawai, amman ko bai amince ba da wahala idan maganar auren nan ba zata zama abu na farko da zai haddasa wata tsaga a alakar su ba.

"Yarinyar yar ina ce?"

Daada ta tambaya tana saka Nawfal sauke wani numfashi da baisan yana rike da shi ba

"Murjanatu... Sunan ta Murjanatu, duka iyayenta suna zaune ne acan kasar da nake karatu, amman asalin su yan garin Adamawa ne, dangin su da yawa suna can, wasu suna zaune a Abuja, suma aikine ya kai babanta can, yayyen ta guda biyu duk suna nan Abuja suma...ni ba zama zanyi acan ba Daada, zan dawo, zamu dawo tare idan muka gama karatun mu"

Ya karasa maganar yana kallon Julde da har lokacin akwai shakku cikin idanuwan shi

"Daada kiyi magana da yaron nan, da gaske fa yakeyi..."

Baki Daada ta bude sallamar Madina ta katse mata maganar ta, Nawfal ne ya amsa

"Hamma... Daddy"

Cewar Madina cikin sigar gaisuwa

"Zafi nake ji wallahi"

Ta furta tana wucewa nufar hanyar dakinta, sai lokacin suka ga Salim da yayi sallama cikin budaddiyar muryar shi, daga makaranta ya wuce yaje ya dauko Madina saboda tunaninta ya hana shi sukuni har a aji, motar shi ta fara tsaitsayawa, dakyar ya iya samun waje gefen titi yayi parking dinta ya kira mai mishi gyara. Sai da yazo ya bashi mukullin tukunna suka tako shi da Madina tunda sun kusa gida, tun a hanya take ce mishi zafi take ji tana shiga gida zata fara watsa ruwa kafin tayi shirin islamiyya. Motar Daddy daya gani ne a wannan lokacin a gidan Daada yasa shi yanken hukuncin shiga dan yaga ko lafiya, in yaso sai su wuce da Daddy ko bai mayar da shi makaranta ba ya rage mishi hanya.

Kallon su yayi yana zare takalman shi hadi da shiga cikin dakin, yanayin su bai nuna kome suke tattaunawa mai dadi bane ba

"Ina wuni"

Ya furta kamar wanda akayiwa dole yana kallon Daada

"Daddy..."

Ya kira, duk yanayin da Nawfal yake ciki bai hana shi kallon Salim ba, daga shi har Madina suna son kiran sunan mutum a maimakon gaisuwa. Sai dai kafin Daddy yayi magana Salim din ya juya, baya son hayaniya. Yana da tabbacin kome suke tattaunawa bai shafe shi ba, baya son sani balle kuma suyi tunanin saka shi ciki.

"Ina zaka je?"

Julde ya tambaya, dan juyawa Salim yayi yana amsawa da

"Naga kuna magana ne..."

Kamar hakan kawai hujja ce da zai bar musu gidan

"Ka dawo ka zauna ayi maganar da kai"

Dan runtsa idanuwan shi yayi yana bude su, dole dai sai sun tsoma shi cikin zancen nan da ya san bai shafe shi ba ko kadan. A nutse ya taka yana samun hannun kujera ya zauna a kai

"Aure Nawfal yake son yi, so yake a daura kafin ya koma"

Kallon Nawfal din Salim yayi, sai dai a nashi idanuwan babu komai sai mamaki, saboda aure baya cikin tsarin abubuwan da yake hango rayuwar shi da shi, hayaniyar nan ba zai iya ba. Amman hakan baya nufin dan wani yana so yayi sai ace kar yayi. Adee ma gashi nan tayi, kuma har ran shi yayi farin ciki da auren nata

"Kana ganin auren ne abinda kake son yi a wannan matakin na rayuwar ka?"

Salim ya tambaya, kai Nawfal ya jinjina mishi

"Karka amsa ni idan kana da shakku, ka tabbata?"

Kai Nawfal ya sake dagawa, girar da Salim ya daga mishi yasa shi cewa

"Ban fada ma Daddy ba sai da na tabbata, shekara daya ina neman tabbaci a kowacce rana..."

Mikewa Salim yayi ya kalli Daddy

"Nanna tace sanda kukayi aure da kadan ka girmi Bajjo, karkayi amfani da shekarun shi a matsayin hujja Daddy, in baka da dalili mai karfi karku hana shi..."

Numfasawa yayi saboda kan shi harya fara sarawa da maganar da yake yi

"Ku barshi yayi auren shi..."

Wanda duk yazo da maganar aure a cikin kannan nashi zasu samu dukkan goyon bayan shi, zaiyi duk wani abu da zai iya wajen ganin basu fada irin rayuwar da yake ciki ba

"Aure zai hanaka biye-biye, zai nutsar da kai waje daya"

Haka yaji wani a ajin su ya fada. Yana da yakinin Nawfal na da dalili mai karfi da yasa yake sonyin aure a wannan matakin na rayuwar shi, kasar yabari don karatu, Allah kadai yasan kalar mutanen da suke zagaye da rayuwar shi

"Ka tabbata bakayi dana sanin zabin nan ba Bajjo"

Ya fadi yana saka Nawfal din yin murmushi

"Hamma..."

Hannu ya daga mishi, shi duk irin wannan abubuwan baya son su

"I love you"

Nawfal ya fadi yana fadada murmushin shi ganin yanda Salim din ya bata fuska yana taku biyu da nufin karasawa kan kujerar da Nawfal yake yana saka shi mikewa babu shiri, kallon shi Salim yayi cike da kashedi yana ficewa juyawa ya fice daga dakin.

Kamar bai fadu maganganun da zasu canza komai ba
Maganganun da zasu zama silar faruwar komai

Kwallar da Daada taji ta fara tarar mata cikin idanuwa tayi saurin saka hannuwa ta dauke su kafin ma wani ya kula. Shikenan abinda ta gina a cikin zuciyarta ya rushe, hangenta ya datse lokaci daya. Wata ta maye wajen da take fatan Madina ce zata zauna a wajen. Yanda kaddara take wasan kura da rayuwar su a kowanne juye na karya mata zuciya. Ba dan kar tayi sabo ba da ta tambayi dalilin da yasa ko sau daya rayuwa ba zata tafi kan tsarinta ba.

"Hamma ma yace karku ce a'a, kaji Daddy, dan Allah karka ce a'a..."

Nawfal ya katse ma Daada tunanin da take yana sata kallon Julde da fuskar shi take dauke da yanayin rasa tudun dafawa

"Daada..."

Ya soma ta girgiza mishi kai

"Allah yasa hakan ne mafi alkhairi, kaje kaga dangin yarinyar kafin ka yanke wani hukunci..."

Murmushin da Nawfal yayi bayan ya dawo inda yake ya zauna na saka zuciyar Daada kara tsinkewa saboda kamannin shi da Bukar da suka kara fitowa fili. Kafin wani ya sake cewa wani abu Madina da ta fito cikin shigar islamiyya ta riga su da fadin

"Hamma kana nan har in dawo amman ko?"

Kai Nawfal ya girgiza mata

"Zamu dan fita da Hamma anjima, kilan in dawo dai, me zaki ajiye mun?"

Dariya tayi

"Zan dafa maka kifi"

Kai Nawfal ya jinjina

"Zan dawo"

Dunkule hannunta tayi tana daga mishi babban dan yatsan ta alamar hakan yayi mata

"Daddy na tafi...Daada sai na dawo"

Binta da kallo Daada tayi, Julde ne ma ya iya cewa

"A dawo lafiya"

Wani abune Daada taji yayi mata tsaye a kirjinta, lokaci daya duk wani tunani da takeyi akan goben Madina ya sauya. Ta ina zata fara yanzun?

"Daada yanzun duka Nawfal nawa yake?"

Julde yace cikin nauyin murya, ko shi da Salim yake magana akan auren wuri da yayi, bawai zabi aka bashi ba a lokacin, kawai hadasu akayi da Saratu

"Zamanin mu da nasu ba daya bane ba"

Murmushi Daada tayi kirjinta yayi mata nauyi, hakan yasa Nawfal mikewa yana nufar dakin daya kan kwana ciki duk idan yazo gidan dan ya basu damar yin magana

"Shisa zaka barshi yayi auren shi, zamanin ba daya bane ba...kar kaja maganar nan da shi Julde...ka kyale shi tunda ba wani abu marar kyau bane ya dauko"

Wani irin numfashi Julde ya sauke, ranshi a jagule yake jin shi, a saman bukatar ta da fatanta kasancewar Bajjo a cikin su yafi muhimmanci, hana shi aure don bukatar ranta ta cika ba zai zama sanadin da zata rasa shi gabaki daya ba. Idan har jinin Datti ne yake yawo a jikin Nawfal to tasan wannan maganar auren ba izinin su yake nema ba, goyon bayan su kawai yake bukata, ko sun yarda ko basu yarda ba bazai canza komai ba.

"Karka ja maganar nan da shi..."

Ta kara jaddadawa, yanayin muryarta nasa wani abu tsirgama Julde saboda yasan inda tunaninta yake son kaita

"Ai shikenan..."

Ya furta yana sauke ajiyar zuciya

"Amman ba zai zauna kasar nan ba, yana gama makarantar nan dawowa zaiyi"

Dan murmushin karfin hali Daada tayi

"Daman yace ba zama zaiyi ba"

Sai dai ita kanta ta maimaita kalaman ne ba dan ta aminta da su gabaki daya ba

"Zan dawo Daada"

Taji wannan kalaman har sun isheta a tsayin rayuwar ta, sai dai a duk mutanen da suka furta mata su Nawfal ne na farko daya fara cikawa, shakkun da take da shi kan kalaman ya dade da kafa rassa a cikin zuciyarta, dan ya dawo yanzun baya nufin in ya koma zai sake dawowa, wannan ma tagan shi akan Yelwa. Da zatayi fata ne, fatan kar ya zamana Nawfal bai cika alkawarin shi na zai dawo ba. Sai dai numfashi kawai ta sauke.

Kowanne rai da nashi kaddarar, yau ma ta sake ganin wannan kaddarar da take tunanin ta shiga tsakanin Nawfal da Madina kamar yanda tayi fata, shisa ba zata sake wani fatan ba a yanzun, idan kaddarar Nawfal ta hada da dawowa zai dawo, idan bata hada ba sai dai ta sake rungumar kaddara a duk yanda tazo mata a karo na ba adadi kenan. Fatanta bashi da tasirin canza komai.

**

Wayar shi Nawfal ya mika mishi, karba Khalid din yayi

"Na fara gajiya fa...ni bana ma amfani da wayata yanda nake so saboda kun isheni kai da ita...ka siyi layi Malan"

Dariya Nawfal yayi

"Kai Hamma, yaushe muke isarka din? In ba irin wannan lokacin ba ai bama waya... Layin zai zama asara tunda ba dadewa zanyi ba. Haka zakayi ta hakuri da mu"

Kai kawai Khalid yake girgiza, ya kalli inda ya ajiye kayan wankin da aka kawo mishi da yamma

"Na kwashe na shirya maka duka wardrobe dinne ma"

Kallon shi Khalid yayi, yana sake kallon yanda dakin ya samu kulawa ta daban tun zuwan Nawfal din, bawai shara bace bayayi, yana share dakin kusan kullum, kawai dai bashida lokacin mayar da wasu abubuwan wajen daya dauke su. Nawfal kuma ya kasance cikin jerin mutanen da suke son ganin komai a tsare, har litattafan shi idan ka duba jakar shi ta makaranta a wani irin tsare suke, bi da bi. Inda yake ajiye fensiran shi da biro ma daban ne. Ko yaya ka taba mishi kaya yana dawowa wajen zai nufa ya gyara abin shi yanda yake son ganin shi.

Wajen wardrobe din Khalid ya karasa ya bude yana ganin yanda Nawfal ya shirya komai, harta

kananun wandunan shi layi daban ya saka su. Sai yaji kamar ace karya taba kayan, ya hargitsa shirin nan

"Aure zanyi Hamma"

Nawfal ya fada cikin sanyin murya, wardrobe din Khalid ya rufe

"Na sani, kowa ma ai aure zaiyi idan lokaci yayi, ko dan kayi budurwa sai ba zamu huta ba?"

Kallon shi Nawfal yayi

"Aure zanyi Hamma..."

Ya sake maimaitawa yana sa Khalid kallon shi

"Ina nufin kafin in koma za'a daura, aure zanyi kafin in koma"

Sosai Khalid yake kallon shi wannan karin

"Nasan ya kamata in fada maka tunda na dawo, amman nabari ne in fadama Daddy tukunna, shi ya kamata ya fara sani kafin kowa"

Kai Khalid ya jinjina

"Allah ya sa alkhairi"

Ya furta yana rasa abinda yayi niyyar yi kafin Nawfal din ya sauke mishi wannan zancen saman kai

"Hamma..."

Nawfal ya kira, amman hankalin Khalid din yaki komawa kan shi

"Hamma mana..."

Waje Khalid ya samu gefen gadon ya zauna yana daukar wasu dakika kafin ya daga kai ya kalli Nawfal

"Me yasa? Ka fahimtar dani yanda zangane"

Saboda har a ranshi yana son gane dalilin da zaisa Nawfal yanke wannan babban hukuncin da yake ganin baiyi hankalin da zaiyi shi ba, duk da tsiran da yake tsakanin su bawani mai yawa bane ba. Yayi girman da yasan duk inda za'ayi magana ta aure ba karamin abu bane ba.

"Ni kadai ne Hamma, tun banda hankalin mutanen daya kamata su tsaya tare dani suka fara watsar dani, ina da ku na sani, ina jin kamar bai kamata ba da nace maka ni kadai ne..."

Kallon shin dai Khalid yakeyi

"Ina kaunar ku, ina kaunar ku fiye da yanda zan fada, nasan kuna kaunata, da yawa, ba zan kira ku nawa ni kadai ba, ba zan kiraka nawa ni kadai ba, ina rabaka da mutane da yawa a yanzun, lokaci zaizo da zan sake rabaka da wata... Ina son abinda zan kira nawa"

Wani sauti ne ya kwace ma Khalid din da yake tsakanin dariya da wani yanayi da bashi da suna

"Ita din ba zaka rabata da wani ba?"

Ya tambaya yana jin wani abu ya tokare mishi makoshi

"Ba kaman ku ba..."

Kokarin hadiye abin da yake a makoshin shi Khalid yakeyi, maganganun Nawfal sun mishi zafin da ya kasa fahimtar su

"Tana da iyaye da yan uwan da ta taso da kaunar su kafin taka, ka fadamun bambancin da yake tsakanin ta da mu... Kana so ka fadamun mu ba zamu taba zama naka kai kadai ba, amman ita zata iya zama? Mu muna da wani lokaci na barin rayuwar ka... Ko dan kaine kasa lokacin barin mu saboda ka samu wadda zaka kira taka?"

Tunda ya fara magana Nawfal yake girgiza mishi kai

"Idan baka fahimce ni ba babu wanda zai fahimce ni Hamma, dan Allah karka fassara kalamai na idan baka fahimta ba, karkayi mun haka"

Nawfal ya karasa muryar shi na karyewa

"Ka fahimtar dani Bajjo..."

Numfashi Nawfal ya sauke zuciyar shi na rawa

"Idan baka so zan hakura, zan bar maganar nan... "

Dan tunda ya yanke hukunci bai dauka akwai wani dalili da wani zai bashi ya sauya mishi ra'ayi ba. Yasan Khalid na da muhimmanci a wajen shi, bai taba tsayawa ya auna girman muhimmancin ba sai yanzun, da a karo na farko tun haduwar shi da Murjanatu yaji zai iya barinta idan har zata zama silar samun matsala tsakanin shi da Khalid din

"Babu wani abu a yar duniyar nan tawa da yake da muhimmancin alakar da take tsakanin mu"

Cewar Nawfal yana saka Khalid jin kafafuwan shi sunyi sanyin da in ba'a zaune yake ba zasu kasa daukar shi, yaja iska ta bakin shi yana fitarwa yafi a kirga kafin ya samu natsuwar fadin

"Ka kalleni Bajjo, lokaci daya nake da shi na barin rayuwar ka, lokacin da ba rayuwar ka bace kawai abinda zan bari, duniyar ce gabaki daya...ba kai kadai bane ba, duk tunanin da yake fada maka haka ka karya tashi, idan kana jin baka da kowa kana da ni, kana jina ko?"

Kai kawai Nawfal ya iya daga mishi

"Idan aure ne zabin da kayi ni banda matsala da hakan, kawai ina so kasan ba abu bane da zaka zaba yanzun ka canza anjima, rayuwar yarinyar mutane ce akan layi Nawfal"

Khalid ya karasa da kiran asalin sunan shi dan ya san maganar da yake na da muhimmanci

"Bana jin zan iya ba mai shekarun ka 'ya ta Bajjo, ba kuma zan daina ganin wautar mutumin nan ba...kadaici kowa yakan ji shi lokaci zuwa lokaci, karya zama dalilin da kawai zaka aure ta, ka hanga shekaru masu zuwa, a cikin shekarun ka duba hali na rashin tabbas, hali na rashin lafiya, ka duba yiwuwar jin dadi da rashin shi, kana ganin kanka a tare da ita a duka yanayoyin?"

Numfashi Nawfal ya sauke, kalaman Khalid din na ratsa zuciyar shi

"Idan ka shiga cikin auren ba zaka iya fita da saurin da ka shige shi ba... Ba zaka iya ba...Bajjo wasan nan ba da rayuwarka kawai zakayi shi ba harda ta Murjanatu da duka ahalinta... Karka fara abinda ba zaka iya karasawa ba..."

Cikin idanuwa Nawfal ya kalli Khalid din

"Ina son ta"

Ya amsa

"Soyayya kawai tayi kadan"

Idan Nawfal bai sani ba, shiya sani, wasu zasu karyata ana ganin soyayya kwance a idanuwan mutane, idan baiga soyayyar Julde a idanuwan Saratu ba shima zai iya karyatawa, amman bata hana su samun matsalar da suke tunanin baya kula ba, suna fada ko da baisan me yake hada su ba, sosai suke yawan yin fada yana kula da hakan. Da soyayya ta isa da wadda Nannar shi take ma Daddy ta hana musu samun matsala

"Bansan sauran abubuwan ba Hamma, amman zamu neme su a tare, shine kawai alkawarin da zan iya a yanzun..."

Kai Khalid ya jinjina

"Aure zakayi Bajjo, aure zakayi"

Khalid yake fadi wata dariyar mamaki da tsoron wannan babban matakin da rayuwa ta kawo dan uwan shi na kwace mishi, shima dariya Nawfal yayi, tsoron da yake gani a fuskar Khalid din na taba shi, a karo na farko shima matakin na bashi tsoro, sai dai tare da tsoron babu shakku ko kadan

Rai da kaddara
Murjanatu na daya daga cikin kaddarorin shi
Tana daya daga cikin hasken da zai yaye wani bangare na duhun da yake bibiyar rayuwar shi yana jiran cikar lokaci.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

11

Shiru bai taba mishi yawa ba, lokutta da yawa ma yana jin yayi mishi kadan, ko shi kadai ne zaune a bangaren su cikin gida, sai ya dinga jin hayaniya a cikin shirun dakin, karar agogo, fanka ko AC din cikin dakin, ko wani kwaro da ba zaice ga inda yake ba, hakan kawai na hana shi sukuni, shisa ya siyi abin toshe kunne, yana da su wajen kala hudu, su kansu basa taimaka mishi, idan yasa duk kananun hayaniyar sai ta daina isa cikin kunnuwan shi, sai kuma ya dinga jin surutun da yake wanzuwa tsakanin kwakwalwar shi da zuciyar shi.

Yana rasa a cikin mutane shi din wanne iri ne? Ya kanyi tunanin ko irin shi guda nawa ne, ko ya suke ji da hayaniyar da take cikin yau da kullum? Musamman idan ya hasaso kasancewar su cikin halin rashi, babu wadatar da zasu samu wajen kebewa su kadai. Amman yau shirun da yake cikin motar yayi mishi yawa, ba dan gilasan suna kulle ba, idan shi kadaine zai dinga jin karar sauran motoci harda ma kukan tashi motar. Sai dai duk lokacin da zai zamana shi da Madina ne a zaune cikin mota, ko kuma tana gefen shi baya jin kowacce irin hayaniya.

Asalima banda muryarta da dariyarta babu wani abu da yake isowa kunnen shi, ko bata magana kamar ganinta na saka komai yin shiru ne. Sai dai yau shirun nata yayi mishi yawa, tunda ta fito ta gaishe da shi ta koma cikin mota ta kwanta kamar marar lafiya, har suka fita daga layin suka hau titi ko motsi baiga tayi ba, lokaci zuwa lokaci yana kallonta. Matsalar bai iya hira ba, bai taba fara hira da wani ba, ko a cikin yan gidan su kuwa, banda gaisuwa sai dai in kaine ka tambaye shi wani abin, ya rasa me ya kamata yace mata.

"Lokacin damuna ne ake noma tumatiri ko?"

Tambayar ta kubce mishi tana saka Madina juyo da kanta tana kallon shi na wasu dakika cike da mamaki, shima dan raba idon shi yayi daga titi yana kallon ta

"Shine abinda ya fara zuwa kai na..."

Ya fadi yana maida hankalin shi kan titi, wata irin dariya Madina ta kwashe da ita

"Da gaske Hamma?"

Ta tambaya, kafadu yadan daga yana rausayar mata da kai

"Kinki mun hira... Bansan me zance ba"

Yayi maganar da dukkan gaskiyar shi, hannu takai ta gyara gilashin fuskarta tana sauke numfashi, har lokacin da murmushi a fuskarta. Kawai ba zatace ga asalin abinda yake damunta ba duk satin. Ta san zazzabi, da shine zata gane, babu inda take ji yana mata ciwo, kawai tana jin kamar dai akwai wani abu da babu a cikin rayuwarta a satin.

"Bajjo zaiyi aure"

Daada ta fada mata, ta zabi ta fada mata lokacin da ta cika bakinta da ruwa tana shirin hadiye wa, ta kuwa sarke tana tarin da ta kusan shafe mintina biyar bai tsagaita mata ba, idanuwanta duk sun tara hawayen wahala

"Cikin satin nan idan Allah ya bamu aron rai"

Daadar ta sake fadi, ko da taso yin wata tambaya bata san ta inda zata fara ba, tambayoyin nata da yawa, wata na danne wata haka suka dinga tasowa cikin kanta. A lokaci daya kuma tana nemar ma maganar wajen zama a tare da ita cike da son gane me hakan yake nufi da tata rayuwar ko wata dangantaka da take tsakanin auren na shi da ita. Shisa sai komai yayi mata yawa, abu dayane take jin zata iya cewa, kamar Nawfal din bai kyauta mata ba, kamar daga bakin shi ya kamata ta fara ji. Kamar ya kamata ace tasan maganar.

"Kunyi shakuwar da zai gaya miki zaiyi aure ne?"

Wata murya ta tambayeta, ta so tayi gardama, taso ta zayyano ma muryar shekarunta na kuruciya, lokuttan da Nawfal yake daukota akan bayan shi daga makarantar islamiyyar su zuwa gida kamar bata da wani nauyi, lokuttan da take jiran zuwan shi dan ta zayyana mishi duk wasu kananun bukatunta ya kuma cire kudin shi ya biya mata su. Sai ta tuna da shekaru biyun da suka ja layi a tsakanin su, abubuwa da yawa zasu iya fara a cikin awanni biyu, balle a tsallaka awannin da suke cikin ranakun da suka shude tare da shekara biyu.

"Ma shaa Allah. Allah ya tabbatar da alkhairi"

Tace maimakon furta ko da daya daga cikin tambayoyin da take da su ne. Hidimar da ta fito da ita ta cigaba dayi, ba dai tasan dalilin Daada na binta da wani irin kallo mai cike da ma'anoni ba. Ba zatace tausayawa kawai ta gani a cikin kallon ba, kamar Daada na son sanar da ita auren Nawfal din yana da alaka da rayuwarta ne, ta kasa fahimtar kalaman da Daada ta zabi tabar su cikin idanuwanta maimakon ta furta mata su. A ranar da ta shiga dakin ta, bayan ta zauna ta dauki agogon Nawfal kamar yanda sabonta yake sai ta tsinci kanta da saukowa daga kan gado tana neman waje ta jefa agogon a ciki.

Har yau da take zaune a cikin motar Salim da yazo daukarta zuwa restaurant din da suka yanke hukunci zuwa yasu-yasu dan gudanar da yar walima ta taya Nawfal din murnar auren shi da aka daura a safiyar Asabar din ba zatace ga dalilinta na adana agogon ba. Hannun Salim da taji a gefen kuncinta na sata saurin janye jikinta kamar wadda wuta ta taba, sake mika hannun shi yayi kamar bai ga yanda ta hade da murfin motar ba, ji yayi babu zazzabi a jikinta. Sannan ya janye hannun shi yana gyara zaman shi yana fadin

"Shirun ki yayi mun yawa"

Numfashi ta sake saukewa a karo na biyu

"Banda labari ne fa... Yau zan missing karatu a islamiyya, bana fashi in ba rashin lafiya ba sai bikin Adee, zasu ga banje ba yau ma kuma ban fada ba"

Kai ya jinjina

"Zasu dake ki ne?"

Saboda tunanin wani zai taba lafiyarta na sa jikin shi daukar dumi da wani yanayi na bacin rai

"A'a, ba su cika dukan fashi ba inba kana yawan yi ba"

Duk da haka hankalin shi yaki kwanciya

"Kin tabbata?"

Yayi tambayar cikin harshen turanci

"Na tabbata"

Ta bashi amsa cikin harshen itama, yana shan wata kwana ya dan rage gudu alamar yana son samun damar da zai tsallaka titi ne, tana kuma iya ganin sunan restaurant din Tasty Corner. Sai da ya tsallaka ya samu waje yayi ajiye motar yana kashewa tukunna take kara ganin kyawun restaurant din tun kafin ma su shiga. Da yake banda makaranta babu inda take zuwa, sai nan cikin unguwar su, sai kuma gidan Julde da shima tana dadewa bataje ba, a garin Kano tsaf zaka siyar da ita. Babu inda ta sani, yanzun ne ma da Salim ke yawon dauko ta daga makaranta yakan biya wani wajen yayi mata siyayya, har wani wajen saida litattafai sukaje da bata san a ina bane ba, amman yayi mata kyau matuka.

Da kan shi ya zagaya ya bude mata murfin motar ta fito. Sai lokacin ya kalli kayan jikinta, jeans ne baki, kamar yanda ta saba ta nannade shi har kwaurinta ya dan fito, sai fararen kambas, rigace ta sanyi mai dogon hannun da taja baya, itama farace kamar hijabin kanta. Ta dora wata farar hular sanyi a saman kanta. Murmushi yayi yana tsayawa a gabanta yana kara mamakin gajartar Madina, da kadan kanta ya wuce cikin shi, kama hular yayi yana cire ta daga kanta ya duba kamar mai son gano wani abu a jiki.

Murmushin dai ya kasa barin fuskar shi har lokacin, gyara hular yayi a cikin hannun shi yana dorawa saman kanta kafin ya gyara mata ita saman kanta, ganin yanda take kallon shi yasa shi amfani da dan yatsa ya tura mata gilashin da yasan gab take da dago nata hannun ta gyara mishi zama.

"You look like a Mug"

Salim yace muryar shi dauke da wani irin yanayi da yake jin fitowar shi daga zuciyar shi, kai Madina take girgiza mishi tana kokarin danne dariyar da take son yi saboda hada tsayinta da kofi da yayi

"Ba zaka fara kirana da Mug ba Hamma"

Girar shi daya ya daga mata

"Gargadi ne?"

Kai ta girgiza da sauri tana saka shi lumshe idanuwan shi yana bude su a kanta

"Mug it's then... Muje"

Juyawa tayi kuwa, wani murmushin na kara kwace ma Salim, da gaske tayi kama da yan

kofinan nan masu kyau da ake zuba coffee a ciki, masu murfin da marassa murfi, amman masu kyan cikin haka yake ganin tsayinta a gaban shi

"Mug"

Ya furta dai-dai kunnuwan shi da murmushi a labban shi, har takai kofar wajen ta juyo tana kallon shi da tunanin abinda ya tsayar da shi, taku biyar yayi ya karasa inda take suna shiga tare, can wani teburi da yake karshen wajen ya hango su Khalid, sai kuma hannuwan Adee duka biyun da take daga musu kamar yace bai gansu ba. Baima san me yasa mijinta yabar ta fitowa ba duka sati daya da aure, dariya take tana sake daga musu hannuwa, dakuwa Salim yayi mata daga inda yake yana kallo ta sake kwashewa da dariya kamar wadda ya bawa kyauta.

Suna karasawa tana tashi daga wajen da take zaune ta kama hannun Salim din da yake kokarin kwacewa yana daure fuska

"Wallahi nayi kewar ku sosai"

Ji tayi kamar tayi waya bakwai bata gansu ba

"Sakeni dalla"

Tabe baki Adee tayi, matsalar Salim ba'a mishi gwaninta, tana zame hannuwanta daga nashi ya daga ya dillar mata bakin da ta tabe mishi

"Dan kinyi aure zaki mun rashin kunya"

Dafe labbanta tayi babu shiri

"Ouchh... Hamma"

Kallon da yayi mata yasa ta koma ta zauna, kujera yaja shima ya zauna yana dan kara janta gaba, kafin ya kalli agogon hannun shi

"Minti talatin..."

Ya fadi yana kallon su, yana da hidimar da zaiyi, ko bashi da ita baida hirar da zaiyi da su, hayaniyar zata dame shi. Gara yaci abinci ya barsu suyi hirar su cikin nutsuwa. Kallon juna Khalid da Nawfal sukayi, dan sunyi gulmar shi, babu ma wanda ya kawo zaiyi minti talatin din duk a cikin su

"Ni nace maka Hamma ba zai minti biyar a wajen nan ba"

Cewar Khalid

"In za'a iya mishi takeaway din duk abinda yake so a kasa da minti biyar ba zai kai ba"

Nawfal ya kara, basu taba tunanin zai zauna a waje irin haka yaci abinci ba

"Nasan kunyi gulmata"

Ya fadi kasan makoshi yana duba menu din da waiter din wajen ya kawo mishi bayan ya dan daga hannu cikin alamar kira, dankali da kaza ya zaba sai bakin lemo yana kallon Madina da tunda ta zauna idanuwanta na kan Nawfal, bata ganshi ba tun da akayi mata zancen bikin, bai kwana a gidan Daada ba, sanda yazo tana makaranta sai dai inta dawo Daada tace mata Nawfal ya zo. Yanzun da ta ganshi kawai sai take jin kamar abin wasanta da ta dade tare da shine aka fisge daga hannun ta.

Kai tsaye ba zatace ranta ya baci ba, amman kuma bata farin cikin da kwacen, wani yanayi ne a tsakanin abu biyun da bata san wacce kalma zatayi amfani da ita wajen fassara shi ba

"Madina..."

Salim ya kira a hankali yana dan daga mata Menu din da yake hannun shi bayan ta kalle shi

"Abinda duk aka baka"

Ta ce cikin sanyin murya, su Nawfal ya kalla, kowa ya fara jero abinda za'a kawo mishi

"Madina yaushe zaki zo gidana? Kinsan ina fushi daman, baki je kaini ba, na kula ai"

Murmushi Madina tayi, har ranta tayi niyyar zuwa kai Adee din tunda harda Daada, a wajen motocin daukar amaryar taji an riko mata hannu ana janta, kafafuwan shi ta fara kallo ta gane waye

"Hamma..."

Ta kira, bai amsata ba ya cigaba da janta har suka inda motar shi take ya bude murfin yana sakin hannunta, yanayin fuskar shi yasa ta shiga batare da tayi musu ba, ya ja motar da bai tsayar ba sai a kofar gidan Daada, nan sukayi zaman su a ciki suna hira, ko tace tana mishi surutun da yake amsawa dai-dai. Har fita suka kara yi ya siyo musu tsire mai yawa da lemo.

"Zan zo, Hamma zai kawo ni. Kibari kunshin ki ya karasa gogewa, sai ki kira Daada kinga idan nazo sai in miki sabo"

Kai Adee ta jinjina

"Kin kusa ki wanke laifin ki"

Yar dariya tayi tana kallon Nawfal

"Hamma Ango"

Hararta yayi

"Yanzun ne zaki kula ni? Bana so"

Hannuwanta ta hade waje daya cikin ban hakuri

"Ance angwaye basa fushi fa ko Hamma Khalid?"

Dariya Khalid yayi

"Ni zan shiga fadan ku? Ku shirya ku ware ni yanda kuka saba? Babu ruwana, sai dai babban Yayaa"

Ya karasa maganar cikin sigar tsokana. Wani kallon kashedi Salim ya watsa mishi yana saka shi gyara murya

"Idan na taso saina mare ka"

Salim ya fadi yana sa Adee kwashewa da dariya

"Me nayi ni kuma?"

Ko da ba'a fara kawo musu abincin su ba yasan ba amsa zai samu ba. Hira ce ta barke tsakanin Nawfal, Khalid da Adee, Salim abincin shi yake ci duk da maganganun su da yake ji har cikin kwakwalwar shi, Madina ma abincin take ci tana tsintar dankalin dai-dai. Salim na kallonta ta gefen idanuwan shi, dan ture plate din shi yayi yana jan nata bai damu da kallon mamakin da take mishi ba, wuka ya dauka yana yayyanka mata cinya guda biyu kanana yanda zata iya dauka kafin ya tura mata plate din batare da yace komai ba yaci gaba da cin abincin shi.

Lemon da yake gabanta ma shi ya bude yana zuba mata a kofi ya tura mata kusa da ita. Da ya gama cin nashi abincin ma ita yake kallo. Lokaci zuwa lokaci takan dago su hada ido, ta saba ciye-ciye a gaban shi, tasan dai idan ta ajiye cokalin magana zai mata tunda ba wani ci tayi ba, ita kuma tana turawa ne badan tana gane dandanon abincin a bakinta ba, sai da taci kusan rabin naman da yayayyanka mata tukunna ta ajiye cokalin a ciki tana dan ture plate din. Ganin girar da Salim ya daga mata cike da alamar tambaya ya sata fadin

"Na koshi Allah, tuwo Daada tayi mana"

Baice komai ba ya mike yana karasawa inda zai biya kudin ya kuma bama Madina damar yi musu sallama, idan yabarta zasu mayar da ita gida ya sani, bai san ko tana so ta zauna ba, ba tambayar ta zaiyi ba. Yanda suka zo tare haka zasu koma tare, saboda hakan yake jinyi badon yana da wani kwakkwaran dalili ba.

"Allah yasa alkhairi Hamma, Allah ya kawo zuri'a dayyi ba"

Madina ta fadi tana rasa dalilin da yasa take jin wani iri

"Zan zo anjima"

Nawfal ya amsa, kai ta jinjina mishi tana mikewa, Khalid ne ya kalle ta da fadin

"Ki bari mu tafi gabaki daya mana, ba sai mu sauke ki ba"

Kai ta girgiza mishi

"Hamma zai ce a'a"

Dakuna mata fuska Khalid yayi

"Ka kyaleta Khalid, kiyi tafiyar ki Madina, saina kira Daada..."

Numfashi ta dan sauke bata ma amsa ba ta juya

"Kai ina ruwan ka? Baka ga tare suka zo ba?"

Ruwa Nawfal ya kurba ya hadiye sannan yace

"Ni kadai naga Hamma ya yankawa Madina nama?"

Dariya Khalid yayi

"Wallahi kiris in shake da taliya... Anya Hamma?"

Kai Adee ta girgiza

"Kuna da bala'in gulma yaran nan, ina ruwan ku? Sai na fada mishi"

A tare suka kalle ta, dan kasa tayi da murya kamar tana tsoron Salim din zaiji ta

"Amman da gaske me yake faruwa ne?"

Kallon 'maganar da nakeyi kenan ai' Khalid yayi. Hirar suka dan karayi kafin su saki zancen suna kama wani tunda sun san koma menene ba zai wuce su ba, suna zaune zai zagayo kowa ma ya gani.

*

"Yanzun wanne mai hankali ne ya dauki yarinya yaba Bajjo?"

Saratu ta fada tana tabe baki

"Mai irin hankalin wanda ya daukeki ya bani"

Julde ya amsa ta, amsar kuma tayi mata zafi

"Ubana kenan?"

Bai ce komai ba, sakon ya isa baya bukatar jan magana kuma

"Idan wulakanci abinyi ne ka cigaba da wulakantani Julde, Allah ya baka sa'a, hirar arziki ma ba zan taba samu inyi da kai ba saika gasa mun magana"

Shirun dai shi ya kara yi mata yana cigaba da neman kayan da yake son sakewa dan ya fita yabar mata gidan ma gabaki daya, a gajiye ya dawo daga Abuja tunda acan ya kwana aka daura aure da safe ya tsaya wata hidima da ta shafi kasuwan cin shi tukunna ya juyo

"Kuma sanda na aure ka aika girmi Bajjo, shekarar ka wajen ashirin da biyar"

Gani tayi da gaske bashi da niyyar amsata, wasu hawaye taji masu zafi sun taru cikin idanuwanta. Duk kawayen ta haka suke cewa tayi sa'a, mijinta ga arziki ga kyau

"Ko yanzun mijinki yaso zai auri budurwa wallahi da zata bi kyawun shi"

Wata kawarta ta taba fada, dan yanzun ma sun raba jaha, daina sakar mata fuska tayi tun da aurenta ya mutu, saboda matar ba karamar gogaggiya bace ba. Ko da aurenta ma duk yanda kuke karka fara yaba kyawun mijinta yanzun zata daina sauke girarta a gabanka. Wani irin kishin shi takeyi na ban mamaki, shisa duk idan taga zai fita haka take jin kamar baza'a waye safiyar ranar da ita ba saboda bacin rai. Da mutanen da suke mata kallon tana zaune a wannan tankamemen gidan tana kuma auren namiji kamar Bajjo sun san me take hadiya da ta daina basu sha'awa.

Ita a bakin yaran da ta haifa da cikinta ma bata ji zancen cewa Nawfal zaiyi aure ba. Yara kamar ba daga jikinta suka fito ba, yanda suke nanike ma Nawfal din yana bata takaici. Sai jiya da Julden zai tafi Abuja yace mata

"Gobe da safe za'a daura auren Bajjo"

Tambayar duk da tayi mishi kuma bata samu amsa ba. Haka ya tsallake ta ya wuce, son da take mishine abinda ya sata yi mishi addu'ar dawowa lafiya. Sai Adee ta kira, itace take fada mata kowa zai aura da inda suka hadu. Duk da bangare mafi rinjaye a zuciyarta na tare da bakin cikin kalar matar da ya samu, sauran karamin kashin yaji dadi da kuma fatan su karata can, ta rike shi karya dawo. Kar ya sake waiwayo su, inda yake ya zauna kamar Bukari, danma yanzun zamani ya canza ko ba'a ga fuskar juna ba za'aji muryoyi, da tace aji shi dif, ayi zaman makokin da babu gawa idan anyi cigiya an gaji.

Ya zamana sunan shi ma zaiyi ma kowa nauyin ambato kamar yanda na mahaifin shi yayi. Wannan shine fatanta, Nawfal yayi ma rayuwar ta da ta ahalinta nisa

Wannan karin ma kaddara ce ta riga fata
Kaddarar da take bibbiyar mutanen da ta kira ahalin ta da Nawfal din da ta zabi ta ware a cikin su
Bata sani ba
Bata san shi din haske bane a tare da su
Bata san shi zai zame musu katanga a lokacin da tarihi ya maimaita kan shi ba

"Sai da safe"

Julde ya fadi yana nufar kofa, hannu tasa tana share hawayen da ya zubo mata. Yana fita yaja mata kofar, a jagule yake jin zuciyar shi harya fice daga gidan, inda ya tsaya ya siyi lemon zaki yaji wani yace

"Mero!"

Sai da zuciyar shi ta nemi fitowa daga kirjin shi saboda tsallen da yaji tayi, da sauri ya waiga yana ganin yarinyar da bata wuce sa'ar Adeen shi ba da take tattare kwanoninta da alama abinci ta gama siyarwa a wajen, lumshe idanuwan shi yayi ya bude su

"Maigida ga canjin ka"

Mai lemon ya fadi, karba Julde yayi ya karasa motar shi ya zauna a ciki yana dora kanshi da abin tukin, har lokacin numfashi yake fitarwa cikin kokarin dai-dai ta bugun da zuciyar shi

"Naji maganganu kala-kala akan ka, wanda duk yake tunanin ya isa dani yace mun kar in aure ka... Ya zanyi da zuciyata Julde? Ya zan fito musu da ita su fahimci hakuri da kai baya cikin

zabin da nake da shi?"

Kalaman Mero suka dawo mishi kamar tana cikin motar a tare da shi, sake runtsa idanuwan shi yayi

"Na yadda kowanne rai da nashi kaddarar, kai ne kaddara ta Julde..."

Ya rasa yanda lokaci zai zama mai adalci kuma marar adalci a lokaci daya, yanda yake wucewa batare da ya jira kowa ba shine babban adalcin shi, amman yanda idan ya wuce baya dawowa kowa a wajen Julde hakan rashin adalci ne, ya zaiyi da kadan daga cikin kurakuren da yake jin zaiso ya sake samun aron lokaci dan ya sauya zabukan da yayi? Yau bama wani waje yake son komawa ba, rana daya ce, dakika ne kayadaddu a cikin ranar da zai sauya amsar da ya bama Mero, so yake ya kalleta ya fada mata ita ce kaddarar shi bashi bane kaddararta.

"Mero tayi aure"

Labarin ya riske shi shekaru hudu bayan rabuwar su, labarin da saida yayi yar karamar jinya a kan shi, hangota da wani, hango rayuwar da tayi da shi tana yinta tare da wani ba zai daina kassara zuciyar shi ba. Shi kadai yake dawainiya da ita a ran shi, ita ta shafe babin shi daga rayuwarta harta bude wani sabon shafin tare da wani. Bai tambayi a ina ko wa ta aura ba, abubuwan da yake gujema cikin sanin masu yawa ne. Da duk rana da yanda yake jin kusancin ta a zuciyar shi yana kuma jin nisanta da rayuwar shi

Da ya san kaddara ta adana musu shafin sake haduwa a titi daya da ya sauya tunani
In da yasan haduwar da zasu sake yi da Mero zata tono mishi abubuwan da za'a hada da rayuwar shi ta baya da ta yanzun a waje daya daya duba zabukan da yake da su

Dago kan shi yayi yana sauke wani irin numfashi ya tayar da motar fitilar ta na haske wajen har yana shirin kashe mishi idanuwan daya dan jima da su a runtse, sai da yasa hannu ya murza idanun, duk da haka ji yake hasken kamar yayi mishi yawa

Da yasan duhun da yake bibiyar shi watakila da ya nemi duk wani haske da zai iya kafin lokaci ya kure mishi
Kaddara
Kaddarar dai...
Ya baro tushen shi saboda ita
Tana biye da shi har wajen da yake tunanin ya boye mata

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan

IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

12

Bai san ko ya kamata ace yana jin shi wani iri tun safiyar ranar ba, da Julde ya kira shi yace an daura ma baiji wani abu ba. Wasu kance sunji su kamar suna yawo kan gajimare saboda farin cikin an daura musu aure. Shi baiji duk wannan ba, farin ciki, yana cikin shi tunda ya samu goyon bayan su Julde akan auren, na rana daya bai taba jin ba zai samu Murjanatu ba, sai dai in rashin tabbas na rayuwa, mutuwa ta raba tsakanin su. Shi da ita din basu fara soyayya lokaci daya ba, daya ganta in da ance zaiji wani abu a kanta, ko zai kirata matar shi wata rana zaiyi mamaki.

"Ka zauna mun a waje"

Shine maganar farko da tayi mishi a coffee shop din daya shiga cikin harshen turanci , an kuma hado mishi irin yanda yake so da kankaru a ciki. Ya zabi teburin ne saboda yana can lungu, kuma mai kujera biyu ne da ba lallai inka zauna kaga wani ya zo ya zauna kusa da kai ba. Harya hango yanda Coffee shop din zai zamana wajen zuwan shi duk rana. Yanda take kallon shi haka shima ya daga kai ya saka nashi idanuwan cikin nata, da yake lokaci ne na sanyi, shigar sanyi ce a jikinta, iya abinda yake gani na daga fuskarta ya gane ita din me kyau ce, kyau irin wanda zaka gani a kallo daya.

"Banga sunan kowa a wajen ba kafin in zauna"

Hannuwanta da babu safa ta murza kamar sun daskare mata

"I'm a regular a wajen nan. Kowa zai fada maka corner dina ce nan"

Ta karashe maganar da hausa wannan karin dan yayi mata kama da bahaushe

"Kaga karfin hali"

Ya fadi da fulatanci a muryar da yayi tunanin dai-dai kunnen shi ta tsaya

"Ba karfin hali bane ba, gaskiya ce"

Ta amsa shi da fulatancin tana ganin mamakin daya bayyana akan fuskar shi, dayar kujerar taja ta zauna

"Bafullatana ce ni, tunda kaji nayi hausa bai kamata kayi mamaki dan nayi yare na ba"

Dariya yayi, ba dan akwai abin nishadi a muryar ta ba, sai kwarin gwiwar ta da yanda take mishi magana kamar ta dade da sanin shi. Kamar ta san cewa ita da shi din ranar ne labarin su ya fara, sai da aka kawo mata abinda tayi order harda cookies ya gani sannan ta sake ce mishi

"Murjanatu Faruk"

Kai ya jinjina mata

"Nawfal Bukar"

Ba zaice sunyi hira ba, ta dai riga shi tashi daga wajen dan lokaci zuwa lokaci tana duba agogon da yake wajen, yanayin ta ya nuna cikin sauri take.

"Next time ka nemi wajen ka, this is my spot"

Dariya kawai yayi, kafin ma ya amsata tabar wajen. Ko da ya tafi ba zaice yayi tunanin ta ba, daga ranar ma zuwa safiya ko sau daya bata fado a ran shi ba. Watakila duk littafine da fina-finai ke zuzuta wannan kalar soyayyar. Sai ace idanuwa sun sarke cikin na juna shikenan har soyayya ta kullu, ko an gogi juna jiki da ruhi sun girgiza. Watakila kuma kaddara ta hada hanyar shi da Murjanatu ne dan su kafa tarihin da zai karyata wannan kalar soyayyar. Sunyi haduwa wajen goma bayan nan, ta shigo Coffee house din shi zai fita, ya shigo ita zata fita, banda gaisuwa babu wani abu da yake hada su.

Maganar su ta fara tsayine randa ta same shi zaune da sketch book dinshi yana nazarin wasu zanunnuka

"Kai Artist ne?"

Ta tambaya, zai tuna ya girgiza mata kai, kamar ba zai ce mata komai ba kafin ya amsa

"I'm a furniture designer, ko ince abinda nake karanta kenan"

Gabaki daya hirar su akan abinda yake karantawa ne har suka rabu. Zaice ita ta fara neman shakuwa da shi, ta fara neman alakar su ta wuce haduwa a Coffee Shop din bayan ta gayyace shi wani furniture showcase da za'ayi a cewarta baban dan ajin su ne a wajen ko wani bayani da ba zaice ya fahimta ba gabaki daya, an gayyace ta, ita kuma ta gayyace shi. Ya amsa ta da cewar zaije ta rubuta mishi lambar ta a takarda tana ajiye mishi sukai sallama.

Ranar ta bude musu sabon shafi, dan duk wani yunkuri da zaiyi sai ya gan su a tare a wani wajen, sai yaji kamar dama can ya santa ne, babu wata bakuntar juna a tare da su. Kamar yanda a cikin duk wata dariya da zasuyi ya fara jin ba ita bace ta karshe. A cikin shekara daya sunyi wani irin sabo da kalamai zasuyi karanci wajen fassara shi, dan a gidan su Murjanatu

babu wanda bai san shi ba, har idan an nemeta ba'a samu ba, yana cikin jerin abokanta da Mamanta ko babanta zasu fara kira suji ko suna tare ko kuma ta fada mishi inda taje.

Rana daya ya tashi da safe yaji baya son hango tana da kayadadden lokaci a rayuwar shi, baya son hango wasu ranaku a cikin rayuwar shi da babu ita a cikin su

"Ina son kasancewa da ke, fiye da abokanta"

Ya fada mata batare da shakku ba, ta dauki mintina biyar, har saida shirunta ya fara tsoro ta shi kafin ta dago tana saka hannuwa ta dauke kwallar dake cikin idanuwanta

"Na dauka ba zaka taba tambaya ta ba"

Tayi maganar muryarta na rawa

"Ka san tun yaushe nake son ka"

Kai ya girgiza mata, jin tayi shiru na sa shi fadin

"Wannan na da muhimmanci ne yanzun?"

Dariya tayi mai sauti

"Babu, kana jin yanda nake ji, shine a saman komai"

Daga nan suka fara, bai san a inda zasu tsaya ba. Ya dai san zai karasa sauran rayuwar shi tare da ita yana mata godiyar yanda ta yarda da shi da zuciyarta, da farin cikinta harda abubuwan da tasan shi kan shi bashida tabbaci akan su.

"Zan sauke ka gidan Daada ko in wuce?"

Khalid daya turo dakin ya fadi yana katse mishi tunanin da yakeyi

"Hamma mana, ba zaka dinga kwankwasa daki ba zaka shigo"

Dan karamin tsaki Khalid

"Har wanka na maka Bajjo"

Dafe kai Nawfal yayi yana fadin

"Inalillahi wa ina ilaihi raji'un"

Kafin ya dago ya kalli Khalid din

"Zan wuce wallahi ina da abinyi..."

Mikewa Nawfal yayi

"Da zan kara watsa ruwa ne"

Ganin yanda Khalid yaja kofar ya rufe yasa shi karasawa wajen kofar da gudu yana budewa

"Yi hakuri ka jirani in dauko jakata"

Dariya yayi ganin hararar da Khalid ya watsa mishi. Anan cikin falon Khalid yake tsaye yana jiran shi dan baiji shigowar Salim ba sai ture shin da yayi yana furta

"Tashi dalla"

Sake matsawa Khalid din yayi, dan Salim ya tsani ka tsaya akan hanya, ya dan fara rage saurin hannu da ya mare shi, ko kuma sun fara girma ne a idanuwan shi, Khalid din ba zaice wanne bane a cikin biyun, dakin shi Salim ya wuce yana rufo kofar, dai-dai lokacin da Nawfal ya fito yana janyo tasu kofar dakin

"Uban me yasa zaku dinga jan kofa kamar zaku rabata da mazaunin ta? Me yasa ba zaku rufe a hankali ba?"

Salim ya leko yana fadi a masife, har kanshi saida ya sara da yanda yaji karar rufe kofar da Nawfal yayi. Ko inda Salim din yake babu wanda ya kalla a cikin su, sauri ma sukayi suna fita daga dakin, Khalid ne karshe, yana sane ya buga kofar da zai rufe

"Khalid!"

Yaji muryar Salim din, sauri suka kara suna dariya, yasan koya dawo ba zai mishi magana ba tunda ba son surutu yake ba. Zai dinga binshi da harara ne, ba ma zai zauna a falon ba sam, dakin shi zai shige yana dawowa, Nafwal zai kwana gidan Daada.

*

Gabaki daya hankalin ta yana kan littafin da take karantawa, novel ne na James Hadley Chase mai suna (A coffin from hong kong). Abincin da ta zuba har yayi sanyi saboda gabaki daya bata san abinda yake faruwa a wajen duniyarta ba. Tana son litattafan mutumin, har mamakin irin fasahar da yake da shi takeyi. Guda goma Salim ya kawo mata a lokaci daya, kamar tayi me dan murna ranar. Cancana su takeyi, bata karantawa sai ranakun karshen mako, ta dauki guda daya ta karanta a ranaku biyun.

Yanzun ma Daada ta daina mata magana kan karatu, a cewar ta

"Bakina ya gaji da surutu Madina, in shaa Allah ba zan kuma ba, in dai akan wannan litattafan ne, ace abinci ma ba zaka natsu kaci shi ba"

Tana kuma kokarin kyautata maganar tata, idan Madina ta kula da ita ne, sai ta ajiye ta dan kara tsakurar abincin ta mayar ta ajiye. To yau tunda Salim ya dawo da ita daga restaurant din can, sallah ce kawai abinda yake tashin ta daga inda take. Littafin saiya rage mata yanayin da ta shigo gidan da shi, yanzun ma isha'i take jira a kira tana da alwala in tayi ta shige dakinta. Shisa sam bata ji shigowar Nawfal ba, balle sallamar shi. Sai hannun shi da ya sa yana yin kasa da littafin nata ta gani, a hankali ta dago suna hada idanuwa ta cikin gilashin ta

"Hamma..."

Ta kira da sanyin muryar da Nawfal yaji yayi mishi tsaye, littafin ya zare daga hannunta, babu gardama ta sakar mishi, duba sunan yayi

"Da dadi?"

Ya tambaya, ta jinjina mishi kai

"Sosai ma... Bansan zaka zo ba. Me zaka ci?"

Dan jim yayi

"Ki bani shayi kawai, bana jin yunwa"

Mikewa Madina tayi tana shiga kitchen din, ta san yanda yake son shayin shi, babu bata lokaci ta hado mishi, kafin ta gama tana jin muryoyin su shida Daada data fito daga daki, tana fitowa ta mika mishi

"Ka sha ko sikarin yayi maka kadan"

Karba yayi yana sake juyawa da cokalin da yake cikin kofin kafin ya kurba

"Ki karamun Milo kawai ko cokali daya"

Cewar Nawfal yana mika mata kofin shayin. Karo mishi tayi ta dawo tana bashi, ta dauki plate din abincin da tasan ba ci zatayi ba ta mayar da shi kitchen, sanda ta dawo ana kiran sallar isha'i, shisa bata zauna ba ta nufi dakin ta. Nawfal ma mikewar yayi, ya shiga kitchen ya bude fridge ya saka kofin shayin yana fita masallaci. Sanda ya dawo babu kowa a dakin, kan kujerar da land-line din Daada take gefe a ajiye ya zauna yana janyowa, lambar Murjanatu ya kira tana

dagawa yace ta kira shi, saboda yasan zaifi sauki daga can akan ya kirata daga nan din

"Jaan..."

Ya kira yana jin yanda yayi kewar ta

"Ina missing din ka sosai"

Murmushi yayi

"Kan ki kawai kika sani"

Yana jin dariyar ta cikin kunnen shi, sautin na nutsar mishi da zuciya yana saka shi sake shigewa cikin kujerar

"Na kira Hamma yace mun kana gidan Daada, nace ba kai nake nema ba na kira ne in gaishe shi..."

Wannan karin shi yayi dariyar

"Bai yarda ba ai, yace yaji dadi dana kira saboda yana so yayi magana da ni daman. Yan uwan suna son ka Gidado"

Ta karasa da sunan da takan kira shi a lokaci irin wannan, idan tana jin tsokana zata kira shi da Bajjo tun ranar da taji Khalid ya kira shi da hakan.

"Na sani, na san hakan Jaan"

Nawfal yayi maganar batare da shakkun komai ba, yana da cikakkiyar yarda akan soyayyar da take tsakanin shi da yan uwan shi

"Hamma yace in kula da kai, yace kar in cutar da kai, zai bada shaida ba zaka taba yin abinda zai basu kunya ba..."

Wani abu Nawfal yaji ya tsaya mishi a kirji, Khalid, Khalid daban ne a wajen shi.

"Zan so ace nayi recording din kiran kaji kalaman shi idan ka dawo, ban rike gabaki daya ba saboda ina ta share hawaye, ya karya mun zuciya da yawa"

Dariya Nawfal yayi, shima tashi zuciyar rawa yaji tana yi

"Ke komai abin kuka ne ai"

Yanayin yanda yayi maganar yasa Madina da ta fito juyawa zata koma dan tasan dawa yake magana, ta kuma san yana bukatar kasancewa shi kadai dan ya sake da matar shi, amman sai taga yana daga mata hannu cikin nuni da ta karasa inda yake din

"Jaan ga Madina zaku gaisa"

Ya fadi yana kallon Madina da take kokarin ware mishi kananun idanuwan ta, nunin dai ya sake mata da hannu yana kiranta, dakyar ta karasa ta karbi wayar tana furta

"Hello..."

Cikin yar karamar murya

"Madina, ya kike?"

Murjanatu ta fadi ta dayan bangaren, yanayin hausarta kawai ya isa bama Madina tabbacin yar gayu ce, dan yanda ta ajiye kowacce kalma harda sunan Madina din cikin ba kowanne harafi hakkin shi zai tabbatar maka da hakan, ga muryarta ma

"Alhamdulillah, ya kike kema? Ya aiki?"

Dariya Murjanatu tayi

"Lafiya kalau, aiki da karatu duka. Ya naki?"

Saida Madina ta gyara gilashin ta sannan ta amsa tana sauke numfashi

"Ban sanki ba, amman na san Hamma, in ya yarda kin zama matar shi, muma mun yarda da kasancewar ki a cikin mu. Dan Allah ki kula da shi"

Maganganun suka kubcewa Madina batare da tayi wani tunani ba

"In shaa Allah, shima kice ya kula dani, ku daina son kai haka"

Kai Madina ta jinjina tana murmushin da batasan me yasa yake bude wani abu a kirjinta ba

"Zan fada mishi shima.. Mungode sosai"

Ta amsa tana mika ma Nawfal wayar batare da ta jira amsar Murjanatu ba, shima bata bari sun hada ido ba, dan haka kawai take jin idanuwan shi na shiga cikin nata zata iyayin kuka. Gashi suna daki daya amman tana jin yayi mata wani irin nisa. Karasawa tayi kan kujera ta dauki littafin ta sannan ta wuce daki tana maido kofar ta rufe a hankali.

*

Wannan karin jirgin shi na karfe hudu ne, tunda safe yaje gidan Daada sukayi sallama, abinda yake gudun saida ya faru, tana ta kuka kamar wanda zaiki dawowa, dan wannan karin duk yanda yace mata zai dawo yana ganin rashin yarda shimfide akan fuskarta. Haka ya dawo duk ta kashe mishi jiki, bacci yayi zuwa azahar, yana tashi ya fara shisshirya kayan shi ya watsa ruwa, ya sake kaya kenan yana taje sumar kan shi aka kwankwasa dakin

"Shigo"

Ya fadi dan a tunanin shi ma Lukman ne, sai yaga Salim daya shigo dakin gabaki daya yana mayar da kofar ya rufe. Lokacin Nawfal yaga yar jakar da take hannun Salim din, mika mishi yayi, da mamaki yasa hannu ya karba

"Na matar ka ne, ka kira mun ita"

Murmushi Nawfal yayi yana kallon Salim din, kafin ya ajiye jakar a gefen shi, wayar Khalid na wajen shi, dan haka ya mike yana duddubata akan gadon ya dauko. Babu bata lokaci ya kira Murjanatu da yasan tana tare da wayar dan yace zai kirata kafin ya fita daga gidan

"Harka gama shiryawa?"

Ta fadi bayan ta daga

"Zaku gaisa da Hamma Salim ne, ina kanyi"

Nawfal ya fadi yanajin yanda harshen shi yayi nauyi a gaban Salim din, wani abu kamar kunya na son lullube shi, mika mishi wayar yayi ya koma ya zauna, yana jin suka gaisa kafin Salim din ya dora da

"Bajjo yace miki bana magana da yawa ko?"

Baisan me Murjanatu tace ma Salim din ba, amman yasa yayi dan murmushi

"Nasiha ya kamata in miki, amman banda wasu kalamai masu yawa. Bajjo bashi da matsala, shine mutum daya marar matsala dana sani, ba don yana kanina ba. Yana da karancin shekaru amman ba yaro bane ba, yana da hankalin da zai rike ki da kyau. Karki cutar da shi, shine kawai abinda zan fada miki, ba kashe di bane ba, roko ne, kece zaki zama mutum ta farko dana roka alfarma, ki rike mun kanina da kyau"

Salim ya karasa cikin sauke muryar da Nawfal bai taba ji a tare da shi ba

"Allah ya sa muku albarka a zaman ku ya tabbatar muku da alkhairi"

Saida ta amsa tukunna ya mika ma Nawfal wayar yana ficewa daga dakin. Da dukkan zuciyar shi yake addu'a tun da aka fara maganar auren, addu'ar da rabon daya zauna yayi irinta harya manta. Saboda hayaniyar dayake gani a cikin auren Julde da Saratu baya son ta kasance a tare da Nawfal, rayuwa da tayi kason tashin hankali a faranti Nawfal baiyi hankalin da zai dauka ba, miko mishi kason shi tayi da kanta ya karba saboda bashi da wani zabi. Baisan duka labarin Nawfal ba, amman yasan me yake faruwa da shi a zaman da yake a cikin gidan su, idan shine bashi da yakinin zuciyar shi zata dauka.

Shisa ya roki Murjanatu, idan bata samar mishi da nutsuwa ba baisan me zai faru da yaron ba. Yanata tunanin kyautar da zai basu, sai shekaranjiya yaga wani bracelet na azurfa a hannun wata yarinya a makaranta, yayi mishi kyau shisa ya tambayeta inda ta siya, tace mishi yayanta ne yake siyarwa, basu rabu ba saida ta kira masa shi sukayi magana ya fadi abinda yake so a rubuta a jiki, da yake aikin cikin saurine sai da ya kara mishi kudi, an kuma yi masa shi yanda yake so. Dakin shi ya wuce yana daura alwalar la'asar, raka Nawfal airport ne abinda ya dawo da shi daga gidan.

Nawfal kuwa inda Salim yabar shi nan ya zauna, ya rasa inda zai sa zuciyar shi ya rage emotions din da yake ji. Dakyar ya iya yin alwala ya fita masallaci. A sujjadar shi, a karo na farko ya roki Allah da karya ba Saratu nasarar raba shi da yan uwan shi, yaranta ne ya sani, amman Allah yake roko daya saka mata salama a zuciyarta ta taimaka mishi ta raba su tare da shi, karta raba su, kome take mishi yana yafe mata, in tayi wannan ba zai iya ba, ba zai taba yafe mata ba saboda suna da muhimmanci na gaske a rayuwar shi.

Har kasan ran shi yaji sanyi daya ga bangaren Saratu a kulle, da alama bata nan, har sauri yake wajen dauko jakar shi dan subar gidan kafin ta dawo, duka haduwa biyu sukayi tunda ya dawo kasar, bayason suyi ta uku, baya son ya tafi da wasu cikin maganganun da yasan dole saita fada masa su. Ai kuwa har Khalid ya zo ya shigo motar, Salim ma ya fito bata dawo ba, ajiyar zuciya ya sauke har Khalid na kallon shi.

Da yake babu wani isasshen lokaci kusan a gaggauce suke sallamar

"Baka dai manta komai ba ko?"

Julde yake tambaya

"Babu abinda na manta Daddy, kayan babu yawa ai"

Kai Julde yake jinjinawa

"Na kara maka kudi, in dai kana bukatar wani abin ka kirani kana ji ko?"

Sau hudu yana kara mishi kudi kenan, saboda gani yake kamar zasuyi mishi kadan, baya so

yaje yana manejin komai ga yarinyar mutane, yanda danginta suka karamma shi a Abuja ba zai so ace Nawfal baya rike musu yarinya da kyau ba, babanta ma kusan sau hudu suna gaisawa, uku daga ciki duk shi ya kira Julden, basu da matsala ko kadan ya kula, mutane ne su masu karamci da saukin kai, duk kuwa da tarin arzikin da yaga Allah ya wadata su da shi, bai saka musu girman kyau da kyamar mutane ba, ko Kawun Murjanatun yaga yanda yake faran faran da ma'aikatan gidan na shi kamar wasu abokan shi.

"Daddy kudin ai yayi yawa, da gaske ba wani abu nake siye ba, kuma nace maka ina aiki"

Kallon shi Julde yayi

"Ka tsayar da hankalin ka kan karatun ka, da zaka ajiye wannan aikin ma zaifi"

Dariya kawai Nawfal yayi, yanda duk zai ma Julden bayani yasan ba zai yarda ba, tsadar rayuwa acan kawai in baka da lafiya ne, ganin likita da magungunan su akwai tsada sai kuma kudin haya, amman abinci kowanne mazaunin New York ko wanda ya taba kai ziyara zai fada maka babu tsadar kayan ciye-ciye. Karasawa yayi kawai yana hugging din Khalid da Julde, bai ma fara nufar Salim ba. Shi din dai ya kara so ya karbi akwatin Nawfal din yana dan yin gaba, sallama ya sake yi wa su Khalid ya karasa inda Salim din yake

"Ka kula musu da yarinya Bajjo, kai kace zaka aure ta. Karka bani kunya"

Murmushi Nawfal yayi

"Ita rokonta naji kayi Hamma"

Babu wasa a fuskar Salim yace

"Kai kashedi ne nake maka"

Hannu Nawfal ya daga cikin alamar salute yana saka Salim din girgiza kai kawai ya mika mishi akwatin shi ya juya

"'Hamma..."

Ya kira, juyawa Salim yayi, hannu Nawfal yasa akan kirjin shi inda yake tunanin zuciyar shi take yana ganin Salim din ya sake bata rai

"Nagode"

Ya fadi a hankali, yasan baiji sautin muryar shi ba, amman ya karanci godiyar akan labban shi. Bai daiyi magana ba kamar yanda yayi tsammani ya sake juyawa. Salim yana da wahalar fahimta, kullum nuna musu yake rayuwar shi yasa a gaba, bai damu da harkar kowa ba, amman

a cikin kananun shiga harkokin su da yakeyi yana nuna musu cewa yana tare da su duk runtsi, zasu kuma iya jingina da shi a duk lokacin da bukatar hakan ta taso, amman su tsaya da nasu kafafuwan shine abinda zaifi son gani

"Allah ya kula da kai Hamma Am"

Nawfal yayi addu'ar cikin zuciyar shi, yana sauke numfashi, inda wani zaigani zaiyi tunanin Nawfal ya leka wasu a cikin shafukan da kaddara ta tanadarwa Salim

Kamar yaga yanda yake bukatar addu'ar
Kamar yasan kurar da take tunkaro rayuwar shi bata wasa bace ba

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com

*RAI DA KADDARA 1*

13

Kan wayar Madina ta maida mazaunin shi tana mikewa, dakinta ta wuce tana sauko karamar hijab, riga da wando ne a jikinta, rigar sai a saka irinta su hudu kafin su cikata, takalman kafarta wasu manya ne da Daada bata san inda ita da Julde suka nemo su ba, amman masu gashine, kamar ma kan kaza-kaza take gani daga karshen takalman dan harda yan idanuwa daga jiki, da tayi magana randa ta fara ganin Madina na yawo da su a cikin gida dariya tayi

"Guda biyu ne, in dauko miki dayan Daada, zaki ji dadin shi, ga laushi, kuma yana da dumi"

Kai ta girgiza

"Allah ya tsare ni, ke dai kiyita fama"

Ai kam kamar ta dauki shawararta, in dai tana cikin daki to da wahala kaga kafafuwanta babu su, ga safa ga wannan takalman.

"Zan ga Hamma a waje"

Ta fadi tana kama hanya batare ma da ta jira amsar da Daadar zata bata ba. Da ido kawai Daada ta bi Madina harta fice. Bata son kawo komai a ranta akan Madinar da Salim, amman

kullum sai yazo, shi yake zuwa ya dauko ta daga makaranta, kuma da yamma idan bai zo ba to dai-dai irin lokacin nan zaka gan shi. Da yawan lokutta takan dawo da ledoji yayo mata siyayya, tayi fata kala-kala a baya da bai kasance ba, ba zatayi wani akan Madina da Salim ba, koma menene yau da gobe zata nuna.

Madina da ta fita motar Salim ta bude ta shiga tana mayar da murfin ta rufe hadi da sauke numfashi, jikinta har bari yakeyi. Bata taba tunanin zata iya boyewa Daada halin da take ciki ba sai yau, saboda wani abu da zaisa tayi hakan bai taba faruwa ba. Asalima bata san ta kwana da wani abu a ranta ba sai bayan auren Nawfal, haka kawai zata nemi bacci a lokacin da ta saba yin shi ta rasa saboda yanda tunanin shi yake damunta, da yawan ranaku takan labe bakin kofa a dai-dai lokacin da yake kiran Daada taji ringing din wayar sannan ta koma ta kwanta.

Zuciyar ta kan raya mata ta fita ta karbi wayar su gaisa, amman sai kafafuwan ta su kasa fitar da ita, tana daukar abin zaiyi sauki lokacin da awanni suka shude a cikin ranaku, amman a hankali wannan ranakun suka dinga tafiya da satikan da suke cikar watanni har shekarar da take ganin kamar ta rufe ido ne ta bude. Yanayin bai barta ba, amman ta saba da shi, ta dai kasa samun amsar dalilin da yasa take jin nisan da yake tsakanin su ya ninka na da. A gefe daya kuma Salim ya zame mata wani bango da take jingine da shi batare da fargabar komai ba.

Duk sanda take da wata bukata sai ta ga Salim tsaye a gabanta yana kallon ta kamar in har yana tare da ita babu wani abu da zatayi kukan rashin shi, tasha tsinto kalmomi biyu a litattafai 'comfort zone' tare da Salim take ganin asalin ma'anar kalaman, dan kamar shi din da matsayin shi a rayuwar ta bature ya kalla ya kirki kalaman. Shisa yau da ya zama rana ta farko da tashin hankali ya fara yiwa rayuwarta sallama ya zama mutum na farko da take son rugawa wajen shi.

Safiyar ranar alhamis din tazo mata a birkice tun bayan zuwanta makaranta suka kuma juyo sakamon rasuwar Malami a makarantar, ba bangaren ta yake koyarwa ba, amman mutuwar ta daketa, sai take ta ganin fuskar shi, ta daiji dadi daya kasance musulmi saboda ko bakomai mutanen da zasu roka mishi gafara a wajen Allah kuma addu'ar ta same shi suna da yawa, a cikin su harda ita kuwa. Da yake ta saba tsara ranarta, sai lokacin ya zame mata wani abu da bata san me zatayi da shi ba.

Shisa ta tsiri yin kwalema, share nan, goge can, lokacin da taje dakin Daada ta sameta ta gama shiri wai zataje jaje nan makota in da yaro ya sa kafa cikin tuwon da aka kwashe a kwano ya kone. Bayan ta Madina tabi tana kulle gidan, tasan gidan da Daada take magana, akwai mahaifiyar maigidan da take zaune tare da su, kusan kawaye ne ita da Daada din, Madina tasan in ta shiga zasu zauna ne suna ta hira, gara ta kulle gidan kafin wani ya fado mata.

"Ko da ba zan dade ba kece fa, zan ga yanda zakiyi da tsoron nan in kikayi aure"

Daada ta fadi cike da zolayar da ta saba yi mata duk sanda zata fita. Dariya kawai tayi, tsoro ai halal ne ko a musulunci babu inda ta ga an haramta shi har yanzun da take zuwa Islamiyya. Bata san ko a gaba ba, in ba nan gidan su ba, batajin akwai gidan da zataje abarta ita kadai a

ciki ta zauna. Tunda Allah yayi mata tsoro, sai ta ga kamar wani zai shigo ya yankata kafin tayi ihun da za'a aji har a kawo mata dauki. Ko da ta koma dakin Daada ta nufa tana cigaba da aikinta

"Yanzun ji tarkacen da yake dakin nan, amman na dakina take gani"

Madina take tsegumi tana janyo wata tsohuwar butar tangaran mai murfi, bambanci dakin Daada da nata bata ganin yana da wani yawa, kawai ita Daada komai a kammale yake, ita kuma nata a barbaje suke. Zama tayi tana bude butar dan ganin meye Daada ta ajiye a ciki, zazzage butar tayi a kasa tana murmushi ganin harda wasu kudin karfe irin na da, ta dauka ta duba, da wani hoton fasfot, duk da babu kala a jikin shi kuma ya tsufa sosai bai hanata ganin kamannin mutumin da na Julde ba, wata irin kama ta ban mamaki.

Ajiyewa tayi a gefe tana daukar wata takarda da saboda tsufan da tayi har ta fara ja, ga wani maikon ajiya da yake jiki kamar an tsoma cikin mai an fiddo. Zaman gilashin ta da ta gyara baisa ta ganin rubutun da kyau ba bayan ta bude takardar, tashi tayi tana sake kunna dayan kwan dakin dan ta ga haske sosai:

Daada,

Ku saka mata Munawwara, ku kira ta da Madina. Watakila albarkacin sunayen biyu rayuwar da bata da zabi a kanta ta zo mata da sauki ko yaya ne. Zan so kaina a karo na biyu, ku fada mata mahaifiyarta ta sota a watanni taran zamanta a cikinta, ko ba zata yarda ba Daada ki fada mata ta yafe mun, ki bata hakuri na yanda zata kare sauran kwanakin ta a duniya tana biyan zunuban mahaifanta. Kuma ku fada mata sunan baban ta Kabiru, yanayin haihuwar ta ba zai canza cewa ita din jinin shi bace ko da bata da gadon shi. Ke ma ki yafe mun, kiyi mun addu'a ko da rayuwa ba zata sake hada fuskokin mu ba.

Yelwa.

Ta karasa karanta suna da ya zama karshen rubutun da yake jikin takardar, a karo na farko tana tabbatar da yaren hausa bashi bane asalin ta saboda yanda rubutun da akayi a cikin harshen ya birkita mata kwakwalwa yana sa ta kasa fahimtar shi kai tsaye, sake karantawa tayi, wannan karin a zaune, zaman da bata san lokacin da tayi shi ba, kamar yanda har zuwa yanzun ba zata ce ga adadin yanda rubutun da yake jikin takardar da zata zama mafarin budewar abinda aka dade ana boye mata ba ya dawo mata. Ta haddace kowacce kalma, ta dai rasa ma'aunin dora nauyin da sukayi mata.

Da rarrafe ta karasa ta kwashe kayan da ta zazzago tana mayar da su cikin butar banda takardar da ta ninke. Butar ma mayar da ita tayi inda ta dauko, har ta karasa share dakin, ta koma nata ta bude littafi ta saka wasikar ba zata ce ga abinda take ji ba, ko me tunaninta yake so da ita ba, saboda yaki daukarta ya kaita ko ina. Murmushi take tana jin kamar ba fuskarta ba, amsa hirar Daada take tana rasa daga inda kalaman suke fito mata, duk idan sautin muryarta

ya koma cikin kunnuwan ta sai tayi mamakin yanda bai fito da alamar tambayar da tafi kowacce yi mata yawo cikin kai ba

"Wacece Yelwa?"

Kusan har ihun wata murya take ji cikin kanta da wannan tambayar, amman yanda akayi bata sakko daga kan nata zuwa makoshinta ba abin mamaki ne. Har girki tayi, duk wani abu daya kamata ace tayi saida ta gudanar yau, wajen karfe biyu da rabi wayar dakin Daadar ta hau ruri, da yake Daada ce a kusa ita ta amsa tana yin jim hadi da fadin

"Lafiya kalau Salim, gata nan a kusa ma"

Ta karasa tana mika ma Madina kan telfon din

"Mug..."

Salim ya kira ta dayan bangaren, muryar shi da taji, da yanda ya kira sunan daya makala mata kamar yasan tana boye wani abu yasa taji gwiwoyin ta sunyi sanyi, zuciyarta ta karye

"Hamma"

Ta amsa tana yin gyaran murya jin maganar ta fito daga kasan makoshin ta

"Kana makarantar mu ko? Banyi tunanin kiran ka ba sam, kayi hakuri"

Tana jin yanda ya sauke numfashi a kunnen ta

"Zanyi abu yanzun, ban san lokacin da zan gama ba, amman zan zo in ganki"

Kai ta jinjina kamar yana ganin ta

"Allah ya taimaka, sai kazo"

Ta san ba wani abu zai sake cewa ba shisa ta mika ma Daada kan telfon din da ta mayar mazaunin shi. Yanda zuciyarta ke karyewa ne yasa ta mikewa tabar falon. Kwanciya tayi har la'asar. Da ta fito taji ko Daada na marmarin wani abin ta dafa mata tace mata a'a daki ta sake komawa. Ba zatace ga abinda take ji ba, lokacine dai yaki yi mata sauri har zuwa yanzun da take cikin motar Salim inda ta hada kanta da gaban motar tana sauke numfashi. Wasu abubuwa da bata san suna daure a jikinta ba take jin suna kwancewa a hankali yanzun.

"Madina..."

Salim ya kira ganin yanayin ta. Ta kasa dagowa, numfashin ta da take jin daidaton shi ya kwace

mata take son nutsarwa

"Madina"

Salim ya sake kira yana jin zuciyar shi na dokawa, bai taba ganin ta yanda yake ganin ta yanzun ba, tunda rana da ya kira yaji kamar yanayin muryata ya canza, baisan yanda zai tambayeta ba shisa yayi shiru, amman tana rashin tun lokacin, kawai akwai abinda yake dubawa ne saboda jarabawar shi ta karshe da take gabatowa. Danma yajin aikin da akayi ta fama da shi, da sun manta da gama wannan wahalar. Hannun shi ya kai yana dan bubbuga kafadar ta

"Hey Mug"

Ya fadi cikin wani irin sauke murya da baisan ya iya ba, lallashi ba sabon shi bane ba, ko su Khalid idan yaga alamar wani abu na damun su, karshen abinda yakeyi shine ya fita ya siyo musu wani abu da yake tunanin suna so yazo ya basu, in a falo suke ya zauna da su har sai sun tashi sun bashi waje, idan a dakin sune zai ta tsayuwa har saiya tabbatar idan ya tafin babu abinda zai same su, ko a fuskar su yaga alamar suna son ya tafin. Ko Saratu da ya sha shiga bangaren su ya jiyo sautin kukanta duk da kofa a kulle take bai taba kwatanta shiga ba.

Zai tsaya daga inda yake zuciyar shi na wani irin ciwo da ba zai fassaru ba har saiya daina jiyo sautin kukan nata sannan zai tafi. Shisa yanzun yake addu'a ba kuka Madina zatayi ba, tunda baisan yanda zaiyi da ita ba, zai sake magana ta dago tana gyara zamanta, da yake ya kunna fitilar cikin motar yana ganin fuskarta fayau, babu alamar kuka tayi, yana dai so yaga idanuwanta ne yau, shisa ya mika hannu yana zare gilashin dake fuskarta, sai idanuwan nata suka kankance mishi, kamar ta cikin gilashin sun fi haka girma.

"Idanuwa ne haka Madina?"

Sai da murmushi ya kwace mata duk kuwa yanda take jin zuciyar ta, Salim na da wannan tasirin a tare da ita, hannu ta mika tana karbar gilashin ta

"Bana gani da kyau Hamma"

Ta fadi tana mayarwa ta gyara mishi zama, takardar da take hannunta ta mika mishi, da mamaki ya karba yana warware wa, kallon Madina yayi ta dan daga mishi kai cikin alamar ya karanta, bai kuwa yi musu ba ya karanta din kafin ya raba idon shi da takardar yana kallon Madina da ta dan daga mishi kafadu

"Mama na ce ko?"

Tayi tambayar da taji tsoron furtawa har a cikin kanta tun safe, Salim na ganin firgicin da yake cikin idanuwan ta

"Madina..."

Ya kira da wani yanayi da yasa ta kai hannuwa tana rufe fuskarta hadi da furta

"Inalillahi wa ina ilaihi raji'un"

Shi kan shi kalaman cikin wasikar ne suke mishi yawo, yana harhada ma'anar su. Baije islamiyya kamar yanda su Khalid suka ba, tunda har yanzun yaga Khalid na zuwa, amman yayi zuwan da ya fahimci kalaman Yelwa a cikin wasikar '...Yanayin haihuwar ta ba zai canza cewa ita din jinin shi bace ko da bata da gadon shi'

"Madina"

Kawai ya iya sake furtawa a karo na biyu yana son ya rungumeta a jikin shi, dan hakan ne hanyar lallashin da ya fara zuwa kan shi, sai dai kafin yayi wani yunkuri ta bude fuskarta tana kallon shi

"Ya zan koma baya Hamma? Ya zan koma lokacin da banga takardar nan ba? Ya zan koma in mayar da ita in jira sai lokacin da Daada ta ga ya kamata in sani ta fada mun da kan ta?"

Sosai take kallon shi tana son ya taimaka mata ko zata daina jin wani abu na budewa a cikin kirjinta, ko tarin tambayoyin da suke mata yawo zasu daina, idan tace bata tunanin su waye iyayen ta zatayi karya, a duk wani PTA meeting na makaranta sukan fado mata, a lokuttan da za'a bayar da wata takarda da sunan iyaye su saka hannu sai Julde ne zai saka mata tunanin me ya faru da su kan zo mata. Bata tambaya bane saboda tasan idan lokacin ta sani yayi za'a sanar da ita.

Ko da wasa bata hango sanin zai iya zo mata da hargitsi irin wannan ba, idan Yelwa mahaifiyar ta ce tana ina? Ba rasuwa tayi ba kenan? Kamar yanda tunanin ta ya sha ba ta, shisa Daada bata maganar ta, zafin rashin ne yake taba ta har zuwa yanzun. Wanne son kaine tayi a karo na farko idan tsallakewa ta barta ne na biyu? Da sauri ta fisge takardar dake hannun Salim tana sake duba wani layi da sai yanzun ma'anar shi take bude mata, yanda ta dago ta kalli Salim ne ya tabbatar mishi da sai yanzun ta gane, ta gani amman sai yanzun ta gane, takardar ya karba ya ninke yana kamo hannunta ya saka a ciki

"Koma menene, ina nan, kina jina, ina nan tare dake"

Kai take daga mishi tana jin hawayen da suka cika idanuwanta suna zubowa

"Kin gani, babu yanda zaki goge ganin da kikayi, idan nace miki komai ba zai canza ba zanyi miki karya"

Kamar yanda baima san me yake ce mata ba, kalamai yake nema, kalaman da zasu tausasa abinda yake tunanin tana ji a zuciyar ta, shisa ya kama dayan hannun nata yana rike shi da nashi, kamar hakan zaisa damuwarta ta koma jikin shi, zuwa lokacin kuka takeyi marar sauti, amman duka jikinta bari yake saboda tashin hankali, bata da gadon babanta, idan bata da gadon shi hakan na nufin ita din ba ta hanyar daya kamata aka same ta ba.

"Kana jinta... Ban.. Banda gadon Baba na, kaji me tace Hamma"

Ta san sunan shi Kabir, tunda da shi take amfani a makaranta, hakan ne ma ya sa ta gane ba Julde bane baban ta, ita da Nawfal ta san bashi ya haife su ba, shi yana amfani da Bukar ita tana amfani da Kabir. Kwance seatbelt din shi Salim yayi yana gyara zaman shi yanda zai rike hannuwan ta sosai, so yake ya hadata da jikin shi

"Madina ce"

Zuciyar shi ta fada mishi kamar harda gargadi a cikin yanda tayi maganar

"Lallashin ta zanyi"

Ya amsa zuciyar tashi a hankali, sai dai anya zai tsaya iya lallashi? Ba tun yau yake son jinta a jikin shi ba, ba tun yau suke zama a mota yake duk wani kokari da zai iya na ganin ko da hannunta ne bai rike ba. Ko mace ya raba da kirjin shi zai fara tunanin yanda zai kasance idan Madina ce, ya rasa lokacin da hakan ya fara, kawai tsintar kan shi yayi a tsakiya, ya kuma rasa yanda zai ya fita. Yanzun ma da hannun ta yake cikin na shi yana jin dumin shi har kasan ran shi. Idan ya rike ta a jikin shi ba zai taba tsayawa a lallashi ba ya sani.

"Baki sani ba Madina, karki fassara duk abinda kika gani a cikin rubutun nan, zai iya nufin komai, kar mu ce zamu bashi fassara daya, umm?"

Ya karasa yana dan jan hannun ta da take kokarin zamewa, bai kokarin hanata ba, hawayenta ta goge tana jinjina mishi kai, so take ta yarda da shi, kalaman shi su zame mata igiyar da zata kama dan jinta take cikin wani irin rami, ko bata fito ba, ya zamana tana rike da igiyar, hakan zaisa taji kamar tana da zabi a fitowa daga ramin.

"Ki mayar da takardar nan inda kika dauka, ki jira Daada, ki jira ta fada miki da kanta"

Kai take jinjina mishi, yana ganin yanda kalaman shi suke zauna mata

"Kirjina yana mun ciwo"

Ta fadi wasu sababbin hawayen na zubo mata, sosai yarintar da take tare da Madinar ta bayyana a yanayin yanda tayi maganar da kukan daya kwace mata bayan hakan, lumshe idanuwan shi Salim yayi yana sake bude su a kanta

"Kukan ne bana so ai, zai bari idan kika daina..."

Hannu tasa ta goge hawayen ta, kara matsawa Salim yayi yana kama hannun nata yayi amfani da shi wajen kara goge mata fuskarta, tsoron ya kai nashi jikin kuncinta kai tsaye yakeyi

"Idon zai kara kankancewa, ki rufa mana asiri Madina"

Dariya tayi mai sauti, duk da ta sake hadowa da wani kukan, shima dariyar karfin hali yayi, gabaki daya wani iri yake jin shi

"Kin ci abinci?"

Ya tambaya bayan ya koma ya gyara zaman shi akan kujerar, kai ta daga mishi

"Tun dazun"

Duk da bata gane kan abincin ba taci, saboda bata so Daada tayi mata magana, ko ta tambayeta mai yasa bata ci abinci ba. Yanda Madina take kallon shi yasa shi fadin

"Kina son wani abin muje mu siyo?"

Kai ta girgiza mishi

"Littafi?"

Dariya tayi

"Da gaske nake yi"

Kai ta girgiza mishi

"I will be fine..."

Ta fadi da wani irin sanyin murya duk da bata jin zatayi dai-dai din

"Karki yi mun karya, bana so, kar ki fara boye mun kina jina?"

Da sauri ta daga mishi kai

"Dare yana yi, ki koma gida, da safe zan zo in kaiki makaranta In shaa Allah..."

Murfin motar ta bude ta sauke kafafuwan ta a waje

"Mug"

Ya kira, juyawa tayi da murmushi a fuskar ta, haka yake son gani, murmushin nan, ko kadan bayason yaga fuskarta babu shi

"Komai zaiyi dai-dai, kina jina, ko babu su, kina da mu, mu kadai ne daman, tuntuni mu kadai ne, kar tunanin su ya dame ki da yawa"

Numfashi ta sauke

"Mu kadai ne daman, tuntuni mu kadai ne"

Ta maimaita cikin kanta, kalaman na zauna mata, tunda ta bude ido su kadai din ta gani, ita da Daada, kafin ta ga su Daddy, su kadai ne kamar yanda Salim ya fada, daga Yelwa har Kabir basa nan, basa tare da ita tun daga farko, ganin takardar nan ba zai kawo su ba in har suna raye, shekaru sha shida suke da shi su zo inda take, duk basu zo ba. Ba zasu dame ta da yawa ba, ba zata basu wannan muhimmanci ba, watakila a gaba, amman yanzun bata jin zasu same shi. Kamar Salim yaji tunanin da take yi

"I love you"

Kalaman suka subuce suna komawa cikin kunnen shi da wani yanayi da ba zai misaltu ba, tunda yake, ko da wasa, ko a mafarki bai taba furta su ba, babu wanda ya taba furtawa, duk da su Adee na yawan fada mishi, amman bai taba mayar musu ba, idan basu gane yana son su a kananun abubuwan da yake musu ba, to baya jin dan ya fada zai canza wani abu, sai gasu yau kalaman sun subuce mishi kamar bashi da iko da su. Dariya Madina tayi tana kallon fuskar shi

"Nawa yafi yawa, nagode Hamma"

Ya kasa ko motsin kirki sai ta fita harta rufe mishi murfin motar, ba shiri ya zare seatbelt din yana fitowa, harta shiga gida, da kusan gudu ya bita yana kiran sunan ta, da mamaki ta juyo, numfashi ya sauke yana kai hannu ya yamutsa sumar da yake askewa kasa sosai, amman yanda take a nannade duk da bamai yawa bace zai sa kagane ya hada jini da fulani.

"Ki fada in ji"

Ya tsinci kan shi da fadi, yana so yaji ta furta kalaman ko zai samu saukin cewa shi sun kubce mishi, yana so yaji ta furta dan ta nuna mishi itama a wajen ta suna da saukin fita kamar a wajen su Khalid, kalaman basu da nauyin da yake jin sun mishi

"I need to hear you say them Mug"

Ya fadi yana saka idanuwan shi cikin nata, ita kuma da mamaki take kallon shi, saboda tana tunanin meye yake so ta fada din

"Mug..."

Ya kira wannan karin muryar shi na fitowa a kagauce, numfashi ta ja

"Oh..."

Tana tuna me ya fada a karshe

"Mi yedi ma Hamma Am, ina son ka"

Numfashin da bai san yana rike da shi ba ya saki yana jinjina kai, kafin ta sake fadin wani abu harya juya. Motar shi ya koma ya kunna yana janta ya fita daga unguwar, yakan ja gilasan ne ya rufe saiya kunna AC din ciki saboda ya rage ma kan shi hayaniyar kan hanyar. Amman yau iskar da take cikin motar yake jin tayi mishi kadan, shisa ya sauke gilasan gabaki dayan su, yana shakar iskar da ta shigo, tana fifita mishi wajajen da baima san yayi zufa ba.

Ba gida yayi niyyar nufa ba, shisa da ya gan shi bakin gate, yaga an bude mishi yasan Allah ne kawai ya kawo shi lafiya, hankalin shi gabaki daya baya jikin shi, shiga yayi da motar ciki, kila idan ya watsa ruwa ya dawo dai-dai. Sai dai yana fitowa daga motar yana cin karo da Julde cikin wata shadda mai maiko da ta karbi jikin shi. Shisa duk yanda za'ace yana da kyau baya mamaki, in har yayi rabin kyawun Julde to tabbas za'a kira shi me kyau, ko shi da kan shi ma zai ga kyawun na shi.

Har yanzun hasken fitilar kyawun Julde zai dishe na shi duk da bambancin shekarun da yake tsakanin su

"Daddy..."

Salim ya kira yana dorawa da gaisuwar da Julde ya amsa fuskar shi dauke da murmushi

"Ya makarantar? Har an dawo?"

Kai Salim ya jinjina

"Zan sake fita, ina so in dan watsa ruwa ne"

Da murmushi a fuskar Julde har lokacin yace

"Allah ya taimaka yayi jagora. A dinga kula dai"

A cikin zuciya Salim ya amsa addu'ar Julden yana wucewa, har yayi gaba ya juyo

"Daddy"

Ya kira yana sa Julde juyowa shima ya kalle shi, dan har ya bude murfin mota

"Wacece Yelwa?"

Ya jefi Julde da tambayar da yaji kamar fadowar gini, babu shiri ya nemi majingini da motar da yake tsaye a jiki, saida ya tabbata muryar shi ba zatayi rawa ba tukunna ya amsa da

"Kanwata ce"

Kai Salim din ya jinjina, haka kawai ya tsinci kan shi da son sani, ko iya hakane, alakar da take tsakanin shi da Madina, ya san yar uwar shi ce, amman yau yana son sanin me suka hada. Juyawa yayi, Julde na bin bayan shi da kallo har ya bace mishi, tambayar ta dake shi, a ina yaji sunan Yelwa? A ina Salim yaji sunan da yake da tabbacin ko Saratu ba zatayi kuskuren furtawa a gaban yaran ba. Ba zama sukayi sukai shawara ba, basa bukatar sanin ya kamata su kare yaran daga abinda ya rabo su da asalin su.

Sai dai wasu sirrikan basa binnuwa
Wasu sirri kan ko ba'a tono su ba sai sun bayyana kan su.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com
Whatsapp: 08074545149

*RAI DA KADDARA 1*

14

Da yawa zasu ce tana jin ranar ne daban saboda ta kasance daya daga cikin ranakun da ya kamata ace suna da muhimmanci a tare da ita, tunda a yau din ta kammala jarabawar aji shidda da ake kira da WAEC. Sai dai ita din ba kamar kowa bace ba, yanda ta ga yan ajin su na murna da rawar kafa tunda ma suka shiga aji shiddan sai ya dinga bata mamaki, zaka rantse da sun gama sakandire shikenan sun rabu da karatu har abada, bayan tana jin tarin burikan da kowanne a cikin su yake lissafawa.

"Ke ba zakiyi su calender din da naga Adee tayi da suka gama makaranta ba?"

Salim ya tambayeta, dan shima yaga da yawa matan ajinsu sunyi a wancen lokacin, tunda duk sun bashi, wasu a ciki yana da tabbacin sun bashi fiye da abinda suka rarraba, da yake shima jeka ka dawo yayi, kuma Julde ya bashi mota tun yana aji biyar, da ba da ita yaje ba, bashida inda zai zuba kayayyakin da aka dinga bashi

"Um um fa, ni babu abinda zanyi..."

Dan ba burgeta sukeyi ba, bata da wata kawa da zata nuna ta kira da tata a cikin ajin gabaki daya. Sai dai tace abokan karatu, zasu gaisa dai, sunma fi kulata idan an bada wani aiki mai wahala da suka kasa fahimta suna son ta taimaka musu. Shisa yau ana gama jarabawa ta fito, taji dadin samun Salim yana jiran ta, sai hade fuska yake sanda ta shiga motar, ta kuma san baya rasa nasaba da hayaniyar da ta karade wajen da zaice mata yana jinta har cikin kwakwalwar shi.

"Mug..."

Ya kira, murmushi tayi mishi, bakar rigace a jikin shi, kamar yanda tunda ya fara aiki yake cikin su, sai ya dora farar rigar da zata nuna maka alamar likita ne a sama, yanzun take kara ganin dalilin da yasa wasu a ajin su suke tambayarta meye hadinta da Salim, yana da kyau, yana da kyawun da ba saika kalle shi sau biyu ba zaka gane hakan. Musamman yanzun da ya ajiye gashi kwance luf a fuskar shi, saiya kara wani irin kyau da Madina ta san ba ita kadai take ganin shi ba. Kaf gidan su babu mai kyawun shi, shine ya biyo Julde sak, sai dai takan ga idanuwan Saratu a cikin na shi.

"Hamma Am, yau fuskar ka ta mun wani iri"

Numfashi ya sauke yana murza mukullin motar, kamar ba zai amsa ba dan har yaja motar ma sun fara tafiya

"Nagaji ne, na kwana a wajen aiki, tunda safe ina can kuma...sai yanzun na taho"

Har ta daina tambayar shi akan maganar shifting da tasan anayi a asibiti, wasu suyi aikin safe, wasu na rana, wasu na dare, tunda ya fara zuwa asibiti ta kula rabin rayuwar shi acan yake yinta, kamar bashi da wani abu a yanzun da yafi majinyatan asibitin da yake aiki muhimmanci. Kuma kusan hakanne, tunda yana jin kamar yana wani abu da rayuwar shi wanda ya kamata, kamar da duk wata dakika da zaiyi wajen taimakon tarin marassa lafiyan da ke asibitin da yanda daudar zunuban shi take dan ragewa, duk da a satikan yana jin da ya rage daudar daya sake maye gurbin ta da matan da yake bi.

"Ki dauki gifts dinki a baya"

Salim ya fadi bayan ya tsayar da motar kofar gidan Daada, duk hirar da ta dinga mishi da um yake binta, yar maganar ma bata samu ba, kamar yanda yace mata a gajiye take duk wata alama ta nuna a gajiyen yake.

"Kasan ina son ka ko?"

Ta fadi tana murmushi, idanuwan shi kawai Salim ya saka cikin nata, shi ya fara cewa yana son ta, sau daya ne, bai kara ba har yau. Sai dai ya bude mata hanyar fada mishi tana son shi duk lokacin da zai mata wani abu da taji dadi. Bai sake fadi bane saboda ya ga soyayyar da yake nufi da wadda take nufi tayi hannun riga. Sai dai baya nufin soyayyar ta bata nukurkusar shi, bayajin ta har kasan ran shi, ya sha farkawa cikin dare ya duba zuciyar shi yaga itace dalilin tashin na shi. Bai kara sanin da gaske soyayyar da yake mata take ba sai lokuttan da ya samu kofar rungumar ta a jikin shi yaki yin hakan.

"Madina ce"

Shine abinda zuciyar shi ta gaya mishi, a lokuttan ne kuma yaga yanda yake da zabi a rayuwar da ya daukar ma kan shi, idan yana son jinta a jikin shi da duka rayuwar shi amman ya iya rike kan shi, me yasa yake kasa rike kan shi akan sauran matan? Ya dauki tunanin ne yayi kasa dashi yasa wani abu mai nauyin gaske ya danne shi, Madina tana nan, babu inda taje, babu inda zataje, zai kara jira, zai tabbatar zuciyar ta na in da tashi take kafin bakin shi ya kara furta mata kalaman yana son ta.

"Ledoji biyu ne Hamma"

Batare da ya juya ba ya amsa ta

"Duka zaki dauka"

Da ta dauka din ma, bayan addu'a sai da ta kara cewa tana son shi, baice komai ba yaja motar shi yana ficewa daga lungun. Ita kuma gida ta shiga da sallama tana kiran Daada tun kafin ta karasa cikin dakin

"Daada..."

Ta kara fadi ganin ta a kwance kan doguwar kujera, takalmanta ta cire tana takawa har inda Daadar take, sai da ta ajiye ledojin hannunta a kasa tukunna ta kai hannu daya ta taba jikin Daada, har lokacin akwai zazzabi, mai zafi ma

"Daada zazzabin nan har yanzun?"

Madina tace cike da damuwa, murnar da ta shigo da ita na dishewa

"Da sauki, dazun ya sauka ma, dawowa dai ya kara yi kuma na sha magani"

Bata yarda ba, tasan Daada da karfin hali

"Ko dai in kira Daddy?"

Da sauri Daada ta girgiza mata kai

"Ki kyale shi, da sauki har abincin da kika dafa na dan ci fa"

Numfashi Madina ta sauke, da yake sai karfe sha daya take da jarabawar ranar, tana tashi da asuba ta shiga kitchen, sai da ta dafa farar shinkafa, suna da miyar kifi a fridge, dumamata kawai tayi. Ta gyara ko ina tsaf tukunna ta fita, dan ko lafiyar Daada kalau ma, da daddare take wanke-wanke, sai ta share ko ina take tafiya makaranta, girki kawai Daadar takan yi musu kafin ta dawo daga makaranta, da ta gane yin miya da yawa ta saka a fridge ma sai dai ta dafa musu ko shinkafa ko taliya.

"Me kika samo haka?"

Daada ta tambaya tana son canza akalar zancen

"Hamma ne ya bani... Bari in watsa ruwa in sake kaya"

Kai kawai Daada ta jinjina mata, wankan kuwa tayi ta fito, wando ne daya dan wuce gwiwarta yana da madauri daga kasan, sai riga ta kusan kamo tsayin wandon, ta saka bakar safa doguwa. Hulace a hannun ta tana rike da ita, kan kujera ta zauna tana kwance abin da ta daure gashinta dashi dan ta gyara kan duk ya cakude mata, kallon ta Daada takeyi, da gaskw gashi rabo ne, waye zaice Madina zatayi gashi? Babu kitso a kanta saboda ta tsani kitso, sai sun kai ruwa rana take zuwa ayi mata, shima guda biyu ne ko hudu. Duk idan tayi biyun nan tana kama jelunan dan ta nannade su sai wani abu ya soki zuciyar Daada.

Yanzun ma yanda take tattara gashin bayan ta warware shi tana kokarin gyarawa sai da taji zuciyarta ta matse, bata yi kama da Yelwa ba, sai dai ko jini, Yelwa na da kyau kamar mahaifinta da sauran yan uwanta da suke biyo shi, duk da itama Daadar fulani ce gaba da baya, ba zatace gashi ya saka Yelwa a tsakiya ba, tunda bata da wadatar shi, amman mahaifinta na da shi, a nannade ma. Na Yelwa ya sauka har kan gadon bayanta, gashi da santsi, kamar yanda na Madina yake yanzun, bambancin kawai shine Yelwa na son gayu, tana kuma ji da gashin ta, Madina bata damu da shi ba

"Badon kar Allah ya kamani ba ko Daada? Da nayi aski, ko rabine dana yanke"

Ta kan fada kusan duk lokacin da zata taje kan ko inta dawo kitso, gashin bai dameta ba, yanda zata kama shi ta nannade ta daure ta saka hula, ba zaka tana sanin tana da gashi ba sam-sam.

"Kinki zuwa kiyi kitso ko?"

Lokaci daya yanayin fuskar Madinar ya canza, bakinta ta turo gaba, tana kai hannu ta gyara zaman gilashin ta, bata ko amsa Daada ba ta janyo ledojin da ta ajiye, da alamar dayan litattafai ne a ciki. Tana kuwa budewa taga sune har guda goma, murmushine ya kwace mata batare ma da ta sani ba tana fadin

"Allah ne kawai zai biya ka Hamma"

Har ranta taji dadin kyautar, batajin akwai wani abu da zakayi mata kyauta da shi da zai faranta ranta kamar littafi. Ko damuwar Yelwa da ta kasa cirewa a ranta, dan duk yanda ta so ta ture tunanin iyayen nata can kasan ranta sai ta kasa, tana zaune zata ji sun fado mata. Idan abin ya isheta zata dauki littafi, babu wani tunani da yake rage mata banda kalmomin da suke yawo a idanuwanta duk idan ta dauki littafi. Ko rike littafin tayi a hannunta sai taji farin ciki. Dayar ledar ta jawo tana budewa, wannan karin ihun da tayi sai da Daada ta dan runtsa idanuwan ta.

Waya, waya ce a kwalinta. Ta kasa daina ihun murna

"Waya Daada.. Waya..."

Take fadi kamar zata fasa dakin da karajin ta, tama kasa nutsuwa ta bude wayar da kyau, zuciyarta har makoshin ta saboda murnar da takeyi, dakyar ta iya samun nutsuwar dubawa taga Itel ce da sukayiwa laqabi da vision. Ta taba ganin wata itel a hannun Samira yar islamiyyar su, da yake yarinyar bata gajiya da nuna cewa babanta mai hali ne, duk tsanani irin na makarantar sai da ta zo da waya a boye, yana ta nunama kawayenta, wayar tayi ma Madina kyau, dan wata taji tana cewa

"Itel ce, irin ta Yayana sak"

Tunda daga nesa take hangen su, waya na burgeta, ko dan ma ta dinga daukar hotunan lallen ta, tana yawan jin ana zancen manhajar Instagram inda zaka iya dora hotuna irin wa'annan, ita duk a cikin kafofin sada zumunta nan ne take zumudin budewa. Saboda jin yanda Instagram yake ne yasa ta dan kulla abota da Nafi'un ajin su, shi yayi mata bayanin komai, har tana ganin ta gama fahimtar yanda manhajar take, waya ce kawai ta rage mata. Inda tace Julde ya sai mata, zai sai mata, amman tunda bai dauka ya bata da kanshi ba, tana da yakinin yana ganin lokacin da zata rike ne baiyi ba.

Gashi Salim ya bata, sai da tazo budewa ta kula da an ma bude wayar, dan babu ledar sabuntar nan, kwalin kawai ta cire, aikuwan an bude dan har pouch an saka mata baki, wayar tayi mata kyau matuka, fara ce.

"Daada kingani"

Ta fadi cike da farin cikin da yasa Daada murmushi, karbar wayar tayi tana dubawa

"Ma shaa Allah. Allah yasa alkhairi yabar zumunci..."

Farin ciki baibar Madina ta amsa Daada ba, wayar kawai ta karba tana kunnawa, cike take da caji, Salim kuma har sim ya saka mata, sa da ta gama kawowa ne taga kusan komai ma ya saita mata shi, dan har email ma taga ya bude mata, yar takarda ta kula da ita a cikin kwalin wayar ta dauko tana warwarewa, aikuwa email dinne da kuma password din shi ya rubuta mata, shafa rubutun tayi cike da farin ciki, tana tunanin yanda wannan cakudin rubutun da likitoci suke da shi na Salim ya bambanta, yana da rubutu mai matukar kyau.

Duba contact dinta tayi, ya saka mata lambar shi, ta Khalid, Adee, Julde, sai lambar Nawfal. Duka da sunayen su yayi saving, sakewa tayi tana gyarawa zuwa yanda take so, ta shi lambar ta saka "Hamma Am" a jiki. Murmushi yaki barin fuskar ta, earpiece din wayar da cajar ta dauko tana gyara kwalin ta rufe ta mayar cikin ledar ta kulle, murna fal cikinta ta dauka da ledar litattafan ta kai daki ta ajiye su kan gadon ta sannan ta dawo tana nufar kitchen, abinci ta zubo ta dawo ta zauna suka fara hira da Daada, duka yau hirar akan wayar tane da abinda zatayi da wayar.

*

Ta dauka bambancin ranar zai kare ne da kyautar da ta samu daga wajen Salim, da kuma wayar da sukayi, duk da sukanyi a land-line din Daada, amman sai take jin wannan din ta sha bamban, sanda duk ta so magana da shi zata iya, flashing kawai zatayi mishi ta san zai kirata. Har ta fara bacci, wajen karfe goma da rabi ta farka, sai ta sauko daga kan gado ta nufi dakin Daada, ba bakonta bane ba, ba kuma ranar bace ta farko da ta saba barin dakinta taje bayan Daada ta kwanta, wasu lokuttan ma cikin bacci takeyin hakan, sai da asuba take sanin ta koma dakin.

Karfe daya da kusan rabi taji Daada tana zare jikinta daga rikon da tayi mata, saukarta daga kan gadon yayi dai-dai da bude idon da Madina tayi tana juyawa, wani yunkurin amai da Daada tayi yasa Madina dirowa daga gadon tana jin ta wartsake gabaki daya, bandakin ta shiga, da yake da wuta kwan a kunne yake, amai Daada takeyi kamar zata zazzage hanjin cikinta, banda sannu babu abinda Madina takeyi mata. Ita ta taimaka mata ta wanke fuskarta ta kuskure bakinta suka fito, zazzabi ne a jikin Daada kamar wuta, cikin kasa da minti talatin harta fara fita daga hayyacinta saboda zafin zazzabi.

Madina bata san hawayen ta zai iya yin nisa ba sai yau, banda bari babu abinda jikinta yakeyi, musamman da ta jijjiga Daada tana kiran sunanta taga ko jinta batayi, dakyar ta samu ta sauketa daga jikinta, dakinta ta nufa tana dauko wayarta ta kunna, sai take ganin ta dade bata gama lodin ba, tana karasawa lambar Salim ta lalubo tana kiran shi, tana jin bugun wayar na daidaituwa da na zuciyarta, sai dai harta yanke bai dauka ba, sai da tayi mishi kira hudu, ana

biyar ya daga yana fadin

"Mug...lafiya?"

Numfashinta na wani irin sama, muryarta na sarkewa saboda nauyin da harshenta yayi tace

"Da... Daada bata da lafiya... Hamma, Daada..."

Ta karasa a wahalce

"Ki nutsu, ki tuna abinda na fada miki na taimakon gaggawa, kina jina? You can do this, kije wajen ta, yanzun zan taho"

Kai Madina take dagawa tana fita daga dakin, wayar ta ajiye a gefe tana karasawa wajen Daada da sauri ganin tana yunkurin amai, juyata tayi kan hannunta kamar yanda ya sha fada mata, saboda a rigingine Daada take, zata iya shakewa idan tayi amai a haka, sai zazzabin jikinta yayi yawa, bandaki ta nufa tana zubo ruwa a bokiti ta dauko towel ta zo tana tsomawa, idan ta matse sai ta goge ma Daada duk inda ta samu a jikinta. Bata san iya tsayin lokacin da suka dauka, ko inda ta samo nutsuwar da ta samu ba.

Da Salim ya kira wayarta ma, da kanta ta dauki mukulli taje ta bude mishi gidan suka koma ciki tare, batayi mamakin yanda ya kama Daada yana dagata ya saba a kafadar shi ba, ko nishi bata ji yayi ba, hijabin Daada ta daukar mata, tana komawa dakinta ta saka karamin hijabi itama. A kofar gida ta samu Salim, shiya karbi mukullin yana rufe gidan, baya ta shiga kusa da Daada tana kama hannunta ta rike, Salim ya zagaya mazaunin direba yaja motar. Asibitin Aminu Kano inda can yake aiki suka nufa, babu wani bata lokaci aka samarwa Daada daki ita kadai aka kuma fara bata taimakon da take bukata, saboda Salim din, shi baibi sauran likitocin ba sai da ya tsaya aka binciko file din Daada tunda nan asibitin take zuwa duk idan bata da lafiya.

Da kanshi ya bude yana bincika record dinta kafin ya bisu dakin, har an saka mata ruwa an mata allurar jini, wata Nurse tace mishi an dauki jininta don a gudanar da gwaji, tambayoyi ya shiga yi ma likitan daya duba Daada din suna magana cikin harshen da in ba fannin aikin su ka karanta ba sai sun fassara maka zaka gane me suke cewa. Tare suka fito da likitan, shi yana wucewa, Salim kuma yana kallon inda Madina take tsaye ta jingina bayanta da bangon wajen, ko takalma bata da shi, safa ce a kafarta, dan dai tana da kauri, sai kayan baccin da ko shi ya saka tsayin wandon ne kawai zai mishi kadan. Dan murmushi yayi yana karasawa ya taba kafadarta.

Da sauri ta kalle shi

"Hamma? Me yake damun ta?"

Kai Salim ya girgiza mata

"Komai zaiyi dai-dai"

Ganin yanda take kallon shi ya sa shi dorawa da

"In shaa Allah"

Kai ta jinjina badan ta yarda ba

"Ki shiga ki zauna da ita, zan kira Nanna in fada mata"

Kan dai ta sake jinjina mishi, murmushin karin kwarin gwiwa yayi mata, baya son yanda tayi sanyi, sai da ta tura kofar dakin da Daadan take ta shiga tukunna ya sauke numfashi. Ya kanji Julde yace Daada bata da lafiya, ko kuma ya biya ya kai mata magungunan ta, wasu lokuttan ma tare suke zuwa su duba ta, amman yaune ranar farko da yasan tana dauke da ciwon zuciya, saboda bai taba tambayar Julde me yake damun Daada ba, yanzun ma a file din ta ya gani, jininta ma yakan hau ya sauka, amman baya irin hawan da za'ace yana barazana da rayuwar ta, ciwon zuciyar ne dai.

Da alama Madina ma bata sani ba, kuma ba zai zama na farko da zai fada mata ba. Lambar Julde ya fara kira sai yaji ta a kashe, hannu ya kai yana murza goshin shi, yana da round din da zaiyi, ba yanda za'ayi ya zauna da Madina, kuma ba zai yiwu abarta ita kadai ba. Baya son wayar ta tashi Saratu, Khalid ya kira, bugu biyu ya daga

"Hamma, lafiya dai ko?"

Yanayin muryar Khalid din ya sa Salim fadin

"Uban me kakeyi ba kai bacci ba har uku na dare?"

Yanajin yanda Khalid ya sauke mishi numfashi a kunnen shi, abinda ya tsana, shisa in zai waya yawanci yake sakata a speaker ya ajiye a kasa, ya rasa dalilin da zaisa anna waya ana numfarfashi da wasu kananun nishi da yake bakanta mishi rai

"Kira na kayi kaji ido na biyu ko akwai abinda zaka fada mun?"

Cewar Khalid din

"Daada bata da lafiya, gata a asibitin mu, ka fadawa Nanna, bana so in tasheta da waya"

Yana jin motsi alamar Khalid din ya tashi

"Subhanallah, tun yaushe?"

Kashe wayar Salim yayi, saboda zai iya watsama Khalid din zagi, yana da tambaye-tambaye marassa amfani, a aljihu ma ya saka wayar, yana barin bangaren gabaki daya zuwa inda ofishin shi yake.

*

"Daga jikin wa ka baro ka taho?"

Cewar Saratu bayan Julde ya shigo dakin tana binshi da wani mugun kallo, bacci takeyi taji ana kwankwasa dakinta, dakyar ta rabu da gado tana zuwa ta bude

"Nanna..."

Khalid ya kira yana dorawa da

"Daada ce bata da lafiya, tana asibiti, yanzun Hamma ya kira yake fadamun"

Dan dakuna fuska tayi, kafin ta jinjina ma Khalid kai tana juyawa batare da tace komai ba

"Bari in sakko dogon wando in dauko id card dina sai in zo mu tafi"

Har ranta batayi niyyar zuwa ba, rashin lafiyar Daada ba matsalarta bace ba saboda dalilai masu yawa, amman akwai halayenta da bata cika son yaran nata suna gani ba, musamman Khalid, shisa ma ta daga mishi kai kawai, kayanta ta sake itama, suna hanya tana hamma saboda baccin da ko awa batayi da samun shi ba. Fadan da sukayi da Julde kafin ya fita ya sa taita juyi a gado ranta na mata zafi

"Bunsuru kika taba kirana Saratu, ko kin manta? Ban canza ba har yanzun, bunsurun ne, ki daina yin kamar baki san abinda zan fita yi ba"

Duk tashin hankalin da tayi bayan nan ko inda take bai kalla ba, tasani, ta fi kowa sanin me yake fita yi duk daren da zai shirya tsaf ya fice, tana kauda kaine yanda ta saba, tana kuma amaye abinda take ji idan yazo mata wuya. Kamar yanda tayi jiya, sai dai ko yaushe ita ce take faduwa kasa warwas, dan fada da Julde babu riba a cikin shi, ko tace bata samun riba a fada da shi. Sai ya tabbatar ya nuna mata bata da muhimmanci a rayuwar shi, zaman da takeyi da shi zabinta ne, in ta barshi babu abinda zai canza. Hakan yafi mata ciwo fiye da neman matan shi, ba zatayi karya ba, zata so ko kadan ne ta samu wani muhimmanci a rayuwar shi.

Don shi yana da shi a tata rayuwar, akan ce wasu mazan na duba darajar 'ya'ya, to a idanuwan Julde bata taba cin darajar yaran su ba, zaka rantse da Allah shi yayi dakon cikin su, nakuda da rainon su

"Saratu"

Julde ya kira cike da kashedi yana kallon Daada da take kwance, da alama bacci takeyi, sanin cewa bai daina halin shi ba shine karshen abinda zai so taji

"Meye? Baka so ta sani? Baka so taji babu abinda ya canza daga mugun halin ka?"

Runtsa idanuwan shi Julde yayi yana sake bude su akan Daada, ko motsi baiga tayi ba. Likitanta daya gani kafin ya shigo ya fada mishi ciwon zuciyarta ne, amman babu wata matsala in dai ta samu hutu kwana biyu, a kuma tabbatar babu wani abu daya faru da zai daga mata hankali, in dai an kiyaye wannan zata samu sauki. Wannan maganar da Saratu take son ya biye mata suyi na cikin abinda zai daga hankalin Daada. Shisa yaja kujera ya zauna yana yin shiru ya kyale ta. Yana jin yanda take watsa mishi wani irin kallo, kafin ta ja tsaki tana mikewa ta fice daga dakin.

Daman ko bai zo ba, ita gida zata tafi, bata da dalilin zama asibiti, ta dai cewa Madina zata zauna ne dan taje gida ta watsa ruwa ta sake kaya ta kuma dauko musu abinda suke bukata. Salim ne ya tafi ya kaita tunda gari ya waye. Da kanta ta kira Adee ta fada mata, saboda tasan zata kawo abincin kari

"Saboda Yelwa kawai"

Ta fadi cikin ranta bayan ta rufo musu kofar. Ko Daada ba darajar Julde take ci ba a wajenta, saboda Yelwa ne, in har mutunci zai shiga tsakanin su bayan tarin kiyayyar da ta nuna mata to saboda Yelwa ne. Julde kuwa numfashi ya sake saukewa yana kallon Daada, wayar shi a kashe take, cikin mota ma yabar ta, sanda ya fito bayan asuba ya zo ya kunna ya ga sakon Khalid, kai tsaye asibitin yayo, sai dai da nisa daga inda yake, tunda yafi zuwa hotels din wajen gari, inda kafin ya hadu da wanda ya sani za'a dauki lokaci, ko gidan gonar da yayi shi don wannan dalilin kawai ba don komai ba.

Kafin yayi wani tunani an turo dakin da sallama

"Daddy..."

Salim ya fadi cikin gaisuwa, Adee da ta shigo bayan shi da murmushi a fuskarta ta gaishe da shi itama, kallon ta Salim yayi, suna hanyar gidan Daada wayar Salim ta shiga vibrating, dagawa yayi ganin Nawfal ne ya sa shi kai wayar kunnen shi

"Na kira Hamma Khalid bai daga ba, me ya sami Daada? Yace mun bata da lafiya tana asibiti, me suka ce yana damun ta? Ya jikin ta?"

Yanda yayi duka tambayoyin a numfashi daya yasa Salim fadin

"Da sauki"

Cikin taushin murya yana dorawa da

"Zazzabi ne kawai, da sauki kuma sun riketa ne dan ta huta sosai"

Duk da baiga Nawfal ba yasan ya ciza gefen leben shi na kasa yanda yakan yi duk idan yana cikin damuwa

"Dan Allah Hamma ka fadamun gaskiya, ya take? Boye mun ba zaiyi amfani ba, is not like zan iya tahowa yanzun-yanzun, kawai ina bukatar in san halin da take ciki"

Bai fada mishi dukkan gaskiya ba, amman da sauki, zazzabin ya sauka, da kan shi ya duba kafin su taho, kuma jininta lafiya kalau, bai hau ba

"Ga Madina..."

Salim ya fadi yana mika mata wayar, saboda baisan me zai fada Nawfal ya yarda da shi ba

"Madina"

Muryar Nawfal ta daki kunnen ta tana sakata jin wani abu ya tsirga mata

"Hamma"

Cikin wani irin yanayi Nawfal yace

"Ya take Madina? Ki fada mun? Ke nasan ba zaki mun karya ba"

Numfashi ta sauke

"Da sauki, bata kara yin amai ba, tana ta bacci ne, gani ma Hamma zai kaini gida in watsa ruwa in dauko mana su kafet haka..."

Tana jin ajiyar zuciyar da Nawfal ya sauke yana ma Allah godiya cikin harshen fulatancin

"Ban san ya zanyi ba in wani abu ya same ta, ban sani ba...na kusa dawowa gabaki daya in shaa Allah, saura yan watanni, ba zan kara nisa ba idan na dawo..."

Madina bata jin ko ya dawo zata daina jin yanda yayi mata nisa

"Idan ta tashi ki kirani, tana tashi Madina"

Kai ta jinjina

"Zan kira ka Hamma..."

Kamar ba zata sake cewa komai ba tace

"Ka yarda dani, da sauki, da sauki sosai"

Yanda ta karasa maganar ne ya kasa barin kunnen Salim, kulawar da take cikin muryarta yaji ta sa kirjin shi ya matse, sai kuma yanda ta mika mishi wayar tana fadin

"Hamma ya cika saka damuwa a ran shi"

Tana saka shi dana sanin bata wayar da yayi, har ya jirata bai daina jin wani zafi-zafi a kirjin shi ba, yanzun ma da yake kallon ta yana jin yanayin na karuwa ne, akan me zata sauke murya da yawa haka, shi bai taba ma jin ta sauke mishi murya cikin kulawa yanda ta sauke ma Nawfal ba, wayar shi da yaji tana zuu cikin aljihun shi ya zaro ya duba

"Hamma ne?"

Madina ta tambaya, shi dinne, baisan me yasa ya girgiza mata kai yana juyawa ya fice daga dakin kafin ya daga wayar ba

"Hamma ta tashi?"

Nawfal ya tambaya daga dayan bangaren

"Yanzun muka dawo Bajjo, bacci takeyi, tana tashi ni da kaina zan kira ka"

Yana jin Nawfal din ya sauke numfashi cike da damuwa

"Bacci takeyi, bacci take Bajjo, na taba maka karya?"

Cewar Salim yana jin yanda baya son damuwar Nawfal din da yake karanta ta cikin wayar

"Zan kara kira"

Kawai Nawfal yace yana kashe wayar. Dakin Salim ya koma, camera din wayar shi ya shiga yana kashe hasken sannan ya dauki Daada hotuna guda biyu, batare da tunanin komai ba ya bude whatsapp din shi yana tura ma Nawfal

"Kagani, da sauki, kuma kaci abinci"

Ya rubuta a kasan hotunan yana sauka daga whatsapp din bayan yaga shigar sakon na shi ya mayar da wayar a aljihu, bashi da matsala da kula da Nawfal, kawai baya son Madina tayi ne, ko kadan baya so, bai taba sanin baya so ba sai yau.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com
Whatsapp: 08074545149

*RAI DA KADDARA 1*

15

Sake runtsa idanuwan ta tayi a karo na babu adadi, saboda duk lokacin da zata bude idanuwan sai ta dinga jinta a wata duniya tsakanin rayuwa da wani abu da ba zata iya kira da mutuwa ba tunda bata san yanda take ba. Ko wacce gaba ta jikinta ciwo takeyi, ga kirjin ta da yayi nauyi tamkar an dora wani irin dutse a saman shi

"Daga jikin wa ka baro ka taho?"

Kunnuwan ta sun jiye mata wannan kalaman, idan ba karya suka isarwa kwakwalwar ta ba tabbas muryar ta Saratu ce, a tsayin shekarun nan duk wasu kalamanta na rashin kirki ta koyi takaita su ne akan Julde kawai, shisa zuciyar Daada take hasasa mata cewa wannan karin ma da Julden take, wani irin hijabi taji ya gifta tsakanin ta da zantukan su Saratun shisa ta hakura tana barin duhun da ya janyeta yin nasara.

"Daada ga Hamma can ana dukan shi a gonar mai saje, kiyi sauri kizo, kiyi sauri kar su illata shi"

Yelwa ta sauke kowacce kalma a tsakanin numfashin da take kokawa da shi cikin alamun gudu tayi, a cikin harshen fulatanci, murfin tukunyar tuwon da Daada ta gama tuqawa ta dauka tana rufewa, kafin ta daga idanuwanta tana sauke su kan Yelwa cike da nutsuwar da zakayi mamakin ta a tattare da mahaifiyar da aka zo ma da sakon ana dukan danta. Sai dai bashi bane karo na farko, ba kuma na biyu bane ba, idan Daada zata runtsa idanuwan ta, lokutta irin wannan zasu bace a tunanin ta, ba zata iya lissafa adadin su ba saboda yawaitar faruwar su

"Daada ki ta so"

Yelwa ta sake fadi a kagauce, murmushi Daada tayi, murmushin da taji ya fito daga tsakankanin zuciyar ta inda yake yawaita yi mata ciwo da labarai irin wa'annan

"Me zan musu Yelwa? Zan iya hana su dukan shi ne?"

Kai Yelwa ta girgiza cikin alamar rashin yarda, daga inda Daada take zaune tana ganin kyallin hawayen da yake cike da idanuwan Yelwar, kafin ta kai hannu tana daukar muciyar da take a jingine da bango, ko gama bushewa daga wankin da Daada tayi mata ba tayi ba

"Ba zasu kashe shi ba, ba zan bari su kashe shi ba Daada"

Yelwa ta karashe maganar tana kai dayan hannunta ta dauke hawayen da take jin alamun zubowar shi tana juyawa

"Allah ya tsine miki albarka idan kika saka kafa kika fita daga cikin gidan nan"

Ta tsinkayo muryar Datti a masife da ta saka kafafuwanta tsayawa cak

"Kin jini ko Yelwa? Allah ya tsine miki albarka idan kika fita daga gidan nan"

Juyawa tayi tana fara sauke idanuwan ta kan butar da take hannun shi, daga bandaki ya fito. Yana gidan kenan? Dariya Yelwa tayi me sauti

"Ki bari su kashe shi, Allah ya basu sa'a su kashe shi"

Wannan karin hawayen Yelwa zubowa su kayi

"Asarar tawa ce ni kadai idan sun kashe shi na sani..."

Ta ce tana sake kai hannu ta share kuncin ta, tana kara ba wasu hawayen damar zubowa, kafin ta janye idanuwan ta daga na Datti tana sauke su cikin na Daada

"Muna da junan mu, ni da shi, ki fada mishi Daada, ya kara tsinuwar shi akan jerin na baya..."

Yelwa ta karashe tana juyawa ta nufi hanyar da zata fitar da ita daga cikin gidan, sautin tsinuwar da Datti yake jera mata nayi mata rakiya

"Daada..."

Ta tsinkayi muryar Yelwa na mata kutse cikin duhun da ya janyeta

"Daada!"

Ta sake jin muryar

"Ki barta tayi baccin ta"

Ta tsinkayi wata murya da take son gane madaukin ta

"Idan naga ta bude idanuwan ta ko kadan ne zan samu natsuwa Hamma...Daada!"

Sai dai a karo na farko ta raina karfin ta, saboda yanda take kokawa da fatar da take lullube da idanuwan ta cikin kokarin bude su. Hannun da taji kan nata ya kara mata karfin gwiwa, dakyar ta iya bude rabi tana ganin dishi-dishi, ta mayar ta rufe, tana sake kokartawa wannan karin dan gabaki dayan shi ta bude shi

"Madina"

Ta fadi cikin zuciyar ta, ganin gilashin da yake fuskar ta, ba Yelwa bace ba, Madina ce, tunani ne ya dibeta zuwa baya, babu wani abu. Tabaro wannan rayuwar, tayi nisa da ita. Inda take yanzun ba can bane ba, tana tare da Madina, tana tare da sanyin idaniyar ta, tana tare da yarinyar da ta saukaka ciwon da yake cikin kirjin ta

"Daada..."

Madina ta fadi da murmushin nan nata da yake sanyaya wajaje da dama a tare da Daadar

"An mata allurar bacci ne fa, me yasa bakya jin magana ne?"

Salim yace yana jin muryar shi ta fito da wani irin sanyi da baiyi tsammani ba, fada yaso yayi mata, a fadace ya jera kalaman cikin kan shi, a tsakanin ratsowa ta cikin kan zuwa makoshin shi suka sanyaya haka, tafi minti sha biyar tana son tashin Daadar yana hanata, har bakin shi ya fara nauyi da yanda take ta saka shi yawan magana. Rigar ta da shi kan shi ta mishi yawa ya kama ta baya yana janyo ta baya kamar ya jawo ledar da babu komai, kafin tayi wata garda ya sa kafar shi ya jayo kujera yana fisgarta ya zaunar a kai.

Bayan yatsun shi biyu da manuniyar da na tsakiyar ya hade waje daya yayi amfani da su yana kai mata duka a goshin ta har saida ta runtsa idanuwan ta dan taji zafi sosai tana fadin

"Ouchhh Hamma..."

Hadi da murza wajen tana turo labba

"Ki zauna nan, nagaji da magana"

Bakin dai ta sake turowa har lokacin tana murza goshin ta, Daada ta kalla, ta sake mayar da

idanuwan ta rufe, yanayin yanda take numfashi na nuna alamar bacci ya sake dauke ta, agogon da yake daure a hannun shi Salim ya duba, sam bai san lokaci ya ja haka ba, shisa yaji kan shi yayi nauyi. Bacci ne sosai a idanuwan shi, gashi aikin dare yake da shi yau ma, mikewa yayi

"Zanje gida in watsa ruwa in dan kwanta, ki kirani idan akwai wani abu, anjima zan dawo"

Kai Madina ta jinjina mishi, tun dazun yake ta hamma, da tace yaje yayi bacci kai ya girgiza mata, itama bata son zama ita kadai, taji dadi da Adee ta zo, amman bata wuce awa biyu ba tace zata koma dan ta dake dora musu abincin da zata kawo da daddare, zasu sake dawowa da mijinta. Julde ma kiran da ake ta mishi a waya yasa Salim ya lallaba shi ya tafi bayan ya tabbatar mishi da cewa babu komai, bacci Daadar takeyi saboda ana so ta huta sosai.

"Ka siyo mun awara idan zaka dawo"

Numfashi Salim ya fitar

"Ina zan ga awara?"

Shagwabe fuska tayi

"Akan titi fa, ko ina zaka ga ana soyawa, ba mun taba siya ba rannan?"

Kai Salim ya girgiza

"Rannan din kinsan wacce hanya ce? Kibari idan muka fita tare"

Yanda tayi da fuska tana kai hannu ta sake tura gilashin ta sai yaji gwiwoyin shi sun yi sanyi, kananun abubuwa haka zatayi duk sai yaji ta kashe mishi jiki

"Fine, idan nagani"

Murmushin nan ya samu da takanyi da dukkan hakoranta, tana saka shi mayar mata da martani

"Ina kudin da Daddy ya baki?"

Hannu ta fara kaiwa aljihun wandon da yake jikinta, tana saka shi girgiza mata kai

"Ba sai kin dauko ba, idan kina son wani abu ki fita ki siya, inda muka siyo ruwa dazun, zaki gane ko?"

Kai Madina ta daga mishi kafin ya sake numfasawa

"Ki kula kina ji? Ba zan dade ba"

Kan dai ta sake daga mishi, ji yake kamar karya tafi ya barta, amman ko baya bukatar hutu yana son watsa ruwa ya sako kaya. Dakyar ya iya jan kafafuwan shi yana fita daga dakin. Gyara zamanta Madina ta karayi akan kujerar tana jingina sosai, ita ma baccin ne a idanuwanta. Ta kusan mintina biyar a haka kafin ta ja kujerar har kusa da gadon Daada, kanta ta dora akan gadon daga gefe tana runtsa idanuwanta

"Allah ya baki lafiya Daada... Allah ya baki lafiya"

Ta furta cikin ranta, addu'a ce da tun da suka shigo asibitin ta dan samu nutsuwa take ta furtawa cikin zuciyar ta. Sanin ba bangaren hannun da ake karawa Daada ruwa bane ya sa ta lalubo shi tana dumtsawa cikin nata, akwai wajaje da dama da ko da wasa ba zata bari tunani ya dauketa ya kaita ba, cikin su har da rasa Daada. Shisa ta sauke numfashi mai nauyin gaske tana sake runtsa idanuwan ta cike da neman baccin da yake cike da su.

*

Yau kwanaki biyu kenan da sallamar Daada daga asibiti, ta ji sauki sosai, sai yawan baccin da takeyi da kuma rashin karfin jiki da ba za'a rasa wanda ya warke ciwo da shi ba, tunda lafiya ce kadai abinda yake kwace maka a yan mintina, amman dawowar ta sai ta dauki lokacin da baka ma yi tunani ba. Madina ta ji dadin kasancewar lokacin cikin hutun da suka samu na tsakanin Waec da Neco. Ko da ace babu hutu ba zata iya tafiya ko ina tabar Daada ba, shisa duk nacin ta da makaranta ta hakura da islamiyya sai ta ga Daada na hidimarta kamar ko da yaushe.

Da wuri ta gama miyar ta da ta sha naman kaza, Julde ya zo ya kawo musu cefane jiya. Ya karo musu kajin da suna da saura a fridge tun wancen karin, farar shinkafa ta dafa, ta fita da kanta tana samun yaro ta aika ya siyo mata salak da tumatir ta yayyanka, kafin sha biyu harta gama gyara ko ina tsaf. Ko da ta idar da sallar azahar ma ta tashi Daada tayi itama, ta samu ta bata abincin da ta dan ci kadan, magungunan rana ta bata sannan ta sake komawa bacci.

Matar da tayi wa alkawarin kunshi tun satin daya fita ce ta zo, ko da tayi mata ya mai jiki Madina batayi mamaki ba sam. Ta san matar ta shiga makota ne ake fada mata, Daada mai mutane, yanda aka dinga zuwa asibitin dubata har mamaki ya dinga bawa Madina, wasu ma ita bata san su ba, duk yawanci basu zo hannu biyu ba, wata mata da kallo daya zakayi mata ka fahimci halin rashin da take ciki dan rake ne ta zo da shi a bakar leda irin wanda ake siyarwa a datse, yanayin karfin halin ta sai da ya taba Madina ba kadan ba.

Kirki abune da ba sai mai hali ba, kowa ma zai iya kamantawa in dai akwai shi a zuciya. Matar ma da ta zo kunshin harda lemon zaki da ayaba ta riko

"Munyi waya da Maman Anisa take fadamun an sallame ku"

Godiya sosai Madina tayi mata, kunyar matar ta sata hada lallen tunda baki ne take so, ta zana

mata a bayan hannu da tafuka, basu wani dauki lokaci ba, yana shan iska tace zata tafi gidan Maman Anisan ya karasa bushewa acan sai ta wanke. Yanda duk tayi da Madina kin karbar kudin kunshin tayi, ko dan alkawarin da tayi ma matar ta saba mata ba zata karba ba. Haka sukayi sallama suna ma juna godiyar karamcin daya gifta tsakanin su, Madina ta tattara kayan kunshin ta tana nade tabarmar ta koma cikin daki. Ganin hudu harda minti biyu ya sa ta nufi dakin ta ta shiga bandaki dan gabatar da uzurinta ta fito bayan ta dauro alwala. Sanda ta shiga dakin Daada ta sameta harta tashi tana sallah.

A gefe ta raba itama tana fara gabatar da tata sallar, ta idar tana dorawa da azkar din yammaci kafin ta jero tarin bukatunta

"Ya jikin Daada? Ko kina marmarin cin wani abin in dafa miki?"

Kai Daada ta girgiza mata

"Alhamdulillah, da sauki sosai"

Hannu Madina ta kai tana taba kuncin Daada

"Babu zazzabin fa, na ce miki yayi sauki"

Daada ta fadi da dan murmushi

"Allah ya karo miki lafiya Daada Am... Kinga wata tazo kunshi ta kawo miki lemo da ayaba da yawa, yar uwar Maman Anisa ce..."

Kai Daada ta jinjina

"Allah ya saka mata da alkhairi, nagode sosai kuwa"

Suna da sauran fruits da Julde ya kawo, wannan dinma duk a fridge ta hada ta samar musu wajen zama

"Ko in kara kawo miki ruwa?"

Kai Daada ta girgiza, babu wani abu da take bukata, matsawa kusa da ita Madina tayi yanda zata iya dora kanta a jikin damtsen hannun Daadar tana jingina da ita sosai

"Karasa ni zakiyi daga farfadowa ta?"

Dariya Madina tayi saboda tana jin zolayar da take cikin muryar Daadar

"Idan na karasa ki in zauna da wa? Hutawa kawai nake danyi, kwana biyu banji dumin ki haka

ba"

Dan kallon ta Daada tayi

"Kaji karya fa, ina ce ko a asibiti a bayana kike kwanciya"

Dariya Madina tayi, jiyama a bayan Daadar tayi bacci, lokutta da dama tafi son jinta makale a jikin Daada, ta zagaya hannunta a cikinta tana saka nata hannun cikin na Daada ta hada yatsun su waje daya. Wasu ranakun ma ko baccin rana a jikin Daada takeyi. Karar wayarta da ta bari a falo ya sata raba jikin ta da na Daada, saboda tasan babu wanda zai kirata in ba Salim ba, har yanzun babu wanda ya san tana da waya, bata samu nutsuwar da zata kikkira mutane da ita ba.

"Hamma..."

Ta furta bayan ta daga wayar ta kai kunnen ta

"Ina kofar gida, yunwa nake ji, me kika dafa?"

Murmushi tayi, yana tuna mata da ita ma bata ci abincin ba

"Ka shigo sai muci, nima banci abinci ba"

Bai amsata ba ya kashe wayar, ta sauke ta daga kunnenta tana ajiyewa akan kujera, dakin Daada ta koma

"Hamma ne ya zo..."

Kai kawai Daada ta daga mata batare da tace komai ba, Madinar ma juyawa tayi, tana shiga kitchen taji sallamar da Salim yayi, daga kitchen din ta amsa shi. Tana zubo abincin a plates guda biyu ta fara kawowa sannan ta hado musu miyar a kwano daya tana sake kawowa, ta samu wani waje ta zubo salak din da kayan hadi. Kafin ma ta dauko ruwa ta dawo Salim harya sakko kasa yaja na shi plate din ya fara ci, tun safe rabon cikin shi da wani abu, shima shayine ya sha dan Saratu na mishi fadan cewa ba inda zai fita bai saka wani abu a cikin shi ba.

"Baka zama kaci abinci ko Hamma?"

Madina ta fadi tana kallon yanda idanuwan shi sukayi zuru-zuru, ya wuce ace yunwar yini daya ce

"Gashi ina ci yanzun"

Ya amsa, kai kawai ta girgiza, in dai akan abinci ne Salim din kamar karamin yaro haka yake,

wata rana idan ya zo sai ta zuba mishi ya tafi da shi, ko ta tsare shi ya ci, sai yace mata aiki ya mishi yawa, ko yunwar ma baiji ba. Ya rigata cinye abincin shi, harya koma plate din ta suka cinye tare

"Ina karo maka?"

Kai ya girgiza mata, ita ce ma ya kamata ta kara, ya san Madina kamar yanda ta san shi, idan tana so ta karo ba zata jira ya fada mata ba. Cikin ta na daya daga cikin abinda bata wasa da shi ko kadan. Kwanonin ta tattara tana mayarwa kitchen ta dawo ta zauna, yatsun ta ya bi da kallo

"Kunshi kikayi ko?"

Ya furta yana jan jikin shi kusa da ita ya kamo hannun ta, bakin da yatsun ukku sukayi har ya fara ragewa dan zaman asibitin da sukayi

"Wata mata nayi wa dazun..."

Kai kawai ya girgiza

"Kina bata hannun ki, na ce ki dinga saka safar hannu"

Dakuna fuska tayi

"Ni wani iri fa, bayamun dadi shisa"

Jujjuya hannun nata yakeyi cikin na shi

"Jibu farcen ki"

Dayan hannun ya dago tana dubawa, shima duk ya taru

"Daada ce take yanke mun, ban iya ba da reza"

Kai kawai Salim ya girgiza yana mikewa. Yana jinta tana binshi da idanuwa, baifi mintina hudu ba ya dawo yana zama in da ya tashi. Hannun ta na dama ya kamo

"Waye yace da reza zaki yanke?"

Karamin yatsanta ya fara kamawa sannan ta kula da nail cutter din da yake rike da shi. Tunda yake mutum daya ya taba yankewa farce, sam baya son yaga kumba ta taru a hannun mutum, yana mishi kazanta ba kadan ba.

"Kalli farcen ka Bajjo"

Ya fadi bayan Nawfal din ya mika mishi remote din daya bukata

"Ni banga mai gyaran farce ba, ni kuma ban iya yankewa ba"

Zai tuna yanda yaja karamin tsaki, yana mamakin yanda kato kamar Nawfal zaice bai iya yanke farcen shi ba, menene a ciki? Ka sa nail cutter din ka datse? Shi kusan duk kayan shi zaka samu nail cutter a ciki, in dai ya gani saiya siya, ko a mota yana da sunfi biyar, baya so ma ya zo ya nema ya rasa. Nawfal din ya sa yaje daki ya dauko ya dawo

"Kai dai katon banza ne Bajjo"

Ya furta yana kama yatsan Nawfal din da yayi dariya kawai. Ya dauka ranar ce ta farko kuma ta karshe, sai yanzun da yake rike da na Madina, daya bayan daya haka ya kama yana yanke mata harya gama tsaf

"Kafar fa?"

Batayi musu ba ta zare safarta guda daya tana mika mishi kafar

"Me yasa kike rufewa?"

Ya tambaya ganin kafar tas, ga kunshin jan lalle da tayi. Ba zai yiwu ace idanuwa shi bane kawai suka ga kyawun kafarta, idan yana da irin wannan kafar baiga dalilin da zaisa ya dinga kunsheta cikin safa ba

"Bana so tayi kura ne fa, iska yana shigar mun kuma"

Numfashi Salim ya sauke, farcen kafar bai wani taru ba, idan na shi ko bai kai haka ba zai yanke, amman kafar ta Madina ce, bai yarda da kanshi cewa zai tsaya a riketa ba kawai

"Na kafar bai taru ba ai..."

Kai ta jinjina mishi tana janye kafarta ta mayar da safar, dan yaji yana wani abu da hannun shi da yake kaikayin son taba kafarta yaji ko laushin da yake gani a idanuwan shi zaiji shi har a tafin shine ya sa yabi duka farcen daya yanke mata yana tattara shi ya saka a hannun shi guda daya ya mike ya nufi kitchen, ya kuwa yi sa'a akwai kwandon shara a ciki, ya zuba ya karasa sink ya wanke hannun shi, sai da ya bude fridge ya sake shan ruwa ya dan tsaya ya mayar da numfashi tukunna ya fito. Yanayin da yake ji ma ba zai iya zama ba

"Tafiya zanyi"

Ya fadi da wani sanyin murya da ya sa Madina kallon shi

"Tun yanzun?"

Ta furta, kai ya daga mata

"Baku gaisa da Daada ba"

Sai daya lumshe mata idanuwan shi yana sake bude su, tukunna ya girgiza kai

"Ki ce ina gaishe ta"

Mikewa Madina tayi, daman tace mishi ne ba dan ta sa rai zai amince ba, jiya ma sa'a taci bai musa ba ya shigo suka gaisa da Daadar, tama fi alakanta yardar shi da son sake duba jikin Daadar tunda taji ya mata wasu yan tambayoyi kan yanda take jin jikin. Shi ba ko yaushe yake son gaisawa da kowa ba, ko su Julde ma yana iya sati banda

"Daddy..."

Ko

"Nanna"

Da zai furta cikin sigar gaisuwa ya wuce, wata gaisuwa mai tsayi bata hada su ba, Khalid ma da suke bangare daya, yana iya gaishe da shi ya wuce batare daya amsa ba, ranakun daya amsa din kuma idan sun sake haduwa da yamma sai Khalid din yace zai kara gaishe da shi

"Wai ba ka gaisheni dazun ba?"

Ya kan fadi a zafafe, amman ko a jikin Khalid, da dare ma in ba ya watsa mishi zagi ba saiya kara gaishe da shi, baya so, ko kadan, tunda sun ga juna ai ya wadatar, kowa ya ga lafiyar kowa, meye na wahalar motsa labba in ba neman surutu da sassafe ba.

"Sai munyi waya ko?"

Madina ta bukata ganin ya shiga motar shi baice mata komai ba, yau yan rashin surutun sun motsa mishi, kai kawai ya daga mata yana jan motar shi, tsaye tayi da murmushi a fuskarta harya bace ma ganin ta. Hamman ta kenan, kamar mai aljanu, lokaci daya suna cikin hira zaiyi dif kamar bai taba surutu da ita ba, duk abinda zatace da kai zai ta amsa ta, karshe ma yace mata shi tafiya zaiyi, ko da wasa ranta bai taba baci ba tunda ta san haka yake, shisa yanzun ma ta koma cikin gida abinta, idan bai kirata ba, ita zata kira shi.

©

📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com
Whatsapp: 08074545149

*RAI DA KADDARA 1*

16

Ina son rubutu
Fiye da yanda duk kuke tunanin kuna son karatu
Ba yanga bace ba
Ba jan rai bane ba
Ba kuma dan naga ana son littafi na bane ba
Idan har banyi rubutu ba ina da uzuri mai karfi
Nagode da fahimtar ku.

*

Da farko tayi tunanin bugun da take ji cikin kanta kwakwalwar tace take kokarin yaki don samun hanyar fita daga kokon kanta bayan shafe tsayin daren da littafi rike a hannun ta, ba karamin mamaki tayi najin kiran assalatu a kunnen ta ba. Dakyar ta karasa azkar tana zuwa ta gaishe da Daada da fada mata kan ta na ciwo zata kwanta, ta kai wasu dakika kafin ta fahimci hayaniyar ba daga cikin kanta bane ba, bugun kofa ne da yake fitowa daga wajen dakin

"Ughhh"

Ta fitar da wani sauti daya fito daga makoshin ta, me yasa yanzun? Duk ranaku me yasa yau? Me yasa sanda take matukar bukatar jin shiru don samun rama ko kadanne daga cikin baccin da tayi sakacin rasawa a daren jiya? Hannu ta kai gefen gadon ta in da tasan gilashinta yana nan ta dauka ta saka a fuskarta ta batare da ta bude idanuwanta ba, dakyar ta iya sauko da kafafuwanta daga kan gadon tana jin kanta kamar an dora jakar kaya saboda nauyi.

Ba karamin yaki tayi da jikin ta kafin ya yarda ta rabashi da gadon ba, tana samu ta bude idanuwanta ta nufi hanyar kofar da bugunta yake ta karuwa. Sai da tayi wata hamma kamar da bakinta zata bude kofar sannan ta mika hannu tana murza hannun kofar tunda ba mukulli bane a jiki. Kafafuwan shi ta fara gani, babu takalma, sai alamar wandon farin yadin da yake sanye da shi, ta kasan gilashin tasa hannu tana murza idanuwanta, ta san mai kafafuwan, tana son dai tabbatar da ba bacci bane yake sakata gane-gane.

"Hamma kafar ka kamar ta mata, zatayi kyau da kunshi"

Maganar da ta taba fada mishi na dawo mata, tana sakata daga kanta ta sauke shi kan fuskar Nawfal da yake tsaye ya harde hannayen shi a kirjin shi yana kallon ta da murmushi a fuskar shi

"Hamma..."

Ta kira kamar wadda tayi gudu saboda mamakin ganin shi

"Daada tace kan ki na ciwo, nace karya kike, bacci ne bakiyi ba kin tsaya karatu"

Dariya tayi, kafin tayi murmushi mai sauti, tana sake wata dariyar saboda ba zatace ga abinda take ji ba, cikin su dai harda sautin bugun zuciyarta da take jin ya karu, da yakan karu ko da tunanin shi tayi, ko kuma taci karo da sakon shi a wayarta kamar yanda sukan yi magana ko da ba kullum bane tunda tayi tata wayar.

"Hamma..."

Ta sake kira a karo na biyu sauran kalaman na makale mata, ko jiya ya tambayi ya take ita da Daada, amman baice mata zaizo ba

"Ki koma baccin ki, zan ganki ne kafin in wuce"

Yanda ta zare mishi idanuwa yasa shi girgiza kai yana dariya

"Gida zanje in huta, daga airport nan nayo... Zan dawo sai anjima..."

Nata kan ta jinjina mishi da murmushin da yaki barin fuskarta har lokacin. Tana kallon shi har ya juya, tana jin tarin maganganun da take son fada mishi, amman ta rasa ta inda zata fara

"Hamma!"

Juyowa yayi

"Sannu da zuwa"

Dariyar shi ya sake yi, sai ta ga kamar ya kara canzawa, kamar shekaru sun nuna a jikin shi, ya kara yi mata girma. Ba kuma gashin daya bari a fuskar shi bane kawai, harda wata kamala da take tare da shi ko a yanayin takun shi ba wai iya fuskar kawai ba. Har ya fita daga falon tana kallon shi ta kasa komawa cikin daki, sai ma kofar da ta rike tana lilo a jikinta batare da ta sani ba. Lokacin da ta raba jikinta da kofar dakin Daada ta nufa tana samun ta a zaune rike da Qur'anin ta da Hizb biyu ne.

"Daada Am"

Ta furta cike da farin cikin da take ji ya cika zuciyar ta taf, ta karasa cikin dakin tana zama gefen Daada hadi da dora kanta a kafadarta kafin ta zame gabaki daya tana kwanciya a jikin Daadar

"Hamma ya zo"

Cewar Madina tana rufe idanuwanta, dayan hannunta Daada takai tana zare ma Madina gilashin da yake fuskarta

"Dagani ki koma kan gado"

Batayi musu ba ta tashi tana jan jikinta zuwa inda tasan gadon yake badan tana ganin komai yanda ya kamata ba, tunda babu gilashinta. Numfashi ta shaka, hancin ta na cika da kamshin da dakin Daada ne kawai yake yin irin shi, wani dan turare ne madara da tun tashin ta tasan Daada na amfani da shi, in ta diba ta shafa sai taji kamshin bai mata a jikin ta ba, ta daifi son ta shigo dakin Daada ta kwanta ta shaki kamshin anan, ko ta kwanta a jikinta, sai taji shi ya bambanta, har tunani take ko wasu mutanen na da nasu kamshin ne.

Dan in dai hakane to da Salim da Daada suna da wannan kamshin nasu na daban, ita bata da tarar turare, kowanne iri ya sha gabanta amfani takeyi da shi in dai taji yayi mata dadi, tana da su kala-kala, Adee ma in dai zataje tayi mata kunshi bayan kudin da sai sun kai ruwa rana take karba sai ta hada mata da turaruka, Julde kan siyo mata shima, haka Daada, Salim kan shi ba zata kirga adadin lokuttan da ya bata kyautar turare ba, duk kuwa da ta littafai ta shallake kowacce kyauta da take giftawa a tsakanin su.

Ita kam tasan bata da wani tsayayyen kamshi, zata iya jera sati kowacce rana da kalar turaren da zata fesa, amman banda Daada da Salim, kamshi daya sukeyi ko da yaushe, in dai bana jikin su bane ba, to ba karamin kokarin su take gani wajen yin amfani da kalar turaren da har ya zame musu jiki haka ba. Nawfal ba zata tantance yana kamshi ko bayayi ba, saboda kamshin shine karshen abinda yake zuwa mata duk in zata gan shi, takan samu bugun zuciyar ta daya kan karu ya koma mata dai-dai ne, zuwa lokacin kuma sun shiga wata hirar da take saka mata manta duk wani abu da yake wakana a wajen abinda suke tattaunawa.

"Me kika ci?"

Madina tayi tambayar a tsakanin hammar da ta subuce mata

"Kwai na soya na sha shayi"

Sake gyara kwanciya tayi, tasan akwai ruwan zafi a flask tunda ita ta dafa da daddare, kuma Julde da yazo ya kawo musu biredin da tafi so mai kwakwa, shisa ma ta koma baccin ta bayan tayi sallah dan tasan Daada zata sha shayi babu wani abu da zatayi banda share-share in ta

gama baccin. Lumshe idanuwan ta tayi, Daada na kallon ta, ko ba bacci takeyi ba yanzun da babu makaranta sai takai karfe tara na safe bata karya ba, yau gashi goma na neman yi. Baccin kuwa Madina ta koma dan shine a idanuwanta.

**

A gidan Daada yabar akwatin shi saboda ba zai iya daukar kayan ba a yanda yake jin shi. Jakar ratayawar kawai ya dauka. Kudin da ya sallami mai mashin din daya kaishi gidan daga airport ma a wajen Daada ya karba, haka wanda zai kaishi Hotoro. Murmushin da yayi ma maigadi ma yanajin yanda ya bayyana kan fuskar shi da duk gajiyar da yake tare da ita kafin ya wuce shi yana kara ma takun shi sauri. Harya daga hannu zai kwankwasa kofar yaji muryar Salim cikin kan shi

"Dole sai kun kwankwasa zaku shigo?"

Murmushi yayi yana kama hannun kofar da tunanin watakila Salim din ma yana falon. Tunanin shi baiyi karya ba kuwa, zaune Salim din yake ya jingina bayan shi da kujerar, hannun shi na rike da remote, yanda idanuwan shi suke a lumshe yasa Nawfal tura kofar a hankali dan yaga kamar bacci yake. A hankali ya karasa shiga cikin dakin, farar rigar da take kan hannun kujera ta tabbatar ma da Nawfal din Salim daga wajen aiki yake

"Ina jin idanuwan ka a fuskata"

Salim yai maganar yana sa Nawfal ja da baya saboda ya dan tsorata shi

"Hamma mana..."

Ya furta yana saka Salim din bude idanuwan shi daya sauke su kan Nawfal

"Sai ka gama kare mun kallo zaka wuce? Me yasa mutum ba zaiyi bacci a nutse a falon nan ba?"

Kallon shi Nawfal yake yana murmushi kafin ya bude hannayen shi yana nufar inda Salim yake zaune hadi da fadin

"Na dawo lafiya, kuma nima nayi kewar ka Hamma"

Yanda Salim din ya zaro idanuwa yana kaucewa ganin da gaske Nawfal rungumar shi zaiyi yasa Nawfal din sauke hannayen shi yana kwashewa da dariya, har kirji Salim ya dafe kamar yaga wani babban abin tashin hankali, wucewa ciki Nawfal yayi ya karasa dakin su, komai a hargitse yake, babu datti dai, amman ko ya rantse bayajin zaiyi kaffara, anfi wata rabon da a gyara gadon. Kwanciya kawai akeyi ana tashi, da zanin gadon da bargon duk sun hade sun cakude waje daya. Numfashi ya sauke yana zame hannun jakar shi daga kafada ya sauke ta

kasa.

Sai da ya fara rage kayan jikin shi tunda farin yadi ne manyan kaya. Yabar singileti da gajeran wando tukunna ya hau gyaran dakin, ya dauko wankakken zanin gado ya shimfida, wannan din dama wasu kayan Khalid din da yayi tunanin masu dattine ya tattara yana saka su cikin kwandon da ya ajiye a dakin don zuba kayan dauda da Khalid baya amfani da shi. Har shara ya sake ya dauki turaruka kala biyu ya fesa. Wanka ya shiga ya fito, wata singiletin ya samu cikin jakar shi da gajeran wando ya saka, da yake babu kaya suna gidan Daada cikin kayan Khalid ya samu wata bakar riga marar nauyi ya saka a jikin shi, bai wani bi takan wando ba dan bayajin Khalid na da wandon da zai mishi.

Yanayin jikin su ba daya bane ba, yafi Khalid tsayi, kuma ya fishi jiki. Kafafuwan Khalid sosai suke mishi kama da sandar snooker, amman bai fada ba saboda Khalid zai zage shi. Kitchen ya nufa saboda yunwar da yake ji, banda shayi baiga wani abu da zai iya ci ba, yunwar da yake tare da ita tafi karfin shayi. Shisa ya fito falon wajen Salim da yanzun ya kwanta kan doguwar kujerar yana fadin

"Hamma ka bani mukullin motar ka da kudi in fita in siyo wani abu, yunwa nake ji"

Hannu Salim yakai ya laluba kujerar da yake kwance a kai yana mika ma Nawfal din mukullin

"Wallet dina na cikin motar, akwai kudi a ciki"

Karba Nawfal yayi

"Zan taho maka da wani abu?"

Numfashi Salim ya sauke

"Ka kyaleni Bajjo"

Juyawa Nawfal yayi yana komawa dakin su, dakyar ya iya samun wani 3 quarter da yake tunanin na shine ya saka ya fita. Cikin abokan da yayi yan Najeriya acan sai yaji suna maganar yanda suka ga komai ya canza da sukaje gida, har wasu na nuna kamar aiwatar da hidimar yau da gobe a kasar Najeriya tana musu wahala. Da idanuwa Nawfal yakan bi su kawai. Saboda in yai magana tashi zata iyayin zafi, duka shekarar su nawa a kasar wajen? Shekarun da sukayi a Najeriya ya ninka wanda sukayi a can.

Karatu ya kai shi, yanzun kuma daya kammala ya dawo, yana da tarin burukan da yake son fitowa da su daga cikin kan shi, shisa ya dawo, shisa bai bata lokaci ba duk kuwa da yanda yake ganin son hakan a idanuwa Murjanatu. Zaman su basu fara shi da boye-boye ba, ta sani, tun farko ya fada mata zaman kasar waje ba nashi bane ba, ta yarda, ta aminta da inda duk ya saka kafafuwan shi zata bishi.

"Turai na tana tare da kai Gidado, in da duk zan saka kafa idan taka bata biye ba zanji dadi ba, zan fi so ace ka cire kafar ka ne a wajen kafin in dora tawa"

Ba zai manta yanda ya riketa a jikin shi ba, kamar yanda kalaman ta suka samu wajen zama a zuciyar shi. Bai bata lokaci ba, duk da yana jin shi kamar dan koyo saboda yanayin tukin nan da can ba daya bane ba, taka manyan dokokin tuki ba wani abu bane a wajen mutane da yawa a Najeriya balle kuma wasu kananu, ya sha zagi yafi a kirga daga fitar shi zuwa dawowar shi, dariya kawai suka dinga bashi. Sai da ma ya tsaya inda yaga alamar ana saida kati ya siyi sabon sim din MTN ya kuma siyi katin da zai saka a ciki.

A hankali ya tura kofar dakin ya shiga, sai dai Salim baya falon, shisa ya wuce dakin su. Zagi zai sha idan yace yaje ya kai mishi mukullin mota ko da kuwa ba bacci yakeyi ba. Dankali ya siyo soyayye da gasasshen kifi sai ice cream roba biyu, canjin da ya rage ma Salim a wallet din gabaki daya dari takwas ne. Ba magana zaiyi ba ya sani, ko da kudin sun fi haka, Salim din ya koya musu kashe kudin shi kamar suna kashe na su. Ko motar shi ka shiga, ko dakin shi, abinda duk yai maka in kasa hannu ka dauka Salim ba zai kalle ka ba.

Sosai yaci ya koshi, ya dauki dayar robar ice cream din shi ya kai cikin fridge yana komawa daki. Wayar shi ya dauka ya ciro sim din shi yana saka MTN din, ya kumayi loading din katin, data ya siya saboda zaifi mishi sauki yayi ma Murjanatu magana ta whatsapp, in yaso ita sai ta kira shi daga nata bangaren. Yana budewa kuwa sakkoninta suka fara shigo mishi, sunfi goma, biyu daga cikine na tambayar lafiya da ko ya sauka lafiya, sauran na yanda take kewar shi ne. Murmushi yayi, yana amsa kowanne a ciki.

In tana haka wani sai ya dauka ita kadai take kewar shi, idan yace mata yanda duk take ji bai koyi rabin abinda yake ji ba sai tace zatayi mishi gardama. Sake tura mata wani sakon yayi yana fada mata zai kwanta, zai kuma saka wayar a silent. Dan karta kira ta ga bai dauka ba. Dan kan shi ya fara nauyi, kan gadon ya hau yaja bargo yana rufe kafafuwan shi hadi da lumshe idanuwan shi kafin bacci mai nauyi ya dauke shi.

*

Ba sai wani ya fada mishi ba, yanayin yanda yaga dakin tsaf ya san aikin Nawfal ne.

"Cikin satin nan fa nake son dawowa"

Nawfal din ya fada mishi

"Allah ya bamu aron lokacin"

Shine amsar da ya bashi, idan ya tambaye shi cikin satin wace rana zai iya cewa shima bai sani ba. Kawai abinda ya sani shine cikin satin zai dawo. Da wahala Nawfal ya tsayar maka da

lokaci, ko ya sakama abu lokaci, zai dai fadi abinda yake hasashen zai iya faruwa. Basu kuma sake maganar ba dan lokacin duk da zasuyi waya ko suyi chatting sai yayi musu karanci, zantukan su ba masu karewa bane ba. Da shi ya wuni a wajen aiki yau, duk wani abu da za'ace maka alfarma da kudi basa yin shi a Najeriya zai iya karyatawa.

Dan yagani akan bautar kasar shi, Julde kawai ya sanarwa baya son barin garin Kano, camp din ma da ake zama shi bai zauna ba, a ASAD pharmaceuticals ltd da yake nan Kano yayi bautar kasar shi da bai shige watanni da kammalawa ba, kuma sai yayi sa'ar samun gurbin aiki tare da su, ya karba tunda albashin babu laifi yana da kyau. Ba nan yake hari ba, asibitin Aminu Kano yake so, zai kuma nema da zarar ya kammala digiri din shi ta biyu da yake jiran a fara siyar da form ya nema.

Tunda yana hangen kacokan abincin shi a bokon yake gara ya zage dantse ya nema da kyau, kafin ya sauke numfashin da ya shaka an kwankwasa kofar

"Shigo"

Ya furta yana kwance agogon da yake daure a tsintsiyar hannun shi

"Kabani charger din ka Khalid, na bar tawa a asibiti"

Jikin bango inda socket yake Khalid ya karasa yana ciro cajar, shisa yake da guda uku, daya a mota, daya a gida dayar kuma a office din shi dan gudun samun irin wannan matsalar tunda ya san halin shi da mantuwa. Abu muhimmi ma mantawa yake balle kuma wata cajar wayar da in ba kiran shi akayi ba saiya wuni baibi takanta ba

"Dole sai kayi zanzaro?"

Salim ya tambaya da murmushi a idanuwan shi duk da yanata kokarin ganin bai karasa kan labban shi ba, kugun shi Khalid ya kalla kafin ya daga kai ya kalli Salim

"Me zanzaro na yayi?"

Kai Salim ya girgiza, idan yayi magana dariya zaiyi, kwanaki yaga Lukman na kallon wani cartoon a bangaren Saratu, ta gefen ido yaga giccin wani a ciki sai da ya dawo baya ya kara kallo da kyau, ya kwana biyu ko shi kadai yake zaune sai yayi dariya saboda kamar sun kalli kugu da kafafuwan Khalid ne kafin suyi zanen. Har yanayin belt din da yake da yakinin sai da Khalid ya kara huda a jiki sannan ya zauna. Duk gidan babu siriri irin Khalid, ya gama makarantar amman yaki yin kumari.

Cajar ya karba yana share kallon rashin fahimtar da Khalid yake mishi, har ya juya ya dawo

"Randa duk ka zo asibitin mu, in dai da wannan zanzaron ne, kar ka cewa kowa gidan mu daya

Khalid, dan Allah kace kawai kana nemana"

Bude baki Khalid yayi, kafin yace wani abu Salim yaja kofar, numfashi yaja ya fitar yana jinjina kai

"Bakomai, Allah na ganin ka Hamma"

Ya furta a hankali yana kwance belt din ya cire shi hadi da zaro rigarshi waje. Salim baya bude bakin shi ya fadi maganar da zaka so kaji, yanzun da hirar arziki ce da wahala in ba zai zage shi ba yace ya saka shi magana. Amman da yake ci masa mutunci yayi niyyar yi ya bude baki ya fadi abinda babu wanda ya tambaye shi. Har yayi wanka ya fito yana tunanin yanda duk shekarar babu wanda yayi mishi irin zagin da Salim yayi mishi. Masallaci ya fita yayo sallar Magriba ya dawo.

Inda Nawfal yaje yake tunani, ko gidan Daada zai kwana ne? Ya tambayi kan shi kafin ya dauki wayar shi da nufin kiran Madina yaji ko Nawfal din yana can sai gashi ya turo kofar da sallama, kafa ma ya saka, hannuwan shi rike suke da ledoji

"Madina zan kira yanzun inji ko kana gidan Daada"

Kai Nawfal ya girgiza mishi yana zare takalman shi a gefe ya sake amfani da kafar shi ya tura kofar. Kasa ya zauna kan kafet yana ajiye ledojin da Khalid ya kawo hannu da nufin dauka Nawfal din ya janye gefe da sauri

"Ba hali me kyau bane wannan Hamma... Daga ajiye abu"

Kafar shi Khalid din ya saka yana harbin Nawfal a baya kafin ya sake kai hannu yaja ledar

"Hamma mana!"

Ko inda yake Khalid bai kalla ba

"Ka aike ni ne?"

Robobine na take away da zafin su rau na kuwa, fito da su Khalid ya shiga yi

"Gidan Adee kaje"

Ya fadi yana saka Nawfal din kallon shi

"Robobin gidan ta ne wannan, dan ita kadai naga tana amfani da irin su"

Kai kawai Nawfal ya jinjina

"Allah ya yafe maka halin nan da ka kwaso"

Jin Khalid din bai kula shi ba sai ma roba daya daya bude yasa shi dorawa da

"Bakin halin da ka koya nake nufi"

Kafar dai Khalid ya sake sawa yana kai mishi harbin daya kauce wannan karin yana dariya. Yayi kewar su, yayi kewar gida da dukkan zuciyar shi. Zama haka a daki daya da Khalid kawai na kara tuna mishi da duk wani dalili da yake da shi na dawowa gida, duk wani dalili da babu inda zaije ya kira gida sai Najeriya. Yana gama baccin shi Adee ya fara kira, ita kadai ya fadama yana airport, dan sunyi hira ma har sai da ya shiga jirgi. Mashin tace yahau suka hadu a hanya dan ta fito karbar ma mijinta wani sako da aka aika mishi daga Abuja.

Har miyar da zata mishi wajen kwana hudu Adee tayi mishi, da farfesun kifi mai yawa. Takarcen da ta hado mishi tsayawa yayi kawai yana kallon ta

"Kafin matar ka ta dawo ne..."

Ta fadi tana dariya, murmushi kawai ya iya yi mata, kuma ta dawo da shi, danma sai da ta tsaya a hanya yayi sallah a wani masallaci tunda ta san yanda baya son rasa sallar a cikin jam'i in ba da wani babban dalili ba. Adee bata shiga gida ba, saboda shine kuma, tare da Adee ba saiya furta abubuwa da yawa ba, ba sai yace mata bai shiga bangaren Saratu ba, ta sani. Idan suka shiga tare dole zaiji kamar bai kyauta ba, shisa taki shiga dan ta kara mishi lokacin da yake bukata.

"Kai ba zaka ci bane ba?"

Khalid ya bukata yana katse ma Nawfal tunanin da yakeyi

"Bangane bana ci ba? In zo da abu kana mun wannan tambayar?"

Zaman shi Khalid ya gyara yana jinjina kai hadi da tsoma hannu cikin robar farfesun kifin daya bude yana fadin

"Okay..."

Ganin da gaske yake yasa Nawfal din mikewa. Gudun kar suyi bari yasa Khalid sauke robar kasa suka ci tare kafin su fita sallar isha'i su dawo.

"Bari inga me aka dafa"

Cewar Khalid, har Nawfal ya jinjina mishi kai zai wuce bangaren su sai kuma ya fasa

"Muje nima ban shiga ba"

Sai da Khalid yayi mishi kallon da yake fassara ka tabbata yaga ya da dan daga mishi kai tukunna ya shiga gaba shikuma Nawfal na biye da shi har bangaren Saratu da suka shiga tare da yin sallamar da ta amsa, yanayin fuskarta na sauyawa lokacin da ta dora idanuwanta kan Nawfal. Zaune take kan kujera da dan karamin kwano a hannun ta da farfesun naman rago ne ta zubo, tama tsame duk naman, romon ne take dan diba da cokali tana sha.

"Nanna..."

Nawfal ya furta, Khalid na karbewa da

"Sannu da gida"

Ya wuce hanyar kitchen da sauri, idon dai Saratu ta kafa mishi cike da tambayoyin da ya rasa wanne zai fara amsawa duk da bata furta su ba.

"Da zun na zo, ina wuni"

Ya ce cikin sanyin murya

"Lafiya lau"

Ta amsa a takaici tana dauke idanuwan ta daga kan shi alamar ta gama bashi iya lokacin da take tunanin zata iya. Juyawa yayi da nufin barin dakin, zuciyar shi yake jin babu dadi, ita kadai ta tsane shi, duk duniya ita kadai ta tsane shi kuma bai san dalili ba, tunanin duniya yayi ko zai tuna wani abu daya taba yi mata banda zama karkashin kulawar mijin ta da Kawun shi ne, yana da hakkin da zai rike shi ko da ba ita yake aure ba. Me yayi mata da zafi haka?

Numfashin kirki ma bayajin yana shaka in tana waje saboda gudun kar sautin shi ya takura mata, yana da rai amman idan Saratu na nan kokarin gani yake ya zama gawar da ba zata iya gani ba, duk dan ya gujema bacin ranta. Ya gaji, bai san yanda ya gaji ba sai yau din nan. Shisa ya koma yana takawa yaje har kan kujerar da take zaune mai daukar mutum uku ya zauna a gefe yana dora murmushin da bayaji a zuciyar shi kan fuskar shi

"Na dawo ne gabaki daya Nanna, ba nida nufin zama a garin Kano saboda dalilai da yawa, zaki cigaba da gaba da gani na lokaci zuwa lokaci saboda banda yan uwan da suka wuce su Hamma, ban san me nayi miki ba, koma menene ba zai taba zama dalilin da zanyi nisa da yan uwa na ba, yaran kine duka, kiyi hakuri zaki cigaba da raba su tare dani..."

Ya karasa maganar yana mikewa ya nufi hanyar kitchen din, yanajin yanda take bin shi da kallo, nauyin da yake ji a kirjin shi duk idan yagan ta yaji ya daga mishi, tsanar da tayi mishi zabinta

ne, ya gaji da raba nauyin tare da ita. Taje ta dauka ita kadai, ko babu wani abu ta bashi su Khalid, shisa take kasancewa cikin addu'o'in shi. Tana da wannan darajar a idanuwan shi, fridge ya bude yana daukar ruwa roba daya

"Zuba abinci ne kamar zaka dafa sabo"

Ya ce ma Khalid da yake rike da filet a hannu

"Ina ruwan ka?"

Khalid din yace, Nawfal ya amsa da

"Babu"

Yana ficewa daga kitchen din, murmushi Khalid yayi, ranar farko da yaji dadin karfin halin da Nawfal yayi. Sai dai yana juya maganar Nawfal din da yace bashi da nufin zama a garin Kano, ina yake nufin zai zauna? Shi bai fada mishi ba, watakila sai sun samu zama tukunna. Koma ina ne in dai yana kasar komai zaiyi dai-dai. Tuwon shinkafa ne, zubawa yayi yana dibar malmala biyu dan shi bai cika rike mishi ciki ba, yana iya kai sha biyu a zaune yaji yunwa.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com
Whatsapp: 08074545149

*RAI DA KADDARA 1*

17

Dakyar yake iya daga idanuwan shi, ya san Allah ne kawai ya tsare mishi hanya daga asibiti zuwa gida

"Idan ka gaji haka ka dinga kwanciya a asibiti ko baccin awa biyu ne kayi tukunna ka hau titi, ko ka kira Hamma Khalid ya zo ya dauke ka"

Rokon da Madina tayi mishi kenan kwanaki tana dorawa da

"Kaji Hamma, dan Allah, kaji"

Bai amsa ta ba, saboda inya amsa zai zama kamar yayi mata alkawari ne. Bacci a asibiti ba zai iya shi ba kamar yanda yaga sauran abokan aikin shi sunayi, saboda akwai hayaniya, duk da ofishin shi ne can karshe, amman karar takun tafiya na zirga-zirgar mutane kamar cikin kunnen shi akeyi haka yake jin su, yana iya jiyo karar wayar wani daga ofishin shi. Duk kananun hayaniyar nan ba zai iya bacci a cikin ta ba. Tun kafin ya tura kofar ya jiyo sautin hayaniyar da yake da tabbacin tv ce a kunne.

Da tsaki a bakin shi ya tura kofar, sai da ya dan runtsa idanuwan shi saboda karar da yaji ta sa kan shi sarawa. Nawfal na zaune kan doguwar kujera ya jingina bayan shi sosai, yanda idanuwan shi suke a rufe ya tabbatar ma da Salim din bacci ne ya dauke shi, wani sautin mamaki Salim ya fitar yana karasawa cikin dakin sosai ya kai hannu ya dauki remote din da yake gefen Nawfal ya rage karar tv din gabaki daya sannan ya zauna gefe don ya zare takalmin da ke kafar shi.

Yana jin wata iska da ta ratsa kafafuwan tun kafin ya cire safar shi, numfashi ya sauke yana jin wani na mishi wahalar shaka saboda Nawfal da ya doro kan shi a kafadar shi batare daya yi tsammanin hakan ba, kafin yayi wani motsi Nawfal din ya zagaya hannuwan shi duka biyun a damtsen shi yana kara kwantawa a jikin shi

"Ina ta missing din ki"

Nawfal ya fadi cikin bacci, shima gajiyar ce a tattare da shi. Bai taba hasaso cewa haka kafa kasuwanci yake da matukar wahala ba sai yanzun da tun wajen karbar lasisin shi na tuki ya fara jin kan shi na nauyi, balle kuma daya fara zirga-zirga tsakanin Kano da Kaduna tun da nan din ya zaba a matsayin garin da zai zauna ya kuma kafa kasuwancin na shi

"Me yasa sai Kaduna? Duk fadin Kano Bajjo? Baka ganin wasu daga Kadunan suna dawowa Kano don kafa kasuwancin su, ka zabi duk inda yayi maka a Kano zan sai maka fili idan akwai, in babu zan sai maka ko meye a wajen in dai zasu siyar mun saika rushe ka gina abinda kake bukata, ina da kudin, in banda su kai kana da kudin... Kaduna tayi nisa"

Julde ya karasa maganar muryar shi dauke da nauyin da yake ji a zuciyar shi

"Kadunan dai nake so Daddy, ai babu wani nisa fa, zan zo in ganku duk sanda nake so. Don Allah karkace a'a, kamun addu'a kawai"

Yana kallon yanda Julden yake kokawa da zuciyar shi kafin ya jinjina kai a hankali

"Allah ya zaba abinda yafi alkhairi, amman ka kara tunani dai"

Shima ya amsa ne da to ba dan akwai wani tunani da zai kara ba. Ya dauke shi tsayin shekara daya kafin ya yanke hukunci zama a Kadunan. Tun kafin ya dawo kuma yake binciken hanyoyin da komai zai zo mishi da sauki. Sai dai ko da kudi ba zasu zamar mishi matsala ba, hanyar tana

da tsayin da bai hango ba. Yau din ma yana dawowa ruwa ya watsa ya fito da nufin shiga kitchen ya hada shayi, sai ya zauna ya fara hutawa tukunna, bai san lokacin da bacci ya dauke shi ba. Kamar jiya ya zo, gashi harya shafe watanni biyu da dawowa amman bambanci lokaci ya kasa barin shi.

Da daddare idanuwan shi kamar an soya gyada a ciki, amman da rana kamar an bubbuge mishi gwiwoyin kafa haka yake ji saboda baccin da zaita dawainiya da shi. Sunyi waya da Murjanatu yana hanya, da tunanin yanda yake kewar ta ya shigo gidan, har bacci ya dauke shi ma yana tunanin yanda zata matsa mishi kafafuwan shi da suke a gajiye da tana kusa. Shisa kwakwalwar shi tayi mishi tunanin itace yaji ta zauna a gefen shi kamar yanda ta saba. Suna da bambanci lokuttan dawowa gida, tana rigan shi fita, yana kuma riganta dawowa.

Ranaku da yawa sai tsakiyar dare take komawa, saboda yanayin karatun su ma ba daya bane ba, kuma in ta tashi daga makaranta zata wuce aikin da takeyi na awa uku wani lokacin awa hudu, ya danganta da yanda take jin gajiya

"Bajjo..."

Salim ya kira a tsakanin jan numfashi da saukewa saboda ya kawo iya wuya. Amman kamar ya tunzura Nawfal din daya kara riko shi

"Jikina ciwo yake"

Cewar Nawfal din, hannun shi Salim yake kokarin fisgewa amman rikon da Nawfal yayi mishi bana wasa bane ba, shisa yayi amfani da gwiwar hannun da yake rike da shi din ya zungure shi a hakarkari, babu shiri ya bude idanuwan shi yana kokarin gane inda yake da kuma abinda yake faruwa, a hankali ya juyo ya kalli Salim da yake watsa mishi wata irin harara da yasan yana gab da kwada mishi mari idan bai daina koma meye Salim din yake tunanin yanayi ba, hannuwan shi da suke sakale da na Salim ya kalla yana tunanin abinda sukeyi a wajen.

Bai san ihun da yayi cikin kan shi ya subuce mishi ba sai da yaji sautin shi a kunnen shi, hannuwan shi na nuna mishi bai isa da su ba saboda sun ki sakin Salim din

"Ba zaka sakeni ba dan uban ka? Sai na karya ka tukunna ko?"

Sai lokacin ya saki Salim din yana mikewa cikin hanzari

"Me kake anan?"

Nawfal ya tambaya cikin tashin hankali, wani irin kallo Salim din ya watsa mishi

"Me yasa baka tasheni ba?"

Ya dora yana yarfe hannuwan shi hadi da goge su jikin rigar shi, kai Salim ya jinjina, an kwana biyu wani bai raina mishi hankali haka ba, ganin yanda ya mike yasa Nawfal din rugawa da gudu

"Ka dawo kaji me yasa tashe ka ba"

Cewar Salim din yana kallon Nawfal da har ya kai bakin kofar dakin su. Kwafa yayi yana komawa kan kujerar ya zauna

"Karka dawo falon nan"

Salim ya fadi yana kwanciya akan doguwar kujerar, yasan in yayi wanka da ruwa mai dumi sosai sai yafi jin dadin baccin, amman kan shi yayi mishi nauyi ba kadan ba.

"Hamma dan Allah... Shayi zan hada sai in koma daki"

Nawfal yayi maganar daga in da yake tsaye

"I will kill you if you make another sound"

Dariya Nawfal yayi yana nufar kitchen, kafin ya gama hada shayin Salim ya kira

"Bajjo!"

Cike da kashedi ya kuma watsa mishi zagi yafi sau biyar. Da gangan ya buga kofar dakin su wajen rufeta yana jin zagin da Salim din yayi mishi, dariya yayi ya saka mukulli a jikin kofar dakin. Yasan har yanzun baiyi girman da Salim din zai ki cin zalin shi in ya so ba, ko kafin ya tafi Kaduna da ya zo ya same shi kwance a falo yana kallo sai da ya kai masa wani duka da ya wuni yana murza wajen

"Bana hana ku zama a falon nan ba"

Da bai saurin tashi ba wani dukan Salim zai sake kai mishi. A ka'ida falo nasu ne su duka, amman tuni Salim ya hada ya mallake da nashi dakin. Ko wucewa zakayi in yana kwance saika dauke numfashi kar kayi ya karasa kunnen shi. Da suna zama suyi kallo in yana dakin shi, ya zo ya hana saboda basa rage karar tv din a cewar shi, yana jin surutan har cikin kwakwalwar shi kar wanda ya sake zama. Shayin shi Nawfal ya shanye ya kwanta ya dan runtsa ko na awa daya ne tunda yaga har biyar ta wuce, yasan dai zai tashi jikin shi yayi mishi nauyi.

**

"Kin siyi jamb?"

Fatima Atiku ta tambayeta lokacin suna rubutu Neco, kai kawai ta girgiza mata. Ita bata ga saurin da dalibai da yawa masu zana jarabawa sukeyi ba, tun kafin ma ta shiga aji shiddan tana ganin sauran dalibai na wannan zumudin. In tace bata hango rayuwar jami'a da yanda zata kasance mata zai zamana karya, amman banda haka bata wani zumudin shiga ko doki, a ganin ta makaranta dai duk makaranta ce, karatu kuma karatu ne, babu wani abu da zai canza mata, yanda bata da wasu da zata kira abokai haka ma acan din bata jin zata samu wanda zata kira da wannan sunan.

Ta fi so sakamakon jarabawar ta su ya fito tukunna, ta ga taci duk wani abu daya kamata kafin tayi wata jamb, har Salim sai da yayi mata maganar

"Ni nafi so jarabawa ta fito ne Hamma"

Kallon ta yayi

"Zaman me zakiyi a gida Madina? Da kinyi jamb din, result na fitowa a shekarar nan ma zaki iya samun admission"

Shi yayi mata bayanin muhimmanci yin jamb din shekarar da ka zana jarabawa, amman yayi mata bayani a kurarren lokaci tunda har an gama saidawa, ko da ba'a gama saidawa ba sai dai tayi saboda shi bawai don ko daya a cikin bayanin ya gamsar da ita ba. Ta fi son bin komai a hankali, kuma daki-daki. Yanzun kuwa dadin hutun ma take ji, daga islamiyya sai in tana da wanda zatayi wa kunshi da kusan kullum ne, da dare tana da isasshen lokacin da zatayi karatu tunda tasan zata koma bacci da safe in ta gama aikin ta.

Bambanci da yake cikin kowacce rana a wajen ta shine yawan mutanen da ta yiwa kun shi sai kuma sabon abinda zata karanta. Banda wannan kullum iri daya ce, abu iri dayane. Sai kuma Daada da take ganin kamar tana ramewa, kamar kuma akwai rashin kuzari a yanda take gudanar da al'amuranta ba kamar da ba, kusan kullum sai ta kai hannu ta taba fuska ko wuyan Daada dan taji idan akwai zazzabi sai taji lafiya kalau. Yau ma kuwa hakanne ya faru har ta sa Daada yin murmushi

"Na ce miki lafiya ta kalau Madina"

Numfashi Madina ta sauke

"Kina ta ramewa Daada...ko dai in kira Daddy muje asibiti a kara duba ki"

Dariya Daada tayi

"Allah da gaske, ni gani nake kina ta ramewa"

Kafin Daada ta amsa sallamar Nawfal ta katse ta

"Hamma dan Allah ba Daada ta rame ba?"

Madina ta tambaya bayan ta amsa mishi gaisuwar shi, kallon Daada yayi sosai, yana kula da yanda shekaru suka nuna a fuskarta, bai gani ba da, amman akwai rama a fuskarta, duk da ita din ba mai jiki bace ba tunda can ma, amman fuskarta a cike take, yanzun kam har hancin ta da yake dogo ya kara fitowa, kana ganin kwanciyar karan hancin daya fara tun da tsakiyar girar ta

"Baki da lafiya ne? Jikin ne?"

Kai ta girgiza musu

"Ku me yake damun ku ne?"

Saboda bata son damuwar da take kan fuskokin su

"Kuma bata yin komai da hanzari kamar da fa"

Madina ta fadi

"Yarinta nake karawa ne kullum? Jikin girma ne, kuyi addu'ar samun jiki me kyau irin nawa"

Dariya sukayi gabaki daya, duk da a kasan ta Nawfal akwai damuwa, waje ya samu gefen Madina ya zauna har lokacin sai kallon Daada yakeyi, musamman yanda sai da ta dafa kujera sannan ta iya mikewa dakyar kamar tana jin nauyin jikinta

"Bacci ma nake ji ni kam"

Shagwabe fuska Nawfal yayi

"Ko gaisawa ba muyi ba Daada shine zaki tashi? Ba zaki zauna muyi labari ba?"

Murmushi tayi

"Ai nasan kana nan har in tashin... Wacce gaisuwar? Ba gani ba ka ganni ina lafiya, kaima kuma nagan ka kana lafiya"

Kai kawai Nawfal ya jinjina yana sauke numfashi, har ta shiga daki bai daina kallon in da ta bari ba, haka kawai sai yake jin zuciyar shi tayi nauyi. Sai dai bai ce wani abu ba har akayi sallamar da ta sa Madina mikewa tana fita tsakar gidan dan ta ga ko waye ya shigo, sanda ta dawo yaja kafafuwan shi ya dora su kan kujerar

"Kunshi zanyi Hamma, in zuba maka abinci?"

Kai ya girgiza mata, bayajin yunwa, wayar shi ya ciro yana kwanciya kan kujerar sosai ya shiga whatsapp yana sake kallon hotunan da Murjanatu ta turo mishi yana murmushi shi kadai, har Madina ta shiga daki ta dauko kayan kunshin ta, ta sake ficewa bai ma kula ba. Bai san lokaci na wucewa ba musamman da Murjanatu kamar ta duba zuciyar shi ta ga yanda yake kewar ta ta zo online. Earpiece din shi da bai cika mantawa ba ya ciro a aljihu ya saka saboda ta kira shi video call.

Sallar la'asar da aka kira ne ya sa shi yi ma Murjanatu sallama yana mikewa yaje ya dauro alwala, batare da ya kalli matar ko yarinyar da ta gaishe shi ba ya amsa yana wucewa, dan lokacin ma kokarin maida links din hannun rigar shi daya bude wajen alwala yake yi. Ita ma sallar ta mike taje tayi, don sallah na daya daga cikin abinda bata wasa da shi. Sanda ta karasa ma matar hudu kusan da rabi. Kudin da ta bata cikin wata jaka taje ta zuba, abinda take siye bashi da yawa, Julde na bata kudin kashewa sosai, Salim ya sa taje ta bude account a banki, shi ya dauketa sukaje tare. Yanzun ma idan kudin kushin sun kai dubu biyar ko fiye da haka sai ta fada mishi yazo ya kaita taje ta saka a ciki.

"In sun taru da yawa zakiyi wani abu mai muhimmanci da su"

Salim din ya fadi, sai da ta fara tarawa tukunna zuciyarta ta raya mata tarin abubuwan da take son tayi da kudin in har sun kai mata yawan da take fata.

"Kunshi kamar kina ma mutum goma, tun dazun"

Nawfal ya fadi bayan ta shiga falon ta samu waje ta zauna

"Kasan wahalar kunshi ne Hamma?"

Kallon ta Nawfal yayi

"Bawani wahala, ai na iya"

Dariya Madina tayi, sosai dariya ya bata

"Ka iya me? Bafa zanen kujeru ba Hamma, kunshi...kunshi irin wanda mata sukeyi"

Kai Nawfal yake jinjina mata tunda ta fara magana fuskar shi babu alamar wasa

"Ni nake yiwa Jaan, kuma kowa ya gani sai yace yayi kyau"

Duk da taji wani iri a zuciyarta bai hanata cigaba da dariya ba

"Baki yarda ba kenan? System dina dayan daya baci ne nake da hotunan da kin gani"

Dariyar dai Madina ta cigaba da yi mishi

"Ki dauko kayan kunshin ki kawo hannun ki kisha mamaki"

Mikewa tayi ta nufi dakin ta tana dauko jakar kayan kunshin, akwai saura da yawa a kwarkwaron da tayi ma matar na bakin lalle ta kuwa mikawa Nawfal da ya sauko daga kan kujera shima yana zama kan kafet suka fuskanci juna da Madina da ke kokarin gintse dariyar ta tana son ganin iya ina Nawfal zai kai da maganar ya iya zanen lalle kafin ya fito ya fada mata wasa yake. Fuskar shi babu alamar wasa ya ware mata tafin hannun shi na hagu yana daga mata girar shi duka biyun. Wani irin tsalle zuciyar tayi kamar tana son bayyana kan fuskarta, hakan ya sata saurin sadda kanta kasa tana jan siririn numfashi, hannun nata da taji yana zufa ta goge jikin wandon ta sannan ta dora shi kan na Nawfal.

Salim ya sha rike hannunta, a rana sai ta rike hannun Daada babu adadi, tafin ta ne kawai kan na Nawfal, amman ji takeyi kamar ta dora shi kan murfin tukunyar da aka sauke daga wuta, dumin na gangarawa har cikin wani lungu a zuciyarta da sai yau ta san da zaman shi. Fuskar shi ta ke kallo da yanda ya nutsu akan hannun ta kamar a duniya kaf bashida wani abu mai muhimmanci da yafi zanen da yake mata, wannan karin duka jikinta taji ya dauki dumi sai kace zazzabi na shirin kamata.

Yawu ta hadiye tana dan daga wuya da nufin hango abinda Nawfal din yake zana mata ya kuwa sake yin sama da hannunta yana fadin

"Kibari in gama Malama"

Dariya tayi

"Karka bata mun hannu Hamma, ka tsaya inga me kake"

Kafada Nawfal ya makale mata yana saka idanuwan shi cikin nata

"Allah ki tsaya in gama"

Kai ta jinjina mishi haka kawai tana jin ba zata iya musu da shi ba. Duka bai kara minti goma ba yayo kasa da hannunta dai-dai lokacin da zata hadiye yawu, ta kuwa sarke wajen kokarin yin dariya, duk da haka ta kasa dainawa, taurari ne Nawfal ya zana mata, daya kwandalele a tsakiyar bayan hannunta, sai yayi yan kanana daga gefe, haka jikin kowanne yatsa yayi karami guda daya

"Inalillahi..."

Ta fadi tana cigaba da dariya, turo baki Nawfal yayi dan baiga abin dariya ba

"Kowa a makaranta yana tambaya wanda yayi mun kunshin nan"

Murjanatu tace mishi, tunda da a yatsunta kawai take saka ja idan ta siyo, shi yace ta kawo ya zana mata, batayi musu ba kuma ta bashi, da kanshi yake kirkirar zane kala-kala, mai taurarin shine yake ganin yafi kowanne kyau, ko kafin ya taho duka hannuwan Murjanatu biyu saida yayi mata, da yan yatsun kafa ma

"Gidado ka kware da kunshin nan yanzun, kaga yanda na kafar yayi kyau"

Har sumba ya samu ta godiya. Sai Madina ce zata saka shi gaba da dariya

"Hamma... Hamma.. Meye wannan?"

Tayi tambayar a tsakanin dariyar da takeyi, kwarkwaron ta ya ajiye mata yana komawa kan kujera ya kwanta

"Ai sai kiyi tayi tunda baki san abin arziqi ba"

Mikewa Madina tayi da sauri tana nufar dakin ta ta shiga bandakin da yake ciki ta bude famfo ta saka hannun, sai dai ya riga ya fito, zai kuma yi aqalla kwana uku ko hudu bai gama fita gabaki daya ba ko da tana yawan amfani da ruwa. Dariya kawai takeyi, tana fitowa daga bandakin taji wayarta da ta bari cikin dakin tana ruri, da sauri ta karasa ta dauki wayar, muryar ta dauke da dariya ta ce

"Hamma..."

Bayan ta kai wayar kunnen ta

"Ina kika je? Ina ta kiran ki. Ke da wa kike dariya?"

Dariyar ce ta sake kubce mata

"Ina nan fa, nabar wayar a dakine, na ma wata kunshi sai nima akayi mun..."

Sai dai kafin ta gama dariyar da ta sake kubce mata ta bashi labari harya katse ta

"Kunshi? Kikayi? Wayayi miki?"

Salim ya jera mata tambayoyin a numfashi daya

"Hamma Nawfal fa.. Wai ya iya, yana ma matar shi, kaga abinda ya zana mun a hannu?"

Ta karasa tana dariya, shirun da taji ya biyo bayan maganar ya sata fadin

"Hello..."

Har sau biyu tana sauke wayar daga kunnen ta dan tunaninta kiran ya katse sai taga sakanni suna tafiya, sake mayarwa tayi

"Hamma... Bana jin ka fa. Ka kashe ka sake kira"

Numfashi taji ya sauke cikin kunnenta, muryar shi can kasan makoshi yace

"Ina zuwa"

Kafin ma ta amsa taji alamar ya katse kiran daga bangaren shi, cajarta ta karasa ta ciro tana daukar wayar ta nufi falo, har lokacin da murmushi a fuskarta.

**

Baiyi tunanin kafafuwan shi zasu dauke shi daga dakin su zuwa na Salim ba saboda rawar da sukeyi, tashin hankalin da yake ciki bai barshi ya tuna cewa ana neman izini kafin a kwankwasa daki ba, turawa kawai yayi yana samun Salim a tsaye da alama wanka ya fito ya sake kaya

"Bajjo..."

Salim ya kira ganin tashin hankalin da yake shimfide a fuskar Nawfal din

"Hamma..."

Nawfal ya kira yanajin zuciyar shi akan harshe

"Meye? Menene?"

Numfashi Nawfal ya sauke

"Hamma Khalid..."

Kokawa yake da sauran kalaman

"Hatsari sukayi...ya kirani....banaji sosai... Hamma ina ta kira ba'a dagawa...ba'a daga wayar"

Mukullin motar da yake kan gado Salim ya dauka, Nawfal baya bukatar Salim yace mishi ya wuce, gaba yayi yana bin shi a baya har suka fita daga gidan. A wajen ajiye motoci suka ci karo da Julde da zai fita, tashin hankali bai hana su duka biyun jin kamshin da yakeyi ba. Ganin

Salim bashi da ko takalmi yasa shi tambayar

"Lafiya? Ina zaku? Me ya faru?"

Salim ne ya iya amsa shi da

"Khalid ne yayi hatsari"

Wani irin rugugi Julde yaji cikin kirjin shi har hanjin cikin shi na taya zuciyar shi amsawa. Su duka ukun motar Salim suka shiga, dan Julde baya ya bude yana zama. Sai da suka hau titi sannan Salim yayi tunanin bai ma san inda zasu nufa ba

"Yana ina? Ina akace maka yake?"

Kafada Nawfal ya dan daga

"Nima ban sani ba, mu bi hanyar wajen aikin shi kawai"

Kallon shi Salim yayi

"Baka da hankali ne? Kasan hanyoyi nawa ne zaka iya bi zuwa Asad?"

Kamar Nawfal zaiyi kuka yace

"Dan Allah ka zabi daya kawai kabi Hamma, kayi sauri"

Dayar kuwa ya zaba yana karanta duk wata addu'a da zata zai iya tunawa, tashin hankali bakon abu ne a wajen shi. Ya sha ganin mutane a asibiti suna faduwa suna tashi akan tashin hankali idan sun kawo yan uwan su, ko kuma ya fada musu rasuwar wani makusancin su, sai dai ya kalle su kawai saboda ko da wasa ma baya son ya hasaso me suke ji, don hakan na nufin ya saka kan shi a takalmin su, ya kwatanta da wani na shi, ba zai iya ba, baya so ya ma iya. Sai gashi yau yana zaune tashin hankalin ya same shi har cikin gida. Daman zuciyar shi a jagule take tun wayar da yayi da Madina. Kai ya girgiza dan ba wannan bane abu mai muhimmanci yanzun.

Suna hawa titin Kawaji kuwa suna ganin cunkoson da aka hada a wajen, gurin ya cika, ko gefen hanya Salim bai samu ya sauke motar ba, a tsakiyar titi ya tsaya suna fita daga ciki gabaki dayan su. Sai da yaji shigar kwalta a tafin kafafuwan shi tukunna yagane cewar bai saka takalmi ba. Runtsa idanuwan shi kawai yayi yana fitar da numfashi, ta tsakanin mutane suke kutsawa. Nawfal najin kafafuwan shi na kara yin sanyi da duk takun da zatayi

"Trailer ce akace ta kwace duk ta bi takan motocin nan"

Ya tsinto muryar wani yana fada a cikin mutanen yana sa makoshin shi bushewa kamar an zuba yashi. Julde ya fara hango Khalid a tsugunne ya hade kan shi da gwiwar shi, har tuntube yakeyi wajen kokarin ya karasa wajen shi, Nawfal kam jinin da yake gani ya kara daga mishi hankali

"Khalid..."

Julde da Salim suka kira lokaci daya suna sa Nawfal kallon inda suke, dagowa Khalid din yayi, har idanuwan shi sun zurma ciki saboda tashin hankali. Shi da yamma ma ya kamata yabar wajen aikin, sai abokin aikin shi ya kira cewar yar shi bata da lafiya suna asibiti, shine ya karbe shi har daren, cunkoso ya samu akan hanya, tsaye motar shi take kamar ta sauran mutane da dama, da kuma babura, ba zaice ga abinda ya faru ba, ihu da kara kawai yaji sai motar shi da yaga tana gaba da kanta, ashe trailer din data kwace sai ta danne motocin da suke can bayan su, da tafiya ake kilan sai hatsarin yafi haka muni.

Sanda wani ya bude motar shi ya fisgo shi ya juya bayan shi ya dora idanuwan shi kan wani mutum da kafar shi ta fita kasa motsawa yayi, tsaye yayi yana kallon yanda ake zaro mutane musamman masu mashina daga karkashin motoci, tunda yake bai taba ganin tashin hankali irin wannan ba. Nan take zazzabi mai zafi ya rufe shi, tunanin ya kira Nawfal ne ya zo mishi, sai da ya ma rasa abinda zaice mishi, bai san ya kiran ya kare ba ko ya akayi ya samu waje ya tsugunna, kawai yasan ko kifta idanuwan shi yayi sai ya dinga ganin mutane da jini na gifta mishi

"Khalid..."

Salim ya sake kira yana kama hannun shi ya mikar da shi tsaye

"Kaji ciwo? Ina kaji ciwo?"

Yake tambaya yana bin jikin Khalid din da kallo

"Daddy..."

Khalid ya kira da dukkan zuciyar shi yana jin yanda babu wani girma da zaiyi a duniya da za'ace baya bukatar lallashin iyayen shi. Karasawa Julde yayi da sauri

"Kaganni nan Khalid, baka ji ciwo ba dai ko?"

Kai Khalid din ya daga mishi yana jin wasu hawaye masu zafi da suka cika mishi ido, da shikenan fa, karshen ganin da zai musu yau da safe kenan, dan Adam da gaske ba abakin komai yake ba, kana tafiya ajali yana bibiyar ka, ko tsautsayi, duka tarin mutanen da tsautsayin ya fadama sun bar gidane batare da sanin ba zasu koma ba, iyalai da yan uwa suna can suna dubar hanyar komawar su, wasu sai dai suji ana sallamar su matsa za'a shiga da gawa, ko suzo asibiti kaza su dauka. Ko ina jikin shi bari yakeyi, wani irin tsoro na shigar shi.

Bashi da rabon wahala, amman bayan motar shi gabaki daya ya molaqe, ba dabarar shi ba, ba komai ba, ko addu'ar fita daga gida bai tuna yayi ba yau din. Allah ne kawai ya kubutar da shi

"Baka ji ciwo ba?"

Julde ya sake tambaya, kai Khalid ya daga mishi, kamar haka Nawfal yake jira ya tsugunna saboda kafafuwan shi da yaji shima sunyi sanyi. Fuskar shi ya saka cikin hannuwan shi yana jero duk wata kalar godiya da zai iya wa Ubangiji da ya tseratar da Khalid din

"Meye kai kuma? Ka tashi Bajjo, baka gan shi ba? Lafiyar shi kalau babu abinda ya same shi"

Kai kawai Nawfal yake dagawa Salim din amman shi kadai yasan yanda zuciyar shi ta girgiza, baka isa ka hana kaddara yin aikinta akan makusancin ka ba, amman in zaka iya bayajin shi kam zai bar ko tsinke ya soki Khalid. Sai da Salim ya kamashi shima ya mikar

"Ku taho ku koma mota..."

Cewar Salim yana jan rigar Nawfal din, Julde ya kama hannun Khalid, bayan suka shiga su biyun. Julde ya rufe bangaren Khalid yana daga kan shi yayi nasarar saukewa akan Mero da hasken fitilar wata mota ya haska mishi fuskarta dai-dai lokacin da ta shiga gaban wata mota tana rufe murfin tare da bude wani abu a cikin kirjin Julde da kafafuwan shi suka fara daukar shi

"Mero... Mero Na"

Ya furta a kasan numfashi

"Daddy... Ina zaka je kuma?"

Salim ya tambaya, amman ko jinshi Julde baiyi ba, mutane yake turewa yana ratsa tsakanin motocin da suke wajen, kafin ma ya tsallaka har anja motar anyi gaba, wani mashin ya dafa yana mayar da numfashi, shekaru goma sha sai yau ya dora idanuwan shi akanta, kafin ya maida numfashin da yake fatan zai dan nutsar da bugun zuciyar shi yaji an dafa shi

"Daddy... Lafiya kuwa?"

Salim ya tambaya yana ganin fuskar Julden ta kara mishi haske kamar babu jini a jikinta

"Lafiya?"

Ya sake tambaya, kai Julde kawai ya daga mishi

"Mu tafi gida kawai, gobe na dawo in duba motar Khalid da safe..."

Kan dai Julde ya sake daga mishi, bai yarda da muryar shi ba shisa bai amsa ba, haka suka karasa, Salim ya bude mishi gaban motar ya shiga. Zuciyar shi kamar kara bugawa take a cikin kirjin shi.

Ashe zai sake ganin Mero?
Ko dai alama ce kaddara take nuna mishi?

"Inajin kamar don kai kawai aka halitta mun zuciya a kirjina, ko dan kai ta fara numfasawa? Wanne irin so nake maka dana watsar da maganar kowa Julde?"

Kalaman ta kenan
Kalaman da suka zauna mishi
Kowanne RAI da tashi KADDARAR.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com
Whatsapp: 08074545149

*RAI DA KADDARA 1*

18

Da idanuwa Saratu take bin shi ba tun safiyar ranar ba, tun sati biyu da suka wuce saboda tambaya babu irin wadda batayi mishi ba akan me yake damun shi yana amfani da damar wajen nuna mata cewa da gaske bata da wani muhimmanci a wajen shi. A tsayin shekarun auren su zata kirga adadin lokuttan da yayi rashin lafiya har ya kwanta, a cikin adadin zatace sau daya ya taba wadda ta kai shi da kwanaki a kwance, wannan kuma rashin lafiya ce da take son shafewa a kundin tarihi idan har tana da halin haka.

Sai kuma satikan nan da suka wuce da alamu duka suka nuna cewa ba ciwo yake ba, ya dai koma kamar wani gunki-gunki ne, abinci haka zai ta wasa da cokali a ciki, a yinin rana baifi ya saka ruwan shayi da yar wainar kwai a cikin shi ba, satin farko ya jera kwanaki hudu yana fita tunda sassafe sai yammaci liqis zai dawo, kafin daga baya ya koma rabuwa da kan gadon dakin shi ma sai yaji su Khalid a falon ne zata ga yayi ta. Suna kuma fita zai koma ya sake bin gadon ya kwanta. Har daki take bin shi da abincin safe, rana da na dare. Yau na safen da na ranar duka haka ta zo ta dauke ta sake fita da su, babu alamar da ta nuna ya ko bude balle ya ci.

Rashin muhimmanci da take da shi a wajen Julde ba sabon abu bane, abune da lokaci bai sa ta daina jin ciwon shi ba, wannan karin dai tunanin halin da yake ciki shiya danne mata ciwon da take ji. Ta na son shi, ta na son Julde fiye da yanda kalamai zasuyi mata adalci wajen misaltawa, saboda ko wulakancin shi na yau da kullum bai dakushe tasirin soyayyar shi a zuciyar ta ba. Na dole sun dawo wuni cikin dakin kamar marassa gaskiya, bai kore ta ba, yanda yake nunawa ma kamar bai san tana cikin dakin ba tunda ko inda take baya kallo.

Ta kai zuciyar ta nesa dai wajen ganin bata yi komai daya wuce taya shi zama a cikin dakin ba. Tana kallon shi bayan la'asar ya shiga bayi, tana nan zaune ya fito, idanuwan ta suka fara sauka kan fuskar shi da ta manta rabon da ta ganta babu gashi, a kwanakin nan ma ta cika sosai saboda bai damu da yunwar cikin shi ba balle wata sumar fuska, yanzun ya kwashe komai, ko fuskar Lukman akwai gashin baki daya fara fitowa luf da shi, har tana tsokanar shi a kai ma. Fuskar Julde da bayan kwai basu da bambanci. Haka kawai sai yanayin ya hasko mata wani hoto da yasa zuciyar ta bugawa kamar tana neman hanyar fita daga cikin kirjin ta.

Tabbas shekaru ba karya bane ba, don sun nuna kan su a tare da Julden, bata san ko idanuwanta bane suka rage wannan shekarun akan fuskar shi suna dai-daita mata fuskar da hoton da take da shi a cikin kanta. Bambancin ba a zanen fuskar yake ba, a sarkar da babu ita yanzun a wuyan shi ce, kayan fulanin da yake sakawa a wancen lokacin, sai kuma askin kan shi da yake kasa sosai, sabanin wancen lokacin da ya tara gashin, bayan kadai ake ragewa an tado gaban yayi tozo irin na samarin fulani da suke ji da kan su a wancen lokacin. Julden ta, Julden da zuciyarta ta zaba tun kafin ma tayi wayon sanin haka.

Mata da yawa na son maza masu kasumba, maza da yawa sukan ce cikar kamala ta da namiji kenan, musamman magidanci kamar Julde, in ba dalili na aikin kaki da kan hana ma wasu mazan yin hakan ba, banda Saratu, a yau, a yanzun kuma ban da ita

"Kayi kyau"

Kalmomin biyu da tayi nufin furtawa a zuciyarta suka kubce mata suna kuma saka Julde sauke idanuwan shi da yanayin da yake ciki bai sa farin su canzawa ba, kyallin na shigar mata wani waje da bata san da shi a zuciyar ta ba, har yana sata gasgata maganar cewa so baya tsufa da masu azancin magana suke yawan fada

"Da ka aske sumar sai kayi kyau"

Ta furta muryarta na sauke kasa tunda kalaman farko suka subuce sai suka bata kwarin gwiwar furta sauran. Har lokacin dai kallon ta yake yi, tun kafin ya san menene soyayya, tun kafin Mero yake ganin soyayyar shi a idanuwan Saratu, a irin wannan lokacin a baya da take fito mishi da asalin kaunar da take mishi ya sha tambayar kan shi dalilin da yasa ya kasa mayar mata ko da kadan ne daga cikin tarin soyayyar da ya gani, kuma ya san tana mishi. Watakila da ta rage mishi radadin rashin Mero da yake fama da shi.

Da bai gan ta ba, da bai sake ganin ta ba da bata fama mishi tsohon ciwon da yake riritawa ba, kamar mahaukaci haka ya dinga zagaye unguwar da ya ganta yana tambayar duk wani wanda zai tsaya ya saurare shi ko ya ganta ta hanyar zayyana mishi kamannin ta, a idanuwan mutane mabanbanta yaga mamakin da suke da ya kasance cikin shiga ta kamala, ko kadan alamu basu nuna cewa yana dauke da cutar rangwamen hankali ba, amman daga ya bude  bakin shi sai kalaman shi su sha bamban da kamammin shi. Ziyara ta zo, ya san iya wannan in ba kuma dalili ya raba auren da tayi a Kaduna ba kamar yanda yake fata.

Har yanzun, yana kuma jin har abada Mero zata kasance rike da kaso mafi girma na zuciyar shi da duka walwalar shi. Baiyi karya ba da ya taba ce mata

"Ina jin kamar ban san farin ciki ba sai da kika shigo rayuwa ta Mero"

Akan ta ya fara sanin menene asalin farin ciki kafin ya samu su Salim da suka karasa cika mishi abinda ya rage na daga cikin farin cikin. A yanzun kuma duk wata yar walwala da yake yi a duniya su ne sanadi, su kadai yake kallo ya samu nutsuwa. Ko sauran matan da yake bibiya baya samun nutsuwar da yake nema a tare da su, kamar akwai wani duhu da yake mamaye da shi ya hana mishi sukuni.

"Ko kana sha'awar cin wani abu?"

Maganar Saratu ta kutsa ta cikin tunanin shi

"Idan anyi sallah ki kira su Khalid sai muci gabaki daya"

Yana kallon murmushin da tayi tana daga kai hadi da mikewa ta fice daga dakin, da zai iya da ya so ta, ko kadan da ya so matar nan. Amman ba zai iya ba, lokaci dai ya koya mishi sabo da ita, amman babu soyayyar ta ko daya a cikin zuciyar shi, akwai dai jin ko na rana daya ya kamata yayi mata godiya, da ta bashi su Salim, da ta ke tare da shi tana kula da gidan shi duk fitowar rana da faduwar ta. Ta cancanci ko da iya wannan jinjinawar ne.

Komai da sanyi-sanyi yake tayin shi, sanda ya gama shiryawa cikin wani farin yadi da ya karbi jikin shi har ana kiran magriba, fita masallaci yayi, bai hadu da kowa ba wajen dawowa sai Khalid da suka taho tare, Nawfal daman ya saba ya zauna masallaci bayan Magriba wasu ranakun ma har sai anyi isha'i yake dawowa. In kuma bai tsaya ba to sai ya gama duka azkar din shi, Khalid ya sha zama tare da shi sai yaga ya samu waje ya jingina bayan shi da bangon masallacin, kamar akwai wata nutsuwa ta daban da sai a cikin masallacin ya ke samun ta.

"Ku zo muci abinci, ka fada ma su Bajjo"

Julde ya cewa Khalid daya daga mishi kai

"Yanzun kuwa... Me Nanna ta dafa?"

Kai Julde ya girgiza mishi

"Ni ma ban sani ba fa..."

Yana ba Khalid din dariya kafin su rabu kowa ya wuce bangaren shi. Sanda Julde ya shiga har Saratu ta shirya teburin cin abincin mai mazaunin mutum takwas. Kujera yaja ya zauna. Ya kusan mintina goma kafin Khalid da Nawfal su shigo da sallamar da ko amsa musu Julde baiyi ba suka cigaba da maganar da sukeyi

"Ni fa bana son wannan tattare-tattaren da kake mun... Jiya ba akan gado na ajiye takardar ba? Saboda idan na zo in dauka, yanzun duk ka hade su waje daya..."

Kallon shi Nawfal yakeyi

"Kan gado wajen ajiye takarda ne Hamma? Kan gado fa? Meye amfanin teburin dakin?"

Kafin Khalid daya daga ido a zafafe ya amsa, Salim ya rike wuyan kowannen su da hannun shi, yana saka su fadin

"Hamma mana..."

A tare

"Tun kafin in shigo nake jin hayaniyar ku...sai kace kaji"

Nawfal ya fara zamewa sannan Khalid, babu shiri kowa ya samu kujera ya zauna, Khalid na sa kafa cikin kokarin ture kujerar Nawfal daya zauna kusa da shi

"Daddy kai ma Hamma magana"

Kallon su Julde yakeyi fuskar shi dauke da murmushi, yanajin wani abu daya kulle mishi kirji yana sassautawa

"Kai da baka ma jin yunwa? Me ka zo yi?"

Khalid din ya amsa

"Idan banzo ba waye zai takura maka?"

Wannan karin Khalid din ne ya kalli Julde

"Kana jin shi ko Daddy? Kana jin me yake cewa"

Khalid ya karasa yana kaima Nawfal dukan daya kauce yana dariya

"Har yanzun kun kasa wuce shekara sha biyu"

Lukman daya karaso wajen ya fadi cikin harshen fulatanci yana tsayawa kan kujerar da Nawfal yake hadi da fadin

"Ka koma can Hamma"

Akwai wani yanayi tattare da Lukman da yake saka kowa yi mishi abinda yake so, ko sanyin halin shine ko kuma kwarjini ne daya ke yalwace saman fuskar shi duk da karancin shekarun shi. Tashin Nawfal yayi, Lukman ya ja kujerar yana zama a tsakiyar Khalid din da Nawfal kafin ya gaishe da Salim da Daddy

"Lukman ba'a ganin ka sam"

Nawfal ya fadi, har mantawa yake Lukman yana gidan, sai ya ga giccin shi

"Ina nan Hamma"

Ya amsa a takaice yana mikewa dan yaga alamar kamar ba yunwa suke ji ba, shi ko abincin rana baici ba, cake ne kwara daya yaci a makaranta. Bubbude warmers din yayi, shinkafa ce da miyar kaji, sai kamshi yake tashi, in dai girki ne Allah ya hore ma Saratu, gashi tana son yin shi, ko wani gidan taje aka bata abinda bata sani ba bata girman kai take tambayar sunan shi da kuma yanda akeyi, hakan ne ya sa ta kara gogewa da abincin gayu kala-kala. Lukman ya zuba ma kowa yana kallon Nawfal daya girgiza mishi kai a hankali. Zai so yaci abinci a cikin su, sai dai ko kifi aka saka ba nama ba a abincin haramiyar shine tunda ya san akwai yaji.

Numfashin da ya shaka yaji yaki kaiwa in da ya kamata da zuwan Saratu wajen, yana kuma jin illar hakan a muryar shi lokacin daya furta

"Nanna..."

Cikin sigar gaisuwa. Bata kalle shi ba, amman ta amsa da

"Bajjo"

Salim da yake kusa da Julde ya mike ta zauna a kujerar shikuma ya zauna a ta kusa da ita

"Na bar wayata a daki, za'a iya kirana"

Yace yana mikewa batare daya kalli kowa ba balle yaga yanda suka san karya yake, suka san

uzuri ne dan kawai ya bar wajen tunda Saratu ta zo, babu kuma wanda yayi yunkurin hana shi, akwai abubuwa da yawa da lokaci yake koya maka ciki kuwa harda kiyaye halayen makusancin ka. Yanda duk Saratu da Nawfal zasuyi kokarin boye rashin kaunar da yake tsakanin su idan wani yana nan, duk su Khalid din na fahimta, kamar yanda suka san daga Saratun har Nawfal sun san biye musu kawai sukeyi. Fitar Nawfal tayi dai-dai da dagowar kan Salim yana sauke idanuwan shi cikin na Khalid da suke shimfide da tuhuma, shakku da alamar tarin tambayoyi.

Baya so, tun shekaranjiya Khalid yake bin shi da idanuwa haka, har yau ya so kauce ma dawowa gidan ya kwana. Ocean Palace guest Inn ne karshen in da yai tsammanin wani wanda ya san shi zai gan shi balle kuma Khalid

"Nagan ka Hamma... Na ganka yau"

Khalid din ya fadi, ba shi bane karo na farko da wani a cikin shi ko Nawfal suka ce sun ganshi, sai dai a shekaranjiyan kawai sai yaji zuciyar shi tayo tsalle zuwa makoshin shi da ya bushe lokaci daya yana kuma neman yawun da zai samu ya jiqa shi ya rasa

"Nagan ka"

Khalid din ya sake maimaitawa muryar shi dauke da wani abu da Salim bai taba tunanin zai gifta a tsakanin su ba

"Kila ya kamata in nuna kamar ban gan ka ba, kamar banga yarinyar da ka hada da jikin ka ba Hamma, amman ba zan iya ba, ban san ya zanki maka magana ba. Kace mun iya abinda nagani ne kawai...dan Allah kace mun iya abinda nagani ne kawai bai kai inda tunani ya nufa ba..."

Duk kalma daya da Khalid din zai furta wani irin abune yake lullube Salim, ko dai haka kunyar da yaji mutane na fada take shisa ya kasa daga idanuwa ya kalli Khalid, a karo na farko a rayuwar shi da yake son kasa ta bude ya shige ciki akan ya fuskanci Khalid a yanzun. Rabon da yaji kamar abinda yake bashi da kyau har ya manta sai a lokacin. Yana jin numfashin da Khalid ya ja ya fitar

"Hamma..."

Ya kira zuciyar shi a shimfide cikin yanayin yanda ya kira sunan Salim din, bai daga kai ba, kasa yake kallo, haka Khalid din bai sake furta komai ba ya juya kawai. Amman tun shekaranjiya din yake bin shi da irin wannan kallon tuhumar duk haduwar da zasuyi, banda gaisuwa wata kalma bata gifta a tsakanin su ba sai yau din nan, shima ya san saboda su Nawfal suna wajen ne. Ya sa shi yanajin babu dadi tun shekaranjiya, abinci ma ya daina gane dandanon shi saboda taraddadin da ya kasa fassara kona menene takamaimai.

Yanda Salim baiyi tsammanin ganin Khalid din ba haka shima. Dan dakyar ma ya gane wajen

da kwatance da komai. Wani abokin aikin shine kirista dan kabilar Igala yake aure a cikin satin, to abokan shi da suka zo daga garin su sai suka sauka a wannan Guest Inn din. Akwai takardun daya manta bai bari ba a wajen aiki kafin ya dauki gajeran hutun, sune ya roki Khalid da zaije dasu hotel din da yaje ya karba. Saboda nisan wajen ma yana tafiya yana jan karamin tsaki harya karasa, kawai dan dai Michael din yana da kirki, bashi da matsala sam, amman Khalid na daya daga cikin mutanen da kunya bata cika saka su yin abinda zasu takura ba.

Ya kira Micheal din kuma yace mishi baima karaso wajen ba, shine abinda ya saka shi zama cikin mota in da yayi parking yana jira, kalle-kalle yake yanda ake shige da fice, mata da maza a hade. Waje irin haka ya kamata ace ya zama wajen da uzuri zai iya kawo kowa, amman ya kasa kauda zargin da yake ma matan da yake ta gani suna shige da fice daga cikin hotel din, watakila tare da mazajen su suke, watakila sako suka zo karba kamar yanda yayi, ko wani uzurin mai tsafta, amman bata gari sun riga sun fesa ma waje irin wannan ruwan da har abada jirwayen shi ba zai taba wankewa ba.

Idanuwan shi da yake ta yawata wa yana kalle-kalle ya sauke kan wata jar mota da baiga lambar ba, amman sak irin ta Salim, sai dai baya tunanin akwai abinda zai kawo Salim wajen nan, watakila ma yana asibiti ko gida a wannan lokacin. Kafin Salim din ya fito yana karyata tunanin Khalid da ya kama murfin mota zai bude da nufin fita ya karasa wajen Salim din, yarinyar da yaga ta sakala hannunta a kugun Salim na saka duk wani abu da yake kirjin shi amsawa cikin yanayi marar dadin misaltawa. Dakyar ya iya runtsa idanuwan shi yana sake bude su dai-dai lokacin da Salim ya juyo da yarinyar da duka alamu suka nuna bambancin addini da yare a tsakanin su,Khalid na sake runtsa idanuwan shi babu shiri

"Inalillahi wa ina ilaihi raji'un"

Ya iya furtawa saboda ba zaiga hoton da baisan yanda zai fara goge shi daga cikin kan shi ba, jikin shi ko ina bari yake saboda tashin hankali. Wacce irin bakar rana ce wannan yaci karo da ita? Me zai gani? Salim? Hamman shi? Hamman shi da kimar shi take kamar jirgin sama a wajen shi har sai ya daga kai yake iya hango nisanta, me yasa ya zo wajen nan? Me yasa kimar nan zata ruguzo a saman kan shi kamar daman bata da nauyin rike kanta a saman shi? Me yasa Salim ma zai karya mishi zuciya haka?

"Kar kayi saurin yanke hukunci"

Wata murya da bata da kuzari ta karfafe shi, bayajin wani lokaci mai tsayi ya wuce, amman ji yayi kamar zamani ne ya zo ya wuce yana nan zaune saboda tashin hankali, sanda ya daga kai baiga yarinyar ba, baiga Salim ba sai motar shi da yake ja yana fita daga wajen. Ko ringing din wayar shi Khalid baiji ba, Allah ne ya taimaka Micheal din ya hango shi zaune cikin mota, idan yace ga yaren da suka gaisa ciki zaiyi karya, ya karbi file din dai, ko sallamar kirki baya tunanin yayi da Micheal balle ya tambaye shi ya shirye-shiryen bikin shi suke tafiya. Duka wannan abubuwane da muhimmanci yayi baya yana tazara mai nisa da abinda Khalid din yake ji.

Da sanyin da jikin shi yayi yake tuki har gida. So kawai yake ya shiga ya tambayi Salim dan ya karyata mishi abinda ya gani, dan ya tabbatar ma da tunanin shi abinda ya gani a wajen Guest Inn din ne kawai. Amman sai shirun Khalid din ya karfafa tunanin shi yana ruguza wani bangare na zuciyar shi. Saura wa kuma ya rage yayi disappointing din shi haka? Sosai zuciyar shi ta sosu, ba farin cikin duniya kawai Salim yake wasa da shi ba, har lahirar shi ma lilo takeyi amman yake rayuwa kullum kamar babu mala'iku har biyu a kowanne gefen shi, kamar baisan suna rubuta duk wani motsin shi ba.

Rashin tsoro irin na dan adam abune mai ban al'ajabi, ko wani abin Khalid yayi da yasan babu kyau sai yazo kwanciya yaji kirjin shi na bugawa cike da taraddadi, kan shi na wankewa yana barin tunani kwara daya tak, zai iya runtae idanuwan shi na har abada, baccin da zaiyi da nufin ya wayi gari zai iya bude idanuwan shi a cikin kabari. Ta ya mutane masu tarin zunnubai suke rayuwar yau da kullum kamar ba zasu hadu da Allah ba? Abin da al'ajabi, ba kadan ba. Laifin na Salim ne amman shi ya kasa bacci duk tsayin daren, ga zuciyar shi da take zafi.

Kwanakin nan biyu haka yake yin su a daddafe kawai, ko da sukai waya da Nawfal shekaranjiyan wajen tara sai da ya tambaye shi me yake damun shi

"Gajiya ce kawai"

Amman ya san Nawfal bai yarda ba shisa ya dawo garin jiya. Yanayin yanda yake ta tsokanar shi yana sanar mishi da cewa ko meye yake damun shi in dai yana son su tattauna Nawfal din a shirye yake da ya saurare shi, in kuma yana ganin zai iya shawo kan abin shi kadai ma Nawfal din ba zai matsa ba. Tsintar kan shi yayi da godewa Allah da Nawfal ya kasance jinin shi, mutum daya kuma da yake da yakini mai karfi akan cewa ba zai taba karya mishi zuciya kamar yanda kowa yake ta zabar yi ba.

Ganin Salim din na ta wasa da cokalin shi cikin abinci yasa Khalid ture na shi plate din, daman ba wai yana jin wata yunwa bane ba

"Har kayi me? Shisa kake ta kara ramewa kullum"

Julde ya fadi, murmushin karfin hali Khalid yayi, kafin ya amsa Lukman ya riga shi da fadin

"Meye babu a fuskar ka Daddy?"

Saboda tun dazun yake ganin kamar akwai abinda ya kamata ace akwai a fuskar Julden, hakan yasa daga Khalid har Salim kallon Julde kafin Khalid ya kwashe da dariya

"Inalillahi... Daddy waye yai maka wannan yankar kaunar?"

Murmushi Julde yayi, bai san dalili ba, amman ji yayi kamar idan ya aske gashin fuskar zai rage nauyin da kirjin shi yayi, kamar ita kanta sumar na da wani nauyi na daban da bai taba sani ba,

banda iska da yake ji tana shigar mishi fuska ta ko ina babu abinda cire gashin yayi mishi

"Ni na aske abu na, furfura ta fara cika shi, shine na aske sai baki ya fito"

Wannan karin har Salim sai da yayi dariya

"Nanna kina ganin shi ya aske?"

Khalid ya tambaya, murmushi Saratu tayi, bata cika saka musu baki a irin wannan lokacin ba, saboda a cikin shine take samun ganin dariyar Julde, ta kuma ji zolayar shi da bai taba gwadawa a kanta ba, sai taga kamar wani ne daban ba mijin da ta aura ba, ba mijin da take zaune da shi ba kuma. Ko dan wannan ba mijin ta bane ba, mahaifi ne tare da yaran shi, ubane da kaunar yayan shi take a bayyane.

"Ko da ya aske din dai babu wanda zai nuna mishi kyau a cikin ku"

Lukman ne ya fitar da wani sauti a kasan makoshin shi da ya sake saka Khalid fashewa da dariya

"Son kai dai Nanna"

Cewar Salim

"Son Daddy dai zaka ce"

Khalid ya amsa suna hada ido, yanayin da yake tsakanin su na sake giftawa kamar labulen da su kadai suke ganin shi. Kamar yanayin ya ba Khalid damar mikewa dai-dai lokacin da suka fara jiyo kiran sallar isha'i

"A gajiye nake ni kam, ina dawowa sallah zan kwanta. Sai da safen ku"

Cewar Khalid din yana dan amsa tambayar Nanna da take mishi na ko karfe nawa zai fita da safe kafin ya juya yana barin dakin. Sai dai bai koyi minti biyu ba yaji takun tafiya a bayan shi da yasa shi juyawa

"Khalid..."

Salim ya furta sauran kalaman da bai gama hadawa a cikin kan shi ba suna makalewa, wani abu ya kamata yace, amman shi din ba mai yawan magana bane tun da can, balle kuma magana irin wannan da bai taba tunanin zata hadasu da Khalid ba. Murmushin da bai kai cikin idanuwan shi ba Khalid yayi

"Bani zaka yiwa bayani ba Hamma, ba fahimta ko yafiya ta zaka nema ba, bani da iko akan

anjiman ka balle har a tsallaka lahirar ka...kawai kabari, ko menene dalilin ka bashi da tushe, ka daina, ka roki Allah ya yafe maka kafin lokaci yayi maka karanci..."

Idan ya fito da sanyin jiki, kalaman Khalid sun sa yaji kamar kashin gwiwar shi ya sulale zuwa wani waje da bai sani ba

"Zanje sallah..."

Khalid din ya furta yana sake juyawa yabar Salim a tsaye. Ya so ya shiga bangaren su ya sake daura alwala, amman yana gudun kar Salim din ya sake bin shi, shisa ya fice daga gidan. A masallaci yayi alwalar, ana idarwa ya gama lazumin bayan sallah ya daga hannuwan shi sama sai kanshi yayi wani irin wayam, ga tarin bukatu a zuciyar shi amman kwakwalwar shi taki bashi hadin kai. Ya dauki lokaci da hannayen shi a sama, zuciyar shi a bude cike da yakini da kuma sallamawa har sai da yaji wani sanyi da tsoron Allah ya ratsa sassan jikin shi tukunna ya mike.

Da ya koma gida kai tsaye dakin su ya wuce, ya samu Nawfal zaune kan kujerar teburin daya dora hannayen shi yana latsa waya da kofin da Khalid ya san shayi ne a ciki. In zai farkawa biyar zai iya ganin Nawfal din a zaune kamar ba dare ba

"Wai kai ba zakayi bacci bane ka huta ma ran ka?"

Ya tambaye shi kwanaki hudu bayan ya zo

"Bana ji ne Hamma, bambanci lokacin nan yana ta bani wahala... Gara in dan rage wani abin da safe na rama In shaa Allah"

Amman hakan baya hana shi yi mishi magana idan ya farka ya ga dare ya raba. Ko ba zai bacci ba dai ya kwanta kwakwalwar shi ta dan samu hutu. Zai so ya watsa ruwa amman kasala yake ji, shisa ya rage kayan jikin shi yana samun T-shirt marar nauyi ya dora akan singlet din shi, sai gajeran wando yabi lafiyar gadon da ya sha gyara sai kamshi ke tashi. Shi kanshi dakin yafi mishi dadi idan Nawfal yana nan, matar shi dai ta huta, Khalid din ya sani. Tsantsainin Nawfal ba zai barshi ya jira sai tayi gyaran gida ba, tana ma iyayi ya sake maimaitawa, dan duk yanda zakayi shara sai kaga ya kara yin wata.

Addu'ar bacci yayi, yana runtsa idanuwan shi, a hankali yake motsa labban shi yana fara karanta ayoyin da suke cikin Suratul-Mulk dan neman saukin kwanciyar kabari, baya taba mantawa tunda ya mallaki hankalin shi ya kuma ci karo da muhimmancin hakan, jarabawar duniya ma neman hanyoyin samun saukin ta yake, balle kuma samun lahira da komai ya zo mana a bayyane. Daya dire cikon ayar karshe harya juya baya sai kuma ya sake juyowa yana bude idanuwan shi akan Nawfal da yake zaune yana danna wayar shi har lokacin

"Bajjo..."

Ya kira da sanyin murya, yana kasa tsayawa ma Nawfal din ya amsa shi dan harya dan juyo da kai

"Dole ne sai yara sun biya zunuban iyayen su? Kana ganin Allah zai iya duba zuciyar yaran yaki jarabtar su?"

Girar Nawfal ta hade waje daya cike da mamaki da kuma son fahimtar in da tambayar Khalid din ta dosa

"Kamar zina da akace maiko take da shi, kana tunanin yara zasu iya kubuce ma wannan maikon kuwa?"

Wannan karin akwai bayanannen tsoro a muryar Khalid da yasa Nawfal mika mishi hankalin shi duka, a iya sanin shi Khalid bashi da wani hali marar kyau, ko a mugun mafarki kuwa ba zai hada shi da aikata laifi mai munin zina ba. Shisa yake neman dalilin da tunanin Khalid din zai dibe shi zuwa inda yake yanzun har ma wannan tambayoyin su hade mishi

"Banajin na fahimci tambayar ka Hamma..."

Nawfal ya fadi da dukkanin gaskiyar shi, numfashi mai nauyi Khalid ya sauke, idanuwan shi cike da wani firgici da Nawfal ya rasa dalilin shi hadi da furta

"Hmmm..."

Sosai Nawfal ya juya dan saida ya motsa kujerar da yake da kai

"Banda amsar tambayar ka, abu daya na sani, kaima kuma ka sani, babu wani abu da yafi karfin Allah, wanda Ya so a cikin kowanne hali zai iya kubutar da shi"

Kai Khalid ya jinjina ma Nawfal yana juyawa da alamar da take nuna ya gama maganar. Mikewa Nawfal din yayi ya karasa wajen kwan fitilar dakin ya kashe ma Khalid din, ba zai daice ya kashe ba, amman yasan hasken zai iya takura mishi. Ya bada wajen mintina sha biyar a tsakani, baiji Khalid din ya motsa ba, cikin sanda ya karasa ya leqa fuskar Khalid, idanuwan shi a rufe suke, da alama bacci ya dauke shi. Abin rufa Nawfal yaja ya rufe shi yana tsaye akan shi, duk wata addu'a ta tsari da neman sauki sai da yayi yana tofa mishi, baisan me ya same shi ba, amman baya son tsoron da ya gani a cikin idanuwan shi

"Allah zai kare mun kai Hamma, daga dukkan abin ki"

Ya furta a kasan numfashin shi yana komawa ya zauna, Khalid na jin shi, yana ji yaja mayafi ya rufa mishi, yana jin addu'ar daya tofa mishi, haka kuma kalaman shi da suka rufe Khalid din ruf, fiye da mayafin da Nawfal ya rufa mishi, kirjin shi yanayin nauyi da sirrin da yake tunanin shi kadai ya san da shi.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com
Whatsapp: 08074545149

*RAI DA KADDARA 1*

19

Mutane zasu tsammaci ganin kunshi a hannuwanta ko da yaushe kasancewar ta wadda ta iya. Amman tana daya daga cikin mutanen da lalle bai dame su ba sam. Asalima sai ta dade ko a farcenta bata saka ba, baifi kagani a jikin babban yatsan ta da kuma mabiyin shi, shima baka raba kowacce mai kunshi da shi, sai dai wanda suke saka safar hannu. Tana da su da yawa, irin na asibiti ma, kwali daya Salim ya bata, rashin sabo yasa duk sai taji ta takura, kwarkwaron kunshin ma yana zamewa daga hannunta idan ta saka. Tun yana mitar baya son ganin tana bata hannun ta harya gaji.

Yau din ma sauran wanda ya rage a kwarkwaron da tayiwa wata yar islamiyyar su ne kawai ta zauna tana zanawa a jikin hannun ta, ba wani mai yawa bane ba, amman ko ita da tayi sai taga yayi mata kyau bayan ta gama tun ma bai bushe ba, hannun harya zama na mace, tana tunanin yanda in ta wanke lallen har wasu zobuna masu yawa da Adee ta bata zata dauko ta bude kwalin ta gwada ko da kwara biyune a yatsun taga yanda zasuyi. Adee akwai son kwalliya, kuma kyau takeyi ma Madinar, zobe zaka gani a kasa da saman yatsun ta, in gidanta kaje yanzun da tayi aure ma har a yatsunta biyu na kafar dama zaka sameta da su ta saka.

Daki ta koma ta dauki remote sannan ta samu kujera ta zauna duk da la'asar ake kira tunda Allah ya hutar da ita, shisa ma ta zana kunshin ta hankali a kwance. Tashar India ta kai ana tsakiyar yin film din Kabhi Khushi Kabhie Gham, labarin film din take ji ana yawan yi, tana kuma sakawa a ranta da zata nema ta kalla, sai dai ba littafi bane ba, film ne. Kallo na karshen abubuwan da ta damu da su, idan tana zaune kamar yanzun ma tana iya taita wasa da remote din tana rasa inda zata tsaya ta kalla, karshe tashar labarai ko documentary ne abinda zaiyi nasarar rike hankalin ta. Da yake ana rubuta fassarar da turanci sai ta bama tv din dukkan nutsuwar ta.

Tana iya juyo sautin bugun zuciyarta da ya zarta har cikin kunnuwan ta da wani yanayi da ba zai misaltu ba, bakinta na gaurayewa da dandanon gishirin da bata san inda ta samo shi ba, ko dandanon hawayen da take jine cike taf da idanuwan ta da take kokarin hanawa su zubo suka koma suka gangara cikin bakinta, shakuwar da take tsakanin jarumin film din da mahaifiyar shi

na jijjiga duniyar da take zaune tana sa hanjinta yamutsawa kamar suna son sake mazauni saboda hargitsin da take ji har su ya tarar a cikin nata. Idan tace Yelwa bata fado mata lokaci zuwa lokaci tun kafin ta karanta wasikar nan zai zamana karya, duk lokacin da idanuwanta zasu sauka akan wani shafin littafi da yake magana kan mahaifiya sai tunanin tata ya kutsa mata.

Haka idan taji wasu suna labarin ta su, ba zatace ta rasa nagartacciyar soyayya da kulawa a wajen Daada ba, amman akwai ramin da take ji a zuciyar ta kamar wajen an halicce shi domin Yelwa ne, kasancewar ta a rayuwar ta ko akasin hakan baya nufin wani zai taba iya zama a gurin. Sai take jin da za'a bata dama guda daya zata koma ta goge ranar da taga wasikar nan, yanda duk ta so ta koma dai-dai, ta koma kamar kafin ta ga wasikar nan sai ta kasa. Abu kadan daya danganci mahaifiya take jin yanda yake samun tasirin raunana mata zuciya.

Ko jiya taga kallon da Daada take yiwa Julde, batasan ko raunin zuciyarta bane ya sa ta ganin zuciyar Daada a cikin idanuwanta duk idan tana kallon Julde, kaman in dai yana karkashin kulawarta zata kareshi daga dukkan wani abu da yake ikon ta, kamar rayuwar ta na da muhimmanci ne tare da dan nata. Da bata gani, amman yanzun tana ganin wannan kaunar, murmushin Daada ma akwai banbanci a cikin shi idan Julden yana kusa. Tsakanin mahaifiya da yaranta wata sirrantacciyar kauna ce da Allah daya halitta musu ne kawai Ya san girman ta.

Sai take tunanin meye bambancin sauran iyaye da tata mahaifiyar? Me yasa tabar ta? Ko dan rashin tabbacin da yake cikin halarcin haihuwar ta? Idan ta duba wannan kawai ya isa ya zama babban dalili a wajen Yelwa, takan ji kamar tana neman wani uzuri ne da zai saukaka mata abinda takeji. Salim yace ta jira Daada idan ta shirya zata fada mata komai a lokacin da take tunanin ya dace, tana kuma kokarin ganin tayi hakan, sai dai da duk wata rana da zata wuce da yanda tarin tambayoyin ta suke kara ninkuwa. Har mamaki takeyi yanda Daada ta kasa karantar tambayoyin a cikin idanuwanta.

Wanne lokaci ne ya dace? Yaushe ne Daada zata fada mata komai? Ko ma tana da niyyar fada mata din? Duka amsoshin tambayoyin nata na wajen Daada. Zuciyarta da nauyi kamar an dora mata dutse ta kai hannu ta dauki remote din tana canza tashar. Mikewa ma tayi tana komawa daki, bayi ta wuce ta wanke kunshin da yanzun ya fita daga kanta saboda zuciyar ta da take ji cunkushe. Sai kewar Salim ta danneta har tana sakata karasawa kan gadon dakin nata ta dauki wayarta ta duba taga bai kirata ba, bai kuma tura mata ko da text bane ba. Sun yi waya da safe, amman gaisawa kawai sukayi, tun shekaranjiya rabon da ta saka shi a idanuwanta.

Jikin ta yana bata akwai abinda yake damun shi, amman shi din ba mai yawan magana bane ba, bai taba bude baki yace mata ga damuwar shi ba, sai dai ta karanci yanayin shu taita jan shi da hirarrakin da take tunanin zasu saka shi murmushi ko kadan ne, ta kuma dinga tuna mishi yaci wani abu, dan in yana cikin yanayi irin wannan sai kaga idanuwan shi duk sunyi zuru-zuru ko idan aiki ya sha mishi kai, in tace ya rame baya cin abinci yanda ya kamata sai yace mata

"Mantawa nake yi Mug, bakya tuna mun, mantawa nakeyi idan abubuwa sun mun yawa"

Yanzun idan ta ganshi haka sai taita jin kamar harda lefinta, kamar in shi ya manta bai kamata ita ta manta ba. Ko ba komai Salim ne, komai nata damuwar shine, shirme da hankali zai bata nutsuwar shi kamar duk duniya babu wani abu mai muhimmanci kamar sauraren ta da abinda yake damunta. Ya kamata shima tashi damuwar ta zama tata, ta kamanta mishi kalar karamcin da yake nuna mata. Tun dazun ta manta basu yi magana ba, bata ma tuna da shi ba sai yanzun da damuwar da take neman ya taimaka ya saukaka mata ta taso.

Tsintar kanta tayi da jin kunya har tana kasa kiran shi, ta dai dauki wayar ta sake komawa falon ko da shi zai kirata. Daada ta samu a zaune ta fito itama, yanzun tafi zama cikin dakinta fiye da yanda take zama a falon. Canjine Madina take gani bayyane a tare da Daadar da ya girmi tsufa kamar yanda take yawan fada, kullum gani Madina takeyi tana kara ramewa kamar bata cin abinci, da ba gida daya suke ba kuma ba ita take kula da cin safe, rana harma na daren Daadar ba zatace ba'a kula da ita yanda ya kamata.

"Assalamu alaikum"

Muryar Nawfal ta daki kunnuwan Madina tana sakata saurin daga idanuwanta da zuciyarta da tayi tsalle zuwa cikin su tana kallon Nawfal da ya sakko kafar shi cikin dakin fuskar shi dauke da murmushi, manyan kayane a jikin shi, yadi kalar sararin samaniya sai hula mai kalar amman mai duhu, kayan sun karbi jikin shi, rigar na nuna fadin kafadun shi da cikar halittar shi duk da bata matse shi ba. Sai dai akwai banbanci a yanayin yanda muryar Nawfal ta sauka a kunnuwan Madina da kuma na Daada. Muryar Bukar taji, muryar dan ta da rayuwa ta zabi ta rabata da shi a karo daban-daban.

Da ta daga ido ma ta sauke akan Nawfal fuskar Bukar ta gani, murmushin shi mai sanyi kamar halayen shi take gani, duk da ko kusa da sanyin halin Bukar din Nawfal bai kai ba, ita kam yau Bukar take gani kamar yanda yanzun da karfin alaka ta jini tasa take ganin Yelwa a tattare da Madina duk da kowa yasan Yelwa zaice bata kama da Madina, amman jini yafi karfin wasa. Da duk wayewar gari da yanda nauyin kirjinta yake karuwa a tsayin shekarun nan, yanzun ya kai inda take jin anya bashi zaiyi ajalin ta ba kuwa? Idan ta kwanta bata tunanin komai sai yanda zata sauka daga gado da safe, yanda za tayi rayuwa a yinin ranar batare da ta kara ma Madina damuwar da take gani cikin idanuwan ta ba.

A satikan nan tana bude bakin ta yafi a kirga sai ta kasa furta komai, me zata ce? Me zata fadama Madina? Ta ina ma zata fara? Yarinyar bata taba tambayar ta komai ba, kamar sun zauna sun hada baki da Nawfal suka zabi shirun da ya saukaka mata komai saboda bata da kwarin gwiwar fuskantar su da labarin da ba zai amfane su da komai ba, bata son ko na minti daya su raba nauyin da take ji tare, duk da tasan nauyin ba nata bane ita kadai, wata rana dole ta raba shi tare da su, yanzun tana jin kusancin ranar fiye da kowanne lokaci. Girma sukeyi su duka, shekaru na riskar su, rashin tabbas din yau da kullum na kara lullube Daadar.

Tana jin ina ma ace ta san sauran kwanakin da suka rage mata, da tafi tsara yanda komai zai kasance

"Daada Am"

Muryar Nawfal ta kutsa cikin tunanin ta

"Soyayyar tawa ce ta motsa haka kike ta kallo na harma bakyajin me nake cewa?"

Murmushi tayi tana jin wani abu ya rabe a cikin kirjinta

"Ko bata bakina ma ba zanyi ba"

Dariya yayi yana karasawa ya tsugunna a gabanta

"Bana son ramar nan dake cikin idanuwan ki Daada... Duka kwana nawa ne ban ganki ba yau amman kin kara ramewa"

Kai Daada ta girgiza tana sauke idanuwan ta daga cikin na shi saboda bata son yanda yake kallon ta kamar yana neman tono dukkan sirrikan da take boyewa

"Wai ba zaku kyaleni ba ne? Idan ma bana ramewa yanzun surutun da kuke mun zai sa in fara"

Ta karasa maganar tana kokarin mikewa, Nawfal na tayata cikin hanzari, yana tuna mata lokuttan da ta taimaka mishi ya mike haka, ta ma daga shi gabaki daya tana mikarwa. Sai da ya tabbatar ta tsaya da kafafuwan ta tukunna ya saketa a hankali yana nazarin ta bayan ta juya, yanda take cira kafafuwan ta dakyar yasa zuciyar shi yin nauyi. Ko lafiyar ta kalau akwai abinda ta saka a ranta, shisa take boye mishi haka, daya shigo gidan suka gaisa take tashi tabar falon, idan dakin ta ya bita sai ta kwanta kamar bacci ya dauketa, wata rana ya dauki filo ya kwanta anan kasa, ko ya dora kan shi akan gadon har saiya gaji da zama.

Yanzun da yake kallon ta babu komai cikin kanshi sai rokon da yake ma Allah na ya ara mishi lokaci mai tsayi tare da Daada saboda itace cikon komai na rayuwar shi, ko Murjanatu bata gani ba sai dai a waya, akwai tarin abubuwan da yake bukatar aron lokaci ya gudanar da su tare da Daada a cikin rayuwar shi. Itama tana jin idanuwan Nawfal din, tasan kallon ta yakeyi, kanta take ji yayi nauyi fiye da misali, kamar babu iska a cikin shi duk da bata san ko akwai yiwuwar cewa iska zata kasance cikin kai ba, kawai hakan zata iya amfani da shi wajen misalta yanayin da take ji.

Hasken daya gilma cikin idanuwan ta na sakata runtsa su ta bude, sai taga duhu, ba duhu irin na gabatowar magriba ba, duhu fiye da na tsakar dare saboda bata iya ganin kyallin komai, sake runtsa idanuwan nata tayi wannan karin duhun na karasawa har cikin kanta

"Daada..."

Taji an kirata kamar daga wata duniya saboda nisan da kwakwalwar ta tayi da kanta duk kuwa da suna hade waje daya, hakan na sa wani abu cikewa a kirjinta kafin komai ya tsaya mata cak.

*

Kamar shirin film haka komai yake dawo ma Madina da Nawfal, da murmushi a fuskokin su, komai na tafiya lafiya kafin ya birkice a kasa da minti daya. Kowa ka tambaya zaice shi ya fara ganin alamar Daada zata fadi, amman babu lokacin wannan musun tunda babu wanda ya iya karasawa ya tare ta a cikin su sai bayan da ta kai kasa tana faduwa tare da wani bamgare na zuciyoyin su. Sai sakanni suka dinga wuce ma Nawfal da nisan awanni, komai baya sauri har shi kan shi, haka yaji daga daukar Daada daga cikin gidan zuwa motar shi haka shigowar su asibiti, haka dorata akan gadon da ya kama aka gungura har zuwa dakin da wani likita ya kai hannu yana turo shi baya kafin su maido kofar su rufe.

Tsaye yake amman ya rasa inda zai sa kan shi yaji sanyi, numfashi ma kokawa yake da shi a wannan lokacin

"Ka zauna Hamma..."

Madina ta fadi cikin sanyin murya tana saka shi juyawa ya kalleta, nutsuwar ta na bashi mamaki, akwai damuwa shimfide saman fuskarta amman a nutse take

"Tashin hankali baya taimakon marar lafiya, nutsuwa yake bukata fiye da komai. Nutsuwar ki ita ce taimakon farko, ki rufe idanuwan ki kiyi numfashi mai nauyi ki fitar har sai kin tabbata kin samu nutsuwar da kike bukata..."

Shine abinda Salim ya fada mata, ya maimaita mata har saida ya tabbatar ta fahimta bayan ta haddace kowacce kalma. Shisa yanzun ita ta fada ma likitan sunan Daada, shekarun ta da kuma lambar katinta da ta haddace ko da zasu taho asibiti a hargitse bata dauko ba za'a iya amfani da lambobin a binciko file din ta kamar yanda tasan anyi yanzun din, ko ana kanyi

"Ina wayar ka?"

Ta bukata ganin gardamar da take cike da idanuwan Nawfal din akan tayin zaman da tayi mishi, ta masa uzuri, wannan ne rashin lafiyar farko da Daada tayi yana nan. Aljihun shi Nawfal ya laluba yana dauko karamar wayar da yaji a jikin shi ya mika mata. Lambar Salim da ta haddace ta saka tana kiran shi, sai da ta kira sau uku ana hudun ya daga da fadin

"Yanzun na shigo na dauki wayar Bajjo, menene?"

Numfashi taja tana fitarwa

"Hamma ni ce"

Da mamaki a muryar Salim yace

"Madina?"

Cike da alamar tambaya kafin ya dora da

"Lafiya? Me ya faru? Ina Bajjon?"

Sai da ta kalli Nawfal sannan ta amsa

"Gashi nan, yana lafiya. Muna asibitin ku... Daada ce ta fadi"

Ta karasa tana jin yanda bugun zuciyar ta yake karuwa cike da tsoro, girman abin da ya faru a gabanta yana danne ta

"Ki tashi ki duba saiki fadamun inda kuke?"

Mikewar tayi kuwa, ya nuna mata yanda zata karanta sunan kowanne ward a asibitin ta kuma gane in da take, dubawar tayi tana fada mishi

"Gani nan zuwa yanzun... Daddy ya sani?"

Kai Madina ta girgiza

"Kai na fara kira..."

Ta fadi cikin sanyin murya

"Karki kira kowa tukunna, gani nan"

Wayar ta sauke daga kunnenta tana kashe kiran. Riga da wando ne a jikinta, ta dora ta sanyi doguwa akan tshirt din da takai mata har gwiwar ta, akwai maballai a jikin rigar daga farko har karshe, an yi kwalliya da wasu har a gefe, sai hula da ta dan tura baya batare da gashin ta ya bayyana ba, haka take zaune sanda Nawfal ya zo, haka kuma ta fito batare da ta saka komai ba sai takalmin da daman akwai shi a kafarta na yawo cikin daki. Tsaye take har Salim ya karaso yana kai hannu ya tura mata gilashin dake fuskarta ganin ya dan sakko ita kuma bata mayar da shi ba.

Tayi mishi kyau kamar ya dauketa ya boye, zuciyar shi ta yamutsa lokacin da ya yawata da idanuwan shi akan fuskarta

"Wanne daki suka shiga da ita?"

Da hannu ta nuna mishi saboda idanuwanta da taji sun cika da hawaye, tana yin magana zubowa zasuyi, kai ya jinjina yana kama hannun nata ya jata ya karasa da ita inda ta tashi a waiting area din yana zaunar da ita. Nawfal ya kalla da yake tsaye

"Bajjo..."

Ya kira a hankali, tun yarinta zaka iya cewa Nawfal na da juriya, tunda kafin kaji kukan shi zai wahala komin dukan da Saratu zatayi mishi kuwa, sai ta mare shi ya fadi ya tashi yayi tsaye kamar yana son ganin iya abinda zata iya yi. Kowa zai ce yana da karfin hali, abinda zai taba shi mai girma ne. Shi ne zai karyata, Nawfal ne yaro mafi rauni daya taba cin karo da shi, ko idanuwan shi ka kalla zaka ga wannan raunin, yana da babbar zuciyar da yake yawo da ita rike cikin hannuwan shi yana jiran mai rabo ya gifta dan ya karbe shi cike da karamci.

Akwai vulnerability a tare da Nawfal din da baisan yanda zai misalta ba. Kullum ya gan shi sai yaga kamar akwai abinda yake bukata da su duka suka kasa ba shi, ya dauka zai ga abin ya kau bayan yayi aure, yana nan, matar shi ma bata bashi wannan abin da yake nema ba, har yanzun bai cika ba, akwai rami mai girma a tare da shi. Wannan raunin kuwa shine a bayyane yanzun, karasawa Salim yayi yana kamo hannun Nawfal din da yake kokarin kwacewa, sai dai ba girman su bane kadai bambancin, harma da karfin su, jan shi yayi yana amfani da karfi wajen zaunar da shi gefen Madina.

"Har yanzun ba su fito ba Hamma? Bata numfashi sanda muka zo...bata numfashi... Daada bata numfashi Hamma..."

Kai Salim ya daga mishi kamar a gaban shi akayi, saboda fahimta Nawfal yake bukata, so yake wani ya fahimci abinda yake ji ko zai samu sauki. Kirjin shi kamar zai tsage gida biyu, da gaske labarin tashin hankali yake ji, bai taba fahimtar ya yake ba sai yau, wancen karin abinda yaji wasan yara ne, ya dauka idan yazo yaga Daada, ana komai a gaban idanuwan shi sai yafi samun sauki. Ashe ba haka abin yake ba, ashe nisan da yayi sauki ne, bai ganta ba, bai ga kamar ya rasa ta ba.

Tare da wani bangare a zuciyar shi suka fadi, ko Daada ta tashi bayajin wannan bangaren zai mike, faduwar da yayi ba wadda zai mike bace ba.

"Breath..."

Salim ya furta cikin umarni

"Yanzun Bajjo, in... Out.... In... Out"

Numfashin kuwa yake ja, yana fitarwa, muryar Salim na mishi jagora, har sai da ya dan fara samun nutsuwa tukunna

"Ka zauna nan, ku duka ku zauna nan"

Ya fadi yana kallon Madina da ta kai hannu tana share hawayen da ya zubo mata. Bayajin ta kamar Nawfal, tana da karfin hali duk da kankantar ta. Idan ta kama ya san zata ture damuwar ta a gefe ta kula da Nawfal din. Yana shirin karasawa dakin likitan na fitowa. Daga inda su Nawfal suke basa iya juyo abinda su Salim din suke fadi, ta gaban su dai suka wuce, sun fi mintina sha biyar kuma kafin Salim ya dawo shi kadai.

"Me yace? Ta tashi? Me yace ya same ta?"

Nawfal ya jera ma Salim tambayoyin da kafin ya zabi wadda zai fara amsawa ya kara da

"Zamu iya shiga mu ganta? In shiga in gan ta Hamma?"

Kai Salim ya girgiza mishi a hankali

"Sai ta kara hutawa...za'a kara mata wasu tests din tukunna..."

So yake ya basu tabbacin da yaga suna nema akan fuskar shi kamar duk wani wanda zai kawo marar lafiya, amman a yanzun ya ture batun cewa su din na shi ne, likita ne shi a yanzun, su kuma yan uwan mai jinya.

"Zamu san komai idan aka karasa sauran tests din...banda abinda zan fada muku yanzun da ya wuce tana samun dukkan taimakon da take bukata"

Hannuwa Nawfal ya saka yana dafe kan shi da su, likita ne a gaban shi ba Salim ba, ya gani, ya kuma ji a muryar shi, numfashi yake ja yana fitarwa a hankali sannan ya dago ya kalli Salim din

"Hamma..."

Ya kira amman Salim yaki kallon cikin idanuwan shi

"Hamma ka cire rigar nan kayi mun magana, dan Allah kayi mun magana"

Nawfal ya karasa cikin roko, muryar shi na fitowa cike da rauni.

"Ka fadamun... Kaji"

Yayi maganar cikin karfin hali yana son Salim ya fahimci zai iya daukar koma menene akace yana damun Daadar, so yake yaga ba yaro bane shi karami da yake bukatar kariya. Dan murmushi Salim din yayi mishi

"Sai an gama running tests Bajjo..."

Gardama zai karayi Madina ta katse shi

"Zaka zauna damu ko zaka kara dawowa?"

Numfashi Salim ya sauke yana godema Madina, idanuwan shi ya sauke cikin nata yana fatan taga godiyar shi

"Zan sake dawowa...da sun gama abinda sukeyi zasu sake mata daki, sai ku zauna da ita"

Madina ce kawai ta iya daga mishi kai

"Idan kuna bukatar wani abin sai ki kirani"

Kan dai ta sake daga mishi, ya kalli Nawfal daya kauda na shi kan gefe da alamar fushi yakeyi saboda yaki gaya mishi me ya samu Daada, numfashi kawai ya sauke yana wucewa yabar su a wajen. Office din shi ya koma ya zauna yana sauke wani dogon numfashi hadi da kai hannu ya murza kan shi daya fara alamar ciwo, ya gama round din shi sai kuma nan da awa daya, idan ba an shigo da marar lafiyar da yake bukatar agajin gaggawa ba. Ya kira Julde bayan sun gama magana da likitan yana kuma jira ne ya karaso asibitin.

Da gaske ne da yace ma su Nawfal sai an gama gwaje-gwaje tukunna, amman yana da abinda zai fada musu, zuciyar da zaiyi amfani da ita ya fada musun ne bashi da ita. Da Madina ce ita kadai zai san yanda zai gaya mata yayi mata bayanin da zata fahimta, Madina ce zai ma iya neman wasu takardu akan matsalar ya bata ta karanta, zai sha tarin tambayoyin da yasan ba zai iya amsa mata ba tunda shi ba likitan zuciya bane ba, amman ya san likitan zuciyar, ya kuma san zaiyi farin cikin amsa ma Madina dukkan tambayoyin ta.

Nawfal yake ji, yanda yake a hargitsen nan yana ce mishi akwai yiwuwar sai an ma Daada aiki, akwai yiwuwar ba toshewar jini bane da rashin kai kawon shi yanda ya kamata a tsakanin jijiyoyin ta da kuma zuciyar ta kamar wancen karin, matsala ce da ta girmi a dora ta akan magunguna, zai iya yiwuwa sashe ne kacokan a jikin zuciyar tata ya gaza yake kuma bukatar a sake shi cikin gaggawa kafin ya haifar da wata sabuwar matsalar, duka hasashe ne yanzun, babu abinda aka tabbatar sai likitan da aka kira ya zo. Bashi da karfin halin da zai sake daga ma Nawfal din hankali akan hasashe, sai an tabbatar da komai tukunna.

Ya godema Allah da bai fada ma su Nawfal komai ba ganin yanda Julde ya hargitse bayan ya zo asibitin ya karasa Office din Salim din ya kuma yi mishi bayanin hasashen da likitan yayi

"Dan Allah Daddy, kar su Bajjo su ganka haka su dauka wani babban abin ne, bafa wata matsala bace da ba za'a iya shawo kanta ba, idan ma surgery dinne bashi da wata matsala..."

Salim yake fadi cikin tausasawa

"Ko kasar za'a bari da ita, Alhamdulillah akwai halin yin hakan... Dan Allah ka kwantar da hankalin ka"

Kai kawai Julde yake daga ma Salim din ba dan yasan ta inda zai fara kwantar da hankalin shi ba. Har ruwa ya bashi mai sanyi, da kan shi ya bude mishi robar, kurba daya yayi yana jin ruwan ya wuce dakyar, kan shi ya dora a jikin teburin office din Salim din yana maida numfashi, yaji dadin shirun da Salim yayi yana bashi dama ya nemi nutsuwa da kan shi. Bugun da zuciyar shi takeyi shi dinma in aka auna za'a iya bukatar yi mishi aiki a cikinta.

"Ina jin kamar ba zan sake saka su a idanuwa na ba Julde"

Muryar Daada a waccen jinyar da tayi ya dawo mishi, shirun da ya biyo bayan maganar tata na biyo shi tun daga wancen lokacin zuwa yanzun da yake zaune a ofishin Salim. Shiru ya zaba, Daada bata matsa mishi ba, bata ambaci sunaye ba, amman yasan me take nufi, bata bukatar ta ambaci sunan kowa. Ya zabi shiru ne ya kuma zabi danna tambayoyin ta can kasa tare da duk wani abu daya danganci Yelwa da Bukar din. Bata sake daga mishi zancen ba, shima bai sake bari ya dawo mishi ba sai yanzun. Saboda ya zabi ya so kan shi, ya dora bukatar shi akan tata. Son kan da sai yanzun yake ganin shi

Su duka Yelwa ta tsalla ke
Ba shi ka dai ta bari ba
Har da Daada.

©
📖✏️
FIKRA WRITER'S ASSOCIATION

Facebook: Lubna Sufyan
IG: SufyanLubna
Email: Calmlubna@gmail.com
Whatsapp: 08074545149

*RAI DA KADDARA 1*

20

A karo na farko a rayuwar shi da ya rike jaka a hannun shi batare da yasan abinda zai zuba a ciki ba

"Kana da passport Bajjo, Daada ma nata baiyi expire ba, da kai ya kamata ku tafi, zan biyo ku daga baya dan kar a bata lokaci"

Abinda Julde yace mishi kenan, yana kallon gamsuwar da su Khalid sukayi da maganar Julden a cikin idanuwan su tun kafin ma su furta. Shisa yayi shiru, yanda duk ya so ya girgiza wani ya fada mishi cewa ba yajin zai iya tafiya shi kadai, bayajin yana da karfin halin da zai kula da Daada batare da zuciyar shi ta rarrabu kashi-kashi a cikin kirjin shi ba, sai ya kasa. Kai kawai ya daga musu cikin yarda shima. Hadiye tsoron da fargaba yayi har sai da ya koma gida a ranar, ya saka mukulli yana kulle dakin bayan ya shiga sannan ya budema Murjanatu zuciyar shi yana jin rashin ta fiye da kowanne lokaci

"Bana jin zan iya Jaan, Daada ce, yau dana ganta a kwance babu abinda naji ina so inyi sai in zauna a gefen ta inyi kuka har sai ta bude idanuwanta tace mun komai zaiyi dai-dai... Ban taba kula da ita ba, ita ta saba kulawa da ni, taya zan fara yanzun?"

Ya karasa yana jan wani irin numfashi hadi da fitar da shi cike da nauyin da yake ji a kirjin shi, saboda yanda yayi maganar batare daya ba kanshi damar numfasawa ba

"Waya yace kai kadai zaka kula da ita? Ba India kace ba? Zaka sameni a filin jirgi ina jiran ku Gidado...idan na kula da kai zaka iya kula da ita? Zan so ince maka zan kula da ku duka biyun, amman Daada ce, zaka so kayi komai daya dangance ta da kan ka... Na san hakan, kaima in ka nutsu ka duba zuciyar ka zaka ga hakane..."

Numfashin dai ya sake ja yana fitarwa

"Babu abinda ba zaka iya ba in dai akan Daada ne, in baka yarda da kan ka ba, ka yarda dani, kasan ba zan maka karya ba, duk da ina son ka"

Baisan murmushi ya kwace mishi da kalamanta na karshe ba sai da yaji alamar shi har a zuciyar shi da nauyinta bai ragu ba, amman numfashin da yaja ya kai mishi har ciki

"Kinsan bangane komai da kikace sosai ba...komai ya kare ne da yanda kika ce kina so na"

Dariyar da tayi sai da ta kara fadada murmushin shi

"Ina son ka... Ina son ka Gidado"

Kai ya jinjina, ya sani, saboda yanda bata gajiya da nuna mishi duk rana haka bata gajiya da fada mishi tana son shi. Wasu ranakun in ta fada sai yaita kallon ta, musamman labbanta da yanda kalaman suke fitowa kamar basu da wani nauyi a wajen ta. Da shi bahaushe ne, daya boye a bayan yaren yace shisa fada mata yana son ta a duk rana yake mishi wahala. To shi bafullatani ne, babu kunya a tsakanin su, sun wuce wannan matakin tuntuni, bashi da abinda zaiyi amfani da shi a matsayin kariya.

Amman kalmomin suna masa nauyin furtawa, zai iya kirga lokuttan daya fada mata su, yana dai

kokarin ganin a rana ya zama dalilin da zatayi dariya ko sau dayane, yana kuma kokarin kyautata mata dai-dai iyawar shi, fada mata yana son ta na mishi wahala, amman nuna mata abune mai sauki saboda ta cancanci fiye da hakan a wajen shi, ta bashi abubuwan da zai dauki lokaci idan an bashi dama yana bayanin su.

"Wai har yanzun kana nan tsaye Bajjo?"

Khalid da ya turo kofar yana katse ma Nawfal tunanin shi ya furta

"Na rasa abinda zan dauka, Murjanatu ta shiryamun jakata da zan taho"

Gira daya Khalid ya daga

"Nasan kana da aure Bajjo, ban manta kana da mata ba"

Dariya Nawfal yayi

"Yi hakuri ba haka nake nufi ba"

Labban shi Khalid ya matse waje daya yana jinjina kai, cikin yanayin dake fassara "Ka dai cigaba Allah yana kallon ka". Dariya ya sake na Nawfal

"Da gaske na rasa abinda zan dauka"

Numfashi Khalid ya sauke

"Me yasa kake fadamun? Ka kira Murjanatu mana sai ta fada maka abinda ta shiryo maka sanda zaka taho ka sake daukar su"

Kai Nawfal ya jinjina cikin yarda da shawarar Khalid din yana nufar inda wayar shi take ya dauko

"Me zakai?"

Cewar Khalid yana bude baki cike da mamaki

"Kiran Murjanatu mana?"

Dafe kirji Khalid yayi yana samun waje kan gadon ya zauna

"Me ka dafe? In zuciyar ka ce ba'a bangaren dama take ba, saika dan matsar da hannun ka tsakiya..."

Wani irin kallo Khalid yake ma Nawfal din daya cigaba da fadin

"Daga bangaren haggu kadan"

Ta baki Khalid ya furzar da numfashi yana sauke hannun shi

"Baka ga kallon da nake maka ba ko? Ba zakayi shiru ba"

Dariya Nawfal yake yi

"Da gaske, wannan ai son kunyata Hamma Salim ne, ace baka san inda zuciyar ka ta ke..."

Robar ruwan da Khalid din ya dauka na sa sauran kalaman Nawfal din makale mishi tare da dariyar da yayi niyyar yi

"I dare you Nawfal Bukar..."

Khalid ya fadi muryar shi babu alamar wasa

"In kira Murjanatun ko..."

Kallon "Magana kake har yanzun" da Khalid ya watsa mishi yasa shi daga hannun shi cikin saranda yana mayar da wayar ya ajiye. A duniya dai yasan in ta bangaren samun yan uwa ne Allah ya gama masa komai, ko da ace dama aka bashi zai wahala ya zabo irin su Khalid. Shisa yake kara godema Allah da kyautar su da Ya yi masa a cikin rayuwar shi. A cikin mintina kadan Khalid kan saka shi yaji yanda zai iya jure duk wani abu da zai faru da shi a cikin kowacce rana. Numfashi da bai san yana rike da shi ba ya sauke. Kananan abubuwa ya fara tattarawa kamar su brush da cajar waya da duk wani abu da yake tunanin zai bukata.

"Ba zance maka Daada zata zauna tare da mu har karshen rayuwar mu ba Bajjo, amman komai zai faru Allah ba zai dora mana abinda ba zamu iya dauka ba, daga karshe komai zaiyi dai-dai... In shaa Allah"

Khalid ya fadi muryar shi na fitowa da wani sanyi da yasa nauyin da Nawfal yake ji a kirjin shi karuwa. Baice komai ba, kayan shi ya cigaba da hadawa, ko ya so ya fadi wani abu bai san me zaice ba

"Hamma yaje ya dauko su"

Khalid ya fada dan ya rage musu nauyin shirun da ya lullube su gabaki daya, kai kawai Nawfal ya jinjina batare da yace komai ba, mikewa Khalid yayi tare da fadin

"Matar ka kake son kira, na bar maka dakin Bajjo"

Murmushi Nawfal yayi, ba dan zai kira Murjanatu bane ya fita, abinda ya zo ya fada mishi ne ya gama fada shisa ya bashi waje yayi tunanin duk da yake bukata

"Nagode Hamma..."

Ya furta a hankali duk da Khalid din ya rigada ya fita daga dakin. Kayan shi ya cigaba da hadawa zuciyar shi da kan shi cunkushe da abubuwa mabanbanta.

*

Da yawa kance lokaci sakarai ne, idan ya wuce baya dawowa. Ta kuma ga hakan a al'amura daban-daban. Ta ga sauri da rashin saurin lokaci musamman idan tana jiran wani abu. Kwanaki bakwai dai basu taba zuwa sun wuce mata haka batare da ta rike wani abu guda daya mai muhimmanci da tayi a cikin su ba. Tayi kuka har sai da ta fara tunanin anya ba duk rana ake halitta ma bawa sababbin hawaye ba? In ba haka bane ba tasan ta inda take samun hawayen fitarwa bayan tarin wanda ta zubda ba.

Ta sha jin labarin kadaici, har ma take tunanin idan ta runtsa idanuwan ta a wasu ranakun takan ji shi, takan ji kewar iyayen da ko fuskar su bata sani ba. Ashe wannan ba kadaici bane ba, yaudara ce da zuciyar ta take yi mata, asalin kadaici na cikin ranar da Khalid ya maida ta gida dan ta dauko kayanta. Yanda ta shiga cikin gidan tana tunanin ta inda zata fara inda ace ta rasa Daada, lokacin ne ta duba tsakar gidan da yayi mata fadi kamar duka duniyar ta ce ta tattaru a waje daya, ta kuma ganta ita kadai a tsaye. Ranar ne ta fara sanin menene kadaici, yanayi ne da yayi matukar firgitata, ranar kuma ta hango maraicin da bata fatan ya kusanto inda take.

Tun jiya aka sallame su, tunda daman sun kara barin Daada ne dan a tabbatar ta samu saukin da zata iya zaman jirgin tunda an riga an gama kammala duk shirye-shiryen da za'ayi da ya danganci tafiyar ta su. Ita dai ce take ta hada kayanta tunda ance gidan Julde zata zauna har su Daadar suje su dawo, ta so ta tambaya me yasa ba za'a tafi da ita ba, me yasa za'a barta, waye zai kula da Daada bayan bata tunanin akwai wanda yasan abinda Daadar take so da wanda bata so fiye da ita.

Amman tunda take bata taba ganin damuwa karara a fuskar Julde ba irin wannan karin. Yau ma da yazo gidan idanuwan shi duk sun kumbura kamar wanda yayi kuka. Maganar shima a shake take fitowa, shisa ta rasa kwarin gwiwar da zata tsare shi da wasu tambayoyi. In da zata iya daukar dakinta kacokan din shi da haka zatayi, saboda komai da yake ciki bukatar shi takeyi. Bata taba kwana wani waje ba bayan asibiti tare da Daada tunda take.

"Kwana nawa zakuyi Hamma?"

Tayi ma Nawfal tambayar da ta kasa yiwa Julde, amman kafadu ya daga mata cike da rashin sani kafin ya amsa da

"Ba zance ga exact kwanakin ba Madina...zan fada miki da na san kwana nawa zamuyi"

Kai kawai ta iya jinjina mishi, tana ture tunanin can kasan zuciyarta saboda bata son hasaso kwanakin da zatayi batare da Daada ba. Ba zata taba daukar duk abinda take da bukata ba, ta sani. Shisa ta rufe jakar kawai tana daukarta ta fito da ita falo ta ajiye. Dakin Daada ta nufa ta sameta a zaune in da tayi sallar la'asar, karasawa tayi ta zauna a gefenta tana matsawa sosai yanda zata iya jingina da jikin Daadar, bata da lafiya, amman tana bukatar hakan ko na yan mintina ne ko zuciyar ta zatayi mata sanyi.

"Allah ya baki lafiya Daada Am... Allah ya kaiku lafiya ya dawo da ku lafiya... Zanyi kewar ki"

Madina ta karasa maganar muryarta na fitowa a karye, hannu takai ta dan daga gilashinta tana sa yatsa ta goge hawayen da take jin ya taru a gefen idanuwan ta. Numfashi Daada ta sauke, akwai ciwo na daban da zuciyarta take fama da shi da yafi karfin ganin duk wani likita a fadin duniya.

"Kina da tambayoyi Madina, na san kina da tambayoyi masu yawa... Nagode da yanda baki taba tsare ni da in fada miki ba"

Sake shigewa jikin ta Madina tayi tana jin zuciya ta na kara karyewa

"Dan Allah kibar maganar nan Daada... Ke dai Allah ya baki lafiya, in akwai abinda ya kamata in sani ai ba saina tambaya ba na san zaki fadamun"

Cewar Madina, tana jin gaskiyar kalaman har ruhin ta. Koma menene bashi da muhimmancin lafiyar Daada a wajen ta. A yanzun ma gabaki daya babu wani abu da take so sama da ganin Daada ta dawo lafiya, an duba ance babu sauran abinda yake damun ta. Murmushi Daada tayi, murmushin da ya fito daga wani tsagi na zuciyar ta da har ya daina bugawa tare da yan uwan shi ba zai daina godema Allah da kyautar su Madina ba, akan su ta kara yarda da yanda Allah yake fitar da mai kyau a cikin mummuna.

Sallamar da suka ji na sa Madina mikewa, a daki ta baro wayar ta, tasan da zai wahala Salim ya shigo gidan. Zai kira ta ne yace mata yana kofar gida, tana fitowa falon kuwa ta ganshi a tsaye, kallon shi tayi tana ganin yanda yafi kofar tsayi. Salim dogo ne, irin dogayen da ko a cikin masu tsayi zaka duba da yawa baka sami kalar shi ba

"Hamma..."

Ta furta yana sauke mata numfashin da yake rike da shi a matsayin amsa kiran sunan shi da tayi, kallon ta yakeyi da gajiya kwance akan fuskar shi, kasan idanuwan shi ya danyi duhun da in baka san shi ba zaka dauka haka suke. Madina ta san rashin wadataccen bacci ne

"Ina ta kiran ki..."

Salim yayi maganar yana daga mata karamar wayar shi da yake rike da ita

"Nabar wayar a daki, amman ga jakunkunan mu nan, na hada komai, bari ince ma Daada ta fito sai mu tafi"

Kai Salim ya dan daga mata yana shiga cikin dakin sosai ya dauki jakunkunan nasu kamar basu da wani nauyi ya fice daga dakin. Ita kuma ta koma tana fada ma Daada ta fito su tafi. Sai da ta shiga dakin ta ta dauko wayarta sannan ta fito, tana kallon yanda Daada take daga kafarta tana saukewa dakyar, amman ba zata yarda ka kamata ba, in dai zata samu ta mike to zatayi tafiya ko yaya ne. Ita ta kulle ko ina tana sauke numfashi bayan ta fita kofar gida taga ta kulle nan ma. Tana juyawa ta ga Salim ya fito daga motar yana zagayowa ya bude ma Daada gidan baya ta shiga.

Ya mayar ya rufe sannan ya zagaya yana komawa mota, sanda ta taka ta shiga, tana rufe kofar taji yace ma Daada

"Ya jikin naki Daada? Kan baya ciwo yau?"

Cikin yaren fulatanci

"Alhamdulillah, gashi ka ganni garas"

Dan murmushi yayi

"Allah ya kara lafiya"

Ya furta da hausa wannan karin, yana jan motar tunda daman yayi kwana kafin ya ajiye ta. Shi Madina take kallo tana son gane abinda yake damun shi a kwanakin nan, rashin maganar shi ya karu, sai suyi zaman awa daya baice mata komai ba, duk hirar da zatayi sai dai in idanuwanta nakan fuskar shine zata kula da yanda yake amsa ta da gira, kai ko nashi idanuwan da zai lumshe ya sake bude mata a kasalance. Salim najin idanuwan Madina da suke yawatawa a jikin shi kamar tana son budo duk wasu sirrikan shi.

Yana jin yanda kallon nata ke sa wani abu amsawa a cikin kirjin shi. Sharewa yayi kamar bai san tanayi ba har suka karasa gida. Kamar wanda yake kan kaya haka ya fice daga motar da sauri. Shi ya bude ma Daada da tace mishi

"Da ba sai na fito ba tunda zamu juya ne... Ko ba yanzun za'a tafi ba?"

A kasalance Salim ya kalle ta

"Ki fito Daada, ko ruwa ki sha, ki dan mike kafafuwan ki kafin kowa ya shirya, ba zakiyi ta zama a mota ba"

Har zuciyar ta zaman motar zata zaba in da wani abu a muryar Salim ya bata damar hakan. Amman tsaye yayi yana jiranta, dole ta sauko da kafafuwanta daga motar. Rabonta da gidan tun bikin Adee, shima ba dadewa tayi ba. Tunda har gida mijin Adeen yaje ya gaishe da ita, ko yanzun yakan biyo lokaci zuwa lokaci, bai taba zuwa mata hannu biyu ba. Zatace yana da kirki, amman ta san kirkin na shine ya hadu da yanda Adee ta nuna mishi darajarta. Sai da yaga ta fito ya rufe murfin motar. Madina ma fitowa tayi ta zagayo suna jerawa da Daada.

"Jakar ki Mug...wacce ce jakar ki?"

Salim ya tambaya ganin ta bi Daada

"Babbar..."

Ta amsa mishi a takaice batare da ta juyo ba tunda ta san zai biyo su. Tare suka shiga har falon gidan suna dan hira da Daadar. Madina ce tay sallamar da Saratu ta fito tana amsawa, fara'ar da take fuskarta na ragewa da ganin Daada.

"Ina wuni..."

Ta furta a hankali tana dorawa da

"Ya karfin jikin? Ku zauna mana Madina"

Zaman Daada tayi sannan ta amsa gaisuwar da Saratu tayi mata, Madina na gaishe da ita

"Ina jakar?"

Dan juyawa Madina tayi dai-dai shigowar Salim da yayi sallama cikin sanyin murya. Saratu ta karasa tana kai hannu zata karbi jakar hannun Salim din

"Ina zan kai?"

Da hannu ta nuna mishi hanyar dakin da nashi ne a cikin gidan kafin ya bar bangaren ya koma in da yake yanzun. Can kuwa ya nufa ya kai jakar ya dawo falon

"Ina Daddy?"

Ya bukata, dan murmushi Saratu tayi

"Yanzun zaka ga ya shigo"

Ta kirashi bai dauka ba, daman bata sa ran zai dauka ba, idan da ta kira fiye da sau daya zai san dole akwai wani abu muhimmi. Ace kai da mijin ka ba zaka kira kaji lafiyar shi ba, ba zaka kira ka tambaye shi wani abu ba balle kasa ran zakuyi hira idan yayi maka nisa. Bakowa bane zai fahimci ciwon abin sai macen da take cikin irin halin da take ciki.

"Madina a zubo muku abinci mana"

Saratu tace tana maida hankalinta kan su, kai Madina ta girgiza

"Ko zaki ci Daada? Baki ci wani abu mai yawa ba fa"

Kai Daadar ta girgiza a hankali

"Ni kam banajin yunwa fa"

Numfashi Saratu ta sauke

"Bari a kawo ruwa to"

Tayi maganar tana nufar hanyar kitchen, bata jima ba ta dawo da ruwa da kofi, Madina ta karba ta zuba ma Daada tana mika mata. Karba tayi ta dan kurba ba dan tana jin kishi ba, ta ajiye kofin a kasa. Sai lokacin Madina ta kula da Salim ya bar dakin, sai Saratu da ta samu kujera can nesa da su ta zauna. Wani irin shiru marar dadi na lullube dakin, su duka ukun an rasa wanda zai ce wani abu. Sai dai motsin Madina da kan gyara zamanta lokaci zuwa lokaci. Ta ji dadi da Saratu ta mike ta kunna kayan kallon da suke cikin dakin tana daukar emote ta koma in da ta tashi ta zauna.

Sai ita da Madina suka maida hankali kan labaran, Daada kuwa kara shigewa tayi cikin kujerar da take zaune, kanta cunkushe yake da tunani kala-kala. Ko shigowar Julde bata ji ba sai muryar Madina da take gaishe da shi

"Daada kun gama shiryawa ko?"

Ya bukata yana murmushin da kallo daya zakai mishi kasan na karfin hali ne, kai Daada ta daga mishi a hankali tana mikewa. Sai take ganin kamar ta dade bata kalle shi ba, kamar duk shekarun nan akwai wani labule a tsakanin idanuwan ta da shi da yake hana mata ganin shi irin yanda take ganin shi yau. Ba Julden da yake da mata da yara ba, ba Julden da ake ma kallon babban mutum a wajen kasuwan ci da cikin unguwa ba. Julde take kallo shi kadai batare da duk wannan abubuwan ba, dan ta take kallo yau tana jin littafin da ta dade da rufewa a cikin kanta yana budewa kafin ya tsaya a wani shafi da yake da muni a rayuwar su gabaki daya.

Duk shekarun nan, watannin da suke a cikin shekarun, ranakun da suka dinga zuwa suna

wucewa bata san dalilin da sai yau ba, sai yau ta zabi ta kalli Julde da idanuwan da tayi mishi alkawarin ta kauda su da kan shi har abada

"Allah ya tsine maka albarka Julde. Allah ya kunyata ka a idanuwan zuri'ar ka yanda ka zame mun abin kunya!"

Idanuwanta ta runtsa, gabaki daya kirjin ta na daukar dumi kamar an hura mata wuta a ciki.

Me yasa sai yau? Shine tambayar da bata da wanda zai amsa mata. Ta kuma kasa daina kallon shi. Ko da ta runtsa idanuwan, tana bude su akan shi suka sauka, sai dai yanzun taga kamar yana cikin wani abune mai kama da kwallon kafa, amman duhun abin bai hanata ganin shi a tsaye a ciki ba, kamar yana tsaye ne a cikin tsinuwar mahaifin shi da take jiran cikar lokaci ta fashe tare da shi. Da Madina bata riketa ba da kafafuwanta sun kasa daukar ta saboda firgicin da ya ratsa ruhinta

"Daada ba dai jikin bane ba?"

Madina ta bukata cike da kulawa da kuma damuwa, kai kawai Daada take girgiza mata, addu'ar duk da tazo mata karantawa takeyi tana neman samun nutsuwa. Haka suka lallaba suna fita waje. Saratu daga bakin kofa tayi musu fatan Allah ya kiyaye hanya, lokaci ya koya mata kama kanta da kinyi musu abinda ta dauka a matsayin shisshigi a cikin rayuwar su. Tun farko Daada bata karbeta ba, tayi biris da cewar ko da bata auri Julde ba jinin da yake yawo a jikin ta yana yawo a jikin shi, ita din dangin shi ce ko da aure bai hada su zumunci ba.

*

"Hamma kana soka mun kashin hannun ka a hakarkari na fa"

Nawfal yai maganar yana sake gyara zaman shi. Motar da Julde ya so su dauka ya manta rabon da ya hau ta, kin tashi tayi, Daada, Madina da Salim baya suka shiga su. Khalid ya bude ta bangaren da Salim yake ya watsa mishi wani kallo da yasa shi mayar da murfin yana rufewa hadi da furta

"Allah ya baka hakuri"

Ta kasan makoshi, zagayawa yayi ya koma gaba in da Nawfal yake zaune

"Ka dauko motar ka mana, matsewa fa zamuyi anan...dan Allah ka dauki mota Hamma"

Amman Khalid yaki sauraren shi

"Zaka matsa ko sai na kwade ka"

Nawfal turo labba yayi yana kallon Julde da ya shiga mazaunin direba ya rufo kofar

"Daddy kace Hamma ya dauki motar..."

Bai rufe baki ba yaji Khalid din ya turmotso rabin jikin shi akan na Nawfal

"Kasheni zakayi ne wai, ka tsaya in matsa maka mana"

Ya karasa yana ture hannun Khalid har yana gabje hanci da murfin motar da yake kokarin jawowa ya rufe

"Wai dan uban ka Bajjo ni sa'anka ne?"

Sake tura shi Nawfal yayi

"Daddy kaji Hamma na zagi ko?"

Dakyar Khalid ya rufe murfin motar, yanda suke tutture juna zaka dauka yarane yan shekara bakwai ko kasa da haka. Murza kan shi da yake ciwo Salim yakeyi tun da suka fara

"Bajjo ku fita daga motar nan"

Ya furta babu alamar wasa a muryar shi, nutsuwa sukayi

"Ba ku jini ba kenan"

Ya sake maimaitawa

"Daddy kace ya barmu dan Allah, ba munyi shiru ba"

Khalid ya fadi, numfashi kawai Julde ya sauke, ya riga da ya koyi shiru ya kyale su, tuntuni kamar suna Khalid da Nawfal na ganin hanjin juna wasu lokuttan, sun girma, Nawfal harda mata amman ba zasu daina fada kamar yara ba. Da Salim yakan bar su tunda can ma. Yau bashi da karfin surutun kwata-kwata shisa yaja motar suka tafi. Da suka ga an hau hanya shine suka cigaba

"Wallahi zaku sauka a hanya ku biyo mu a napep. Maganar da zan karayi akan ku sai kun sauka daga cikin motar nan"

Salim ya fada, saboda Daada na tare da su, kuma a tsakiya take zaune. Madina ce ta bangaren da su Nawfal din suke zaune, daga inda yake zai iya mika hannu ya kai musu duka, amman baya son su duka su gwada hali a gaban Daada. Kan shi har juyawa yake saboda surutun da sukeyi. Amman dan su san da gaske sauka zasuyi shisa ya rantse suka ji, yana kallon Nawfal

na ture hannun da Khalid yake kara dora mishi. Madina kanta murmushi takeyi, tana son ganin Khalid da Nawfal a tare, fadan su nishadi yake sakata, ko yanzun ma sun saukaka mata damuwar da take ciki.

Su dukan su basu kara nutsuwa ba sai da suka fita suka shiga cikin filin jirgin, suka tsaya inda zasuyi sallama da su Daada, lokacin tsoron da yake tare da Nawfal ya fito shimfide akan fuskar shi

"Kace zaka biyo mu Daddy"

Yayi maganar yana kallon Julde da ya daga mishi kai, Madina karasawa tayi ta rungume Daada tana jin wasu hawaye masu dumi na zubo mata

"Karki karya ni Madina"

Sake riketa tayi gam tana jin kamar ace in ta raba jikinta da na Daada zata taho da dumi da kamshin Daadar a tare da ita, iya wanda zata rike har sai ta dawo

"Allah ya dawo mun dake cikin aminci Daada... Ina son ki sosai.. Kin sani ai ko?"

Kai Daada ta daga tana kama Madina ta rabata da jikin ta

"Bajjo zai kira mun ke ta hoton nan yanda naga kunayi"

Hannu Madina ta sa tana goge fuskarta, sai da ta dan ja hanci sannan tayi murmushi

"Video call Daada"

Dan daga idanuwa Daadar tayi

"Oho ni ban san sunan shi ba"

Dariyar karfin hali Madina tayi, wasu hawayen na sake zubo mata, hawayen da Salim yake ji har kasan ran shi. Shisa ya saka hannuwan shi cikin aljihu saboda kaikayi suke mishi, kaikayin ya rikota ya hadata da jikin shi ya lallasheta ta sigar da yafi kwarewa

"Hamma sai mun dawo"

Nawfal da yake tsaye gefen Daada ya fadi yana sa Salim janye idanuwan shi daga kan Madina yana mayarwa kan shi

"Allah ya tsare...komai zaiyi dai-dai ka sani ko?"

Kai Nawfal din ya jinjina mishi, sallama suka kara yi gabaki daya, su suka fara juyawa suna barin Daada da Nawfal a tsaye. Madina ce ta juya tana daga ma Daada da taji zuciyar ta ta tsinke hannu, lokaci daya taji tsikar jikinta ta mike. Murmushi Madina tayiwa Nawfal da suka hada ido, sai dai zuciyar shi tayi nauyin da ya kasa mayar mata da martani har ta juya, yabi bayan ta da Kallo, da yanayin tafiyar ta.

Kallon ta Nawfal da Daada sukeyi
Kallon ta Nawfal yakeyi batare da ya san kaddarar da take bibiyar su ta kusan cika ba
Kallon ta yake batare da ya hango doguwar igiyar da take shirin kulle su a waje daya ba

Haka ya ga Salim yayi dabarar tsayawa Madina ta karasa suka jera tare, yanda ya juyar da kai na tabbatar ma da Nawfal din magana yayi ma Madina

Salim magana yayi mata kamar ba su da wata damuwa da ta wuce jiran dawowar Daada. Nawfal ya fara juyawa ya na ba Daada passport din su ta rike, ya dauki jakarta ya dora kan akwatin shi yanda zasuyi mishi saukin ja, sannan ya kama hannun ta yana fadin

"Muje Daada..."

Tana tunanin me likitoci zasu gani idan sun bude kirjin ta saboda zuciyarta na tare da su Madina, gabaki daya zuciyarta da ta kasa nutsuwa na tare da su. Haka tabi Nawfal suna tafiya, tana jin littafin da yake cikin kanta yana bubbudewa yana komawa shafin farko, takun duk da zatayi da nufin barin garin na zamar mata adon da yake janta don ta waiwayi in da komai ya fara....!

*****

Anan zan kawo karshen kashi na daya. Bayanin lokaci da kuma in da kashi na biyun zai zo na nan tafe ba da jimawa ba da yardar Allah.

Comments
Sakon fatan alkhairi
Addu'o'i
Ta wattpad
Whatsapp
Da masu kira har a waya

Banda kalaman da zanyi amfani da su wajen yi muku godiya. Allah ya saka muku da alkhairi. Nagode da duk kwarin gwiwar da kuke bani.

Allah ya sadamu da alkhairin shi.